WA'AZI A RUBUTATTUN WA{O{IN MATA NA {ARNI NA ASHIRIN

NA

MUHAMMAD, HAUWA BUGAJE

MA/ARTS/18254/2007-08

SASHEN HARSUNAN NIJERIYA DA AFRIKA

JAMI'AR AHMADU BELLO, ZARIYA

NIJERIYA

JANUARY 2011

WA'AZI A RUBUTATTUN WA{O{IN MATA NA {ARNI NA ASHIRIN

NA

MUHAMMAD, HAUWA BUGAJE

B.A. (Hons) Hausa

MA/ARTS/18254/2007-08

KUNDIN DA AKA GABATAR DOMIN CIKA SHARU[[AN SAMUN SHAIDAR DIGIRI NA BIYU A FANNIN HARSUNAN AFIRKA, SASHEN HARSUNAN NIJERIYA DA NA AFIRKA,TSANGAYAR FASAHA, JAMI'AR AHMADU BELLO, ZARIA.

JANUARY, 2011

Declaration

I declare that the work in the project entitled "Wa'azi A Rubutattun Wa}o}in Mata na

{arni na Ashirin" has been performed by me in the Department of Nigerian and African Languages, under the supervision of Dr. Magaji Tsoho Yakawada. The information derived from the literature has been duly acknowledged in the text and a list of references provided. No part of this project was previously presented for another degree or diploma at any university.

Muhammad, Hauwa Bugaje ---------- ------

Signature **Date**

Certification

This project entitled "WA'AZI A RUBUTATTUN WA{O{IN MATA NA {ARNI NA ASHIRIN" BY Muhammad, Hauwa Bugaje meets the regulation governing the award

of the degree of Master of Arts, African Languages, (Hausa) of Ahmadu Bello University, Zaria, and is approved for its contribution to knowledge and literary presentation.

---	---
Chairman, Supervisory Committee	Date
---	---
Member, Supervisory Committee	Date
---	---
Member, Supervisory Committee	Date
---	---
Head of Department	Date
---	---
Dean, Postgraduate School	Date

Acknowledgment

In the name of Allah, the Beneficent, the Merciful. May Allah's mercy and Blessings

be upon the Prophet of Islam, Muhammad (S.A.W). The success of this work is as a result of the support and contribution of many people.

I am particularly grateful to my humbled supervisors, Dr. Magaji T. Yakawada and Dr. Muhammad Lawal Amin who gave generously of their time to wide-ranging discussions on this work. I really appreciated their support and contributions. My sincere appreciation goes to my husband Dr. Y. U. Abubakar, my children and my family members (Bugaje family). May Allah continue to support and guide them to the right path.

I am also grateful to my teachers; Prof [alhatu Muhammad, Prof M. A. G. Raji, Prof Munnir Mamman, Dr. Bello S. Y. Al-hassan, Dr. M. A. Auwal, Dr Ilyasu Abbas, Mal. Adamu Ibrahim Malumfashi, Dr. Yahuza Imam, Dr. S. Khalid, Malam Abubakar Sarki, Malam Salisu Kargi, Malam Shu'aibu Hassan, Malam S A. Abdulmumin, Malam Sani Usman, Malam Rabi'u Tahir, Malama Rabi Garba and Malama Binta A. Tahir.

Thanks are also due to my Internal Examiner Dr. Isa I. Suleiman. I owe a debt of gratitude to him. Gratitude is also due to Dr. Atiku Ahmad Dumfawa and Malama Balbasatu Ibrahim all from Usmanu [anfodiyo University, Sokoto, and also to Prof. Abdul}adir [angambo, Prof Sa'idu Muhammad Gusau, and Dr. Ahmad Magaji all of Bayero University Kano, for offering useful suggestions and advice.

To my colleagues who helped me with useful advice and prayers, I pray that Allah will continue to guide and protect us. Finally, thanks are also due to the Poets; Amina Muhammadu Anda, Raihanatu Usman and Shema'u Abdullahi and every individual that supported this work in one way or the other.

Thanks a lot.

Muhammad Hauwa Bugaje

MA/ARTS/18254/07-08

ABUBUWAN DA KE CIKI

Shafin Tabbatarwa **i**

Shafin Amincewa **ii**

Shafin Sadaukarwa **iii**

Shafin Godiya **iv**

Tsakure **v**

BABI NA FARKO: GABATARWA

1.0 Shimfi]a 1

1.1 Manufa Bincike 3

1.2 Dalilin Bincike 4

1.3 Muhimmancin Bincike 5

1.4 Iyakacin Bincike 6

1.5 Hanyoyin Gudanar da Bincike 7

1.6 Mata a {asar Hausa 8

1.7 Gudummawar Mata a Fannin Rubutattun Wa}o}in Hausa 17

1.8 Ta}aitaccen Tarihin Mata Marubuta Wa}o}in Wa'azi na {arni na Ashirin 19

1.9 Na]ewa 30

BABI NA BIYU: WAIWAYE KAN AYYUKAN DA SUKA GABATA

2.0 Shimfi]a 31

2.1 Ma'anar Wa'azi 32

2.2 Tarihin Samuwar Wa}o}in Wa'azi a {asar Hausa 34

2.3 Ayyukan da Suka Gudana Kan Jigon Wa'azi 46

2.3.1 Kundaye 47

2.3.2 Litattafai 49

2.3.3 Mu}alu 50

2.4 Ayyukan da aka Gudanar Kan Rubutattun Wa}o}in Addini

2.4.1 Kundaye 54

2.4.2 Litattafai 59

2.4.3 Mu}alu 60

2.5 Ayyukan da aka Gudanar Kan Wa}o}in Tarbiyya da Fa]akar Al'umma 63

2.5.1 Kundaye 63

2.6 Ayyukan da aka Gudanar Kan Nazarin Adabin Mata (Rubutacciyar Wa}a) 65

2.6.1 Kundaye 65

2.6.2 Litattafai 67

2.6.3 Mu}alu 70

2.7 Na]ewa 73

BABI NA UKU: JIGOGIN WA{O{IN MATA NA WA'AZI A {ARNI NA ASHIRIN

3.0 Shimfi]a 74

3.1 Ma'anar jigo 74

3.1.1 Jigo a Rubutattun Wa}o}in Hausa 76

3.2 Jigogin Wa}o}in Mata na Wa'azi a {arni na Ashirin:

3.2.1 Ilimi 77

3.2.2 Ri}on Amana 87

3.2.3 Zamani 98

3.2.4 Lullu~i 106

3.2.5 Kishi 113

3.3 Na]ewa 119

BABI NA HU[U: TSARI DA SALON SARRAFA HARSHE A RUBUTATTUN WA{O{IN MATA NA WA'AZI A {ARNI NA ASHIRIN

4.0 Shimfi]a 120

4.1 Ma'anar Tsari a Wa}a 120

4.1.1 Tsarin Wa}o}in: 120

4.1.2 Mabu]i da Marfin Wa}a 123

4.1.3 Tsarin Layukan Wa}a 125

4.1.4 Yawan Baitoci a Wa}a 125

4.1.5 Amsa-Amo 127

4.1.6 Kari 130

4.2 Salon Sarrafa Harshe a Wa}o}in

4.2.1 Ma'anar Salo 135

4.2.2 Ire-iren Salo da ake Samu a Wa}a 136

4.2.3 Tubulan Ginin Salo 137

4.3 Na]ewa 147

BABI NA BIYAR: KAMMALAWA

5.0 Shimfi]a 149

5.1 Na]ewa 149

5.2 Shawarwari 153

5.3 Manazarta 158

Rataye 167

Abstract

Over the years, researchers have overlooked the contribution of women to the development of Hausa literature, most especially written poetry.

This research entitled: *Wa'azi a Rubutattun Wa}o}in Mata na {arni na Ashirin* "*Admonishing in 20th century Hausa women poetry,* compiled and surveyed the poems of some renowned writers. The research explores the themes and style of the poems. Such themes include; *ilimi* 'education' *gaskiya* 'trustworthiness' *kishi* 'rivalry between wives of the same husband' and some other related themes. These are considered as the major themes of poems composed by women poets of the 20thC.

Finally, an anthology of poems by renowned women poets is made to serve as a data-bank for the use of researchers.

Tsakure

Nazari kan ayyukan mata a fagen adabi fanni ne da aka bari a baya a fagen bincike. Wannan aiki mai suna: “Wa’azi a Rubutattun Wa}o}in Mata na {arni na Ashirin” bincike ne da aka gudanar domin fito da gudummawar mata a fannin bun}asar adabin Hausa. Aikin ya tattaro wasu daga cikin rubutattun wa}o}in mata na }arni na ashirin musamman masu jigon wa’azi, kuma an nazarci jigo da tsari da salon da ke cikin wa]annan wa}o}i. Har wa yau, an duba tare da sharhi kan batutuwan da marubutan suka fito da su a fannin wa’azinsu, kamar muhimmancin ilimi da muhimmancin ri}on amana da lullu~i da sauransu . Domin haka, a iya cewa wannan aiki shi ne na farko da ya tattara rubutattun wa}o}i masu jigon wa’azi da mata suka rubuta a }arni na ashirin.

BABI NA FARKO: Gabatarwa

1.0 Shimfi]a

Wa}a na]aya daga cikin manyan sassa uku na adabi, walau na baka ko rubutacce. Wa}a na da matu}ar muhimmanci wajen isar da sa}o tun asalin samuwarta har zuwa yau. Rubutattun wa}o}i, wa}o}i ne da kan zo a rubuce da tsari na musamman wanda ya samo asali daga tasirin rubutattun wa}o}i na Larabci (ita dai rubutacciyar wa}a tana zuwa ne da tsarin baiti da kuma kari irin na rubutattun wa}o}in Larabci). Wannan tasirin ne ya bambanta tsakanin rubutacciyar wa}a da wa}ar baka.

Masana sun yi ittifa}in cewa rubutattun wa}o}i a }asar Hausa sun samo asali ne daga Musulunci, domin sakamakon zuwansa ne aka sami manyan malamai suka fara rubuta wa}o}in da suka shafi addini. Mafi yawa daga wa}o}in malaman nan na]auke da jigon wa'azi. Irin wa]annan malamai sun ha]a da Ibn Al- sabbagh (wanda aka fi sani da Wali]an Marina), da Malam Abduljalil (wanda aka fi sani da Wali]an Masani) da Muhammad Al-Barnawi (mutumin Borno), da Muhammad Al-wali da dai sauransu. (Hiskett, 1975; Yahya, I.Y, 1988:p38.)

An ci gaba da samun rubutattun wa}o}in wa'azi a }arni na goma sha takwas inda aka samu marubuta irin su Muhammad al-Kashnawi, da Muhammadu na Birnin Gwari, da kuma Malam Shi'itu]an Abdurra'uf.

Tarihin rubutattun wa}o}i ba zai kammala ba har sai an ta~o gagarumin aikin da Shehu Usman [anfodiyo (Mujaddadi) da iyalansa da kuma al'majiransa wa]anda suka

samar da]imbin wa}o}in da suka shafi madahu da wa'azi da zuhudu da sauransu.

Za a iya cewa a wannan lokaci na masu jihadi ne }o}arin mata wajen rubuta wa}o}i ya fara fitowa fili. Hakan ya bayyana ne idan aka yi la'akari da aikin da Nana Asma'u 'yar Shehu ta yi ta fuskar rubutawa da fassarawa da kuma yi wa wasu wa}o}in Shehu tahamisi. Daga wannan lokaci ne aka sami mata suka ci gaba da rubuta wa}o}i kan jigogi daban-daban, wanda jigon addini shi ne kan gaba.

{arni na ashirin (1900- 2000) lokaci ne da aka sami sauyi a }asar Hausa, sakamakon mulkin mallaka da Turawan Ingila suka yi na tsawon shekaru gabanin su ha]e yankin arewaci (}asar Hausa) da yankin kudanci (a 1914) su tayar da abin da a yau ake kira Nijeriya . Daga baya an sami 'yancin kai (a 1960) a }ar}ashin }asa]aya wato Nijeriya, wadda ta gwamutsa al'ummomi daban daban masu }abilu da addinai daban daban. Wannan ne ya haifar da sauyi a tsarin rayuwa ta yau da kullum a }asar Hausa (kamar shigowar boko da sauransu).

Amma duk da wannan sauyi da aka samu an ci gaba da samun rubutattun wa}o}in wa'azi a wannan }arni, kuma mata sun shiga an dama da su wajen rubuta irin wa]annan wa}o}i.

Kodayake masana irin su Hiskett (1975) da Abdul}adir (1979) na da ra'ayin cewa wa}o}in }arni na sha tara wa}o}i ne na addini zalla, yayin da suka bayyana wa}o}in }arni na ashirin a matsayin wa}o}i da suka shafi harkokin duniya, kamar

yadda Malumfashi (1984) da Aminu (2000) suka bayyana. Wa]annan masana sun }alubalanci ra'ayin su Ibrahim, domin sun bayyana cewa ai ba a raba hanta da jini, wato ba wani bambanci tsakanin wa}o}in addini na }arni na sha tara da na ashirin. Domin kamar yadda aka sami wa}o}in addini da dama a }arni na sha tara, haka ma abin yake a }arni na ashirin. Kusan ma mafi yawa daga rubutattun wa}o}in }arni na ashirin na]auke ne da jigon addini.

1.1 Manufar Bincike

Manufar wannan bincike ita ce:

- {ara tabbatar da da'awar masana da ke cewa an ci gaba da samun rubutattun wa}o}in addini (har da wa'azi) a }arni na ashirin.
- Bin diddi}in hasashen da ake yi cewa shin ko mata sun ci gaba da rubuta wa}o}i musamman na wa'azi duk kuwa da koma baya da suka samu a fannin ilimi na addini da na boko?
- Idan har aikin ya cim ma manufar wannan bincike na tabbatar da hasashe cewa mata sun ci gaba da shiga a dama da su fagen rubuta wa}o}in wa'azi, aikin na da nufin binciko irin muhimman darussa ko sa}onnin da wa}o}in nasu ke isarwa. Wato za a duba jigon wa'azi a wa}o}i nasu tare da binciko abubuwan da mata suka mayar da hankali a kansa wajen wa'azantar da

al'umma.

- Har wa yau, za a yi nazari a ga wace irin hikima da fasaha ke cikin wa}o}in nasu?

1.2 Dalilin Bincike

Duk da cewa an yi ayyuka da dama game da gudummawar mata wajen samuwa da ha~akar rubutattun wa}o}i, amma har wa yau akwai gi~i tsakanin ayyukan da aka gudanar a kan ayyukan mata na }arni na sha tara da }arni na ashirin. Hatta wa]anda suka nazarci ayyukan mata na }arni na ashiri irin su Balbasatu (2008) sun ambaci sunayen matan ne da ayyukansu kawai ba tare da sun nazarci ayyukan nasu ba. Domin haka ne wannan aiki ya nazarci jigon wa'azi a rubutattun wa}o}in mata na }arni na ashirin.

- Dalilin da ya sa aka za~i gudanar da binciken a kan wa}o}in wa'azi na }arni na ashirin shi ne domin an gudanar da ayyuka da dama a kan wa}o}in addini (har da wa'azi) na }arni na sha tara.
- Haka kuma, an za~i gudanar da binciken ne a kan wa}o}in wa'azi na mata kawai domin an bincika an ga su ne ake da }arancin bincike a kansu. Kuma mutane ba su sansu sosai ba, in ma an san da zamansu, to a iya cewa }ila ba a cika kula da su ba kamar na maza. Saboda kamar yadda bitar ayyukan da suka gabata ta nuna, akwai aikace-aikace da dama da aka yi kan nazarin rubutattun

wa}o}in addini na maza.

- Har wa yau, wani dalilin da ya haifar da wannan bincike kan jigon wa'azi a wa}o}in mata na }arni na ashirin shi ne domin taskace wa]annan wa}o}i da nazarin jigo da tsari da salon da ke cikin wa}o}in nasu.

Yin aikin zai sa a sami ire – iren wa]annan wa}o}i da mata suka yi a wuri]aya kuma zai ba da haske kan irin salon da marubutan ke amfani da shi.

1.3 Muhimmancin Bincike

Wa}a muhimmiyar hanya ce ta isar da sa}o ga jama'a, kuma hanya ce da za a iya fahimtar tunani da fasahar mutum. Domin haka ne aka za~i gudanar da bincike a fannin rubutattun wa}o}in mata na wa'azi.

- Wannan bincike na da muhimmanci domin ya taskace wani fanni na adabi (rubutattun wa}o}i) tare da nazartarsu.
- Haka kuma ana sa ran binciken ya zamo mai alfanu ga marubuta tarihi da manazarta ayyukan mata, saboda za a taskace ayyukan adabi (rubutattun wa}o}i) da mata suka yi da kuma tarihinsu.
- Har wa yau, ana fata warwarar jigon da aka yi a aikin (sa}onnin marubuta wa}o}in wa'azi) ya zamo abin da malaman addini za su iya waiwaya a matsayin hujja domin ci gaba da wa'azantar da al'umma ta hanyoyi da dama.
- A }arshe, ana fata wannan bincike ya yi alfanu ga]alibai manazarta adabi

domin zaburar da su, wajen waiwayen ayyukan adabi na mata da gudanar da bincike a kansu. Wannan zai sa a cike gi~in da ke akwai tsakanin bincike-binciken da aka gudanar a kan ayyukan adabi na maza da na mata.

1.4 Iyakacin Bincike ko Farfajiyar Bincike

Kamar yadda ya gabata a baya, wannan aiki mai suna ‘wa’azi a rubutattun wa}o}in mata na }arni na ashirin’ zai shafi rubutattun wa}o}i ne, ba na baka ko na fiyano ba.

- Haka kuma, aikin ya tsaya ga rubutattun wa}o}in wa’azi ne kawai, sabanin wasu wa}o}i da suka shafi al’amurran duniya.
- Har wa yau, aikin ya toge ne a rubutattun wa}o}in wa’azi da mata suka rubuta ban da wa]anda maza suka rubuta.
- Kuma an za~i wa}o}in }arni na ashirin ne (ba na sha tara ba ko na ashirin da]aya), duk kuwa da cewa wasu daga cikin matan da aka nazarci ayyukan nasu sun rayu har zuwa wannan }arni da muke ciki (}arni na ashirin da]aya).

An yi wannan ta}aitawar ne domin fagen rubutattun wa}o}i fage ne mai fa]in gaske wanda in dai ana son bincike ya yi ma’ana dole ne a]auki sashe]aya daga cikin sassa. Wannan dalili ne ya sa aka tsaya a kan rubutattun wa}o}in mata na wa’azi na }arni na ashirin kasancewar wa}o}in wa’azi da mata suka rubuta na da matu}ar yawa wanda mawuyacin abu ne a iya nazarinsu baki]aya a bincike irin wannan.

1.5 Hanyoyin Gudanar da Bincike

Wannan aiki ya yi amfani da muhimman hanyoyin gudanar da bincike da aka amince da su a tsarin gudanar da bincike irin wannan.

- An yi amfani da kundayen bincike na neman digiri tun daga na]aya har zuwa na uku wa]anda ke da ala}a ta kusa da ta nesa da wannan bincike.
- Haka kuma, an yi amfani da litattafan da aka wallafa da mujallu da jaridu da }asidun da masana daban-daban suka rubuta musamman wa]anda ke da nasaba da wannan aiki.
- Binciken ya yi amfani da hanyar tattaunawa da masana da malaman addini musamman kan abin da ya shafi wa'azi.
- Har wa yau, aikin ya ziyarci kafafen ya]a labarai domin samun wa}o}i da }arin bayani game da marubuta wa}o}in. Daga cikin kafafen ya]a labaran da aka ziyarta akwai gidan Rediyon Tarayya na Kaduna, da gidan Rediyon jihar Kaduna da gidan Rediyon jihar Katsina da gidan Rediyon Nagarta da sauran kafafen ya]a labarai.
- Haka kuma, an yi amfani da taskar ODU ta sashen Harsunan Nijeriya da Afrika ABU Zaria.
- An kuma kai ziyarar neman bayanai wurin matan da aka za~i wa}o}insu da kuma samun wa}o}in nasu daga taskokinsu.
- A }arshe, an nemi }arin bayani daga wurin manyan malamai masana wannan

fage na wa}a.

1.7 Mata a {asar Hausa

Da yake wannan bincike ya ta'alla}a ne a kan mata da nazarin adabinsu, zai yi kyau idan aka yi kyakkyawar shimfi]a ta musamman kan nazarin mata a }asar Hausa. Abin nufi a nan shi ne komawa baya da waiwayar yadda rayuwar mata ta kasance a wannan al'umma ta Hausawa, tun da daga lokacin maguzanci da bayan jihadi da kuma bayan zuwan Turawa. Wannan zai sa a fahimci halin da mata suka shiga da gwagwarmayarsu a fagen neman ilimi da kuma irin gudummawar da suka bayar wajen bun}asa adabi da kyautata tarbiyyar al'umma. Wani hanzari ba gudu ba, wannan bayani zai gudana ne a ta}aice.

Kafin Jihadin (Zamanin Maguzanci)

Hausawa kamar sauran al'ummomin duniya mutane ne da suka]auki mata a matsayin halitta mai raunin hankali da tunani. A al'adar Hausawa, mata ba su da matsayin da maza ke da shi, wato akan fifita]a namiji a kan 'ya mace, sai dai duk da haka ba a sami tarihin kisan gilla ga mata a }asar Hausa ba kamar yadda aka ri}a yi wa mata a]aular Larabawa da Girkawa da Indiyawa da Sinawa da sauransu ba.

Matsayin da Bahaushe ya ba mace shi ne na kula da aikace-aikacen gida kamar tsabtace gida da dafa abinci da kula da yara, domin haka ma Bahaushe ke wa mata

kirari da: “mata iyayen gida, in ba ku ba gida…” Shi kuwa namiji, an san shi da fita waje, ya yi aikin }arfi domin samar wa iyali abin da za su ci. Irin ayyukan da maza kan yi sun ha]a da noma, gini, }ira, dukanci, wanzanci, fatauci da sauran sana’oin gargajiya na Hausawa. A gargajiyar Bahaushe, mata ba sa fita ya}i saboda raunin da ake danganta su da shi, kamar yadda kirarin matan ya nuna “mata na Inna dangin yun~u….” Bahaushe ya]auki mace a matsayin mai }arancin hankali wadda ba ta isa a yi shawara da ita ba ko da kuwa a kan abin da ya shafe ta ne, (kamar wurin aure). Haka kuma, Bahaushe ba ya ~ata lokacinsa wajen koya wa ‘ya’yansa mata sana’o’insa da sauran dabarun zaman duniya da akan koya wa ‘ya’ya maza, domin a tunanin Bahaushe ‘ya mace ‘yar gidan wani ce, komin da]ewa gidan za ta bari ta koma gidan mijinta da rayuwa (sai dai akan koya mata sana’o’i da suka ji~anci mata, kamar ka]i, da sauransu), shi kuwa]a namiji shi ake sa ran zai zama magajin gida, wato zai gaji sana’ar mahaifinsa da sauran al’amurran da mahaifinsa ya sa gaba.

Haka kuma, mata ba sa shugabanci a gargajiyar Bahaushe, sai dai an sami ‘yan tsirarun mata da suka yi shugabanci a }asar Hausa kamar a masarautar Zazzau inda aka ce sarauniya Amina ta yi shugabanci, sai kuma masarautar Daura inda a tarihin masarautar aka ce mata ke shugabanci har sai bayan zuwan Bayajidda da ya auri sarauniya Daurama ya kuma kar~i ragamar shugabanci. Wa]annan su ne ‘yan tsirarrun matan da aka samu sun yi shugabanci a tarihin }asar Hausa baki]ayanta, sai dai akwai

mu}amai da akan ba mata a kowace masarauta ta }asar Hausa, su kuwa wa]annan mu}aman sun fi shafar matsalolin mata ne, kamar mu}amin Inna a Gobir wadda akan ba }anwar sarki kuma ita ke shirya abin da ya shafi girka ta bori domin samar wa mata da yara lafiya daga matsalolin da ke damun su. (Mack, 2000: shafi 36). Sauran mu}aman mata sun ha]a da Jakadiya da magajiyar gari da sauransu.

Haka kuma, mata sun kasance, kullun su ne koma baya a cikin al'umma. Ko bayan da Bahaushe ya kar~i Musulunci, matsayin mata bai sauya ba, domin maimakon malamai su yi amfani da ilminsu su koyar da matansu da 'ya'yansu mata ibada (kamar yadda Manzo (S.A.W) ya koyar kuma sahabansa suka yi koyi) a }asar Hausa sai aka sami akasi, domin za ka ga malami ya kai ya kawo a fagen ilmi ga shi da al'majirai amma matansa ba su iya ko fatiha ba, sai dai ya fita waje ya koyar, ya bar matansa zaune kamar dabbobi. Kamar yadda Shehu Usmanu ya bayyana a cikin littafinsa mai suna Nur-al-albab cewa:

> suna tafiyar da matansu da 'ya'yansu mata na gida kamar wasu kayan amfani, wa]anda in aka gama cin moriyarsu sai a watsar da su a shara. Haba! Ta yaya za su bar matansu da 'ya'yansu cikin duhun jahilci? Amma suna koyar da almajiransu a waje don neman suna.
>
> (Fafunwa,1974:49-50).

Wannan mummunan al'amari ba }aramar illa ya yi wa mata a }asar Hausa ba, domin yanzu haka za ka sami mata dattawa da suka dage neman ilimi domin gyara ibadarsu, idan suka tuna da zaman jahilcin da suka yi a baya har kuka suke.

Bayan Zuwan Shehu Mujaddadi

Mata sun fara samun damar neman ilimin addini a }asar Hausa a }arni na 19, lokacin da Mujaddadi Shehu Usmanu da iyalansa da al'majiransa suka tashi hai}an domin ganin sun jaddada addini a }asar Hausa. A wannan lokaci ne Shehu Usmanu ya tashi tsaye wajen nuna wa jama'a muhimmancin ilmin mata inda ya kafa misali da kansa ta hanyar ilmantar da matansa da 'ya'yansa, kuma ya sa su suka zama malamai ga sauran mata domin ganin an magance matsalar jahilcin da ke damun al'umma. Shehu ya jaddada bu}atar da ke akwai ta ilmantar da mata kan sauran al'amurran da suka shafi rayuwa kamar harkokin kiwon lafiya da ciniki da sauransu.

Wannan }o}ari na Shehu Usmanu ya sami gagarumar nasara domin ta wannan hanyar ce aka fara jin]uriyar mata a fagen ilimi a }asar Hausa, domin Nana Asma'u da 'yan uwanta sun taimaka wajen horar da malamai mata wa]anda suka ri}a shiga gida- gida suna ilmantar da mata a }ar}ashin }ungiyar nan ta'yan Taru' wadda Nana Asma'un ta shugabanta. A sanadiyyar haka ne mata suka san matsayin da Allah ya yi musu, kuma suka tashi tsaye wajen koyon yadda za su bauta wa Allah domin samun babban rabo a ranar }iyama.

Matsayin mata a }asar Hausa ya ci gaba da bun}asa a fagen ilimi da kasuwanci da sauran fannoni na rayuwa bayan jihadin daular Usmaniyya har zuwa }arshen }arni na 19, lokacin da Turawan mulkin mallaka suka shigo }asar Hausa.

Bayan Zuwan Turawan Mulkin Mallaka {asar Hausa

Turawan mulkin mallaka sun mamaye }asar Hausa tare da kar~e ragamar shugabancinta a zamanin Sarkin Musulmi (Sultan) Attahirun Amadu (wanda ya gwabza ya}i da Turawa har Allah ya yi masa rasuwa a wurin ya}in). Kafin wannan lokaci }asar Hausa na tafiyar da mulkinta ne kan tsari irin na addinin Musulunci wanda Shehu Usmanu da mabiyansa suka kafa daga ranar 21/6/1804 zuwa ranar 1/1/1900 (ranar da aka sanar cewa }asar Hausa ta koma }ar}ashin mulkin Turawan Ingila (Balogun, 1979:39). Kar~e mulkin Turawan ke da wuya sai suka sauke wasu daga cikin Sarakunan da suka tarar suka na]a wasu wa]anda suke ganin za su iya aiki da su ta hanyar ba su umurni a kan mulkin }asa. Ba a nan ‘yan mulkin mallakar suka tsaya ba, sai da suka tabbatar sun rage }arfin da }asar Hausa ke da shi a fagen ilimi da harkar tattalin arziki. Sun kuwa yi haka ne ta hanyar fito da makarantun boko tare da ba su takardar sheda wadda daga }arshe wanda yake da irin wannan takarda ne ake]auka aiki a gwamnati, yayin da wa]anda suka kammala makarantun allo (addini) za a bar su ba su da madafa. (Fafunwa, 1974:60).

Babban dalilin da ya sa Hausawa suka }i amincewa da makarantun boko da sauri shi ne saboda tasirin wa]anda suka kafa makarantun wato Turawa, domin turawan da suka fara shigowa }asar Hausa a wancan lokaci Turawa ne na Mishan wa]anda suka shigo }asar da sunan ‘yan yawon bu]e ido amma manufarsu ita ce ya]a addinin Kirista (Bahaushe kan masu kirari da “Mishan ~ad da Musulmi”). Su kuwa al’ummar }asar Hausa sun da]e da kar~ar addinin da suka yi imani ba wani addini bayansa(Musulunci) kusan tsawon }arni biyar kafin Turawa su gane hanyar }asar Hausa. Wannan dalili ne ya sa Hausawa ke]ari-]ari da ilimin boko da kuma duk wani abin da Nasara (Bature) ya zo da shi domin gudun fita daga Musulunci.

Wannan matsala ta sauyin rayuwa da aka shiga sakamakon mulkin mallaka da }asar Hausa ta samu kanta a ciki ya }ara jefa mata cikin halin }a}a-nika yi tare da komawa ‘yar gidan jiya da matan suka yi, wato “ba su ga tsuntsu, ba su ga tarko.”

Matsalar farko da mata suka fuskanta ita ce ta ta~ar~arewar ilimin addini, wato damar da suke da ita ta neman ilmin addinin ta ragu saboda hankalin al’umma ya]agu da sabon yanayin da ake ciki. A fagen ilmin bokon kuma ana tsoron a ba su damar shiga su nemi ilmin saboda a wancan lokaci bokon abin }yama ne, ko]a namiji ma ana ~oye shi domin kada hukuma ta sa shi makaranta, bare mace wadda ake tsaro da taka-tsan-tsan da rayuwarta. Wannan dalili ne ya sa aka bar mata a baya a kowane ~angare na rayuwa a }asar Hausa. Wani dalilin da ya taimaka wajen tauye matsayin

mata a }asar Hausa shi ne rashin kulawar su kansu Turawan mulkin mallakan a kan ilimin mata, domin ko da suka sa doka ta sa yara makaranta, ba su kafa makarantar mata ba sai a shekara ta 1930 (a Kano) shekaru 21 bayan bu]e makarantar maza. (Mack, 1988: 65).

Duk da wa]annan dalilai, wasu daga cikin mata sun samu damar samun ilimin addini da na boko tun a farkon }arni na ashirin. Wasu daga cikin matan da suka sami wannan dama sun ha]a da Hajiya Hauwa Gwaram da Hasana Ahmed sufi da sauransu, sai dai duk da haka a wannan lokaci mutane na tsananin }yamar sa 'ya'yansu makaranta kamar yadda Hauwa Gwaram ta shaida wa Beverly Mack a firar da ta yi da ita, inda take cewa:

> Sa'adda aka sa ni makaranta, ba a cika sa yara mata makaranta ba, wa]anda ke zuwa makaranta a wannan lokaci sai 'ya'yan Sarakuna da 'ya'yan masu ku]i da 'ya'yan Al}alai….(wanda ya zama dole a sa su) Kamar mu 'ya'yan mai garin Gwaram, an sa mu makarantar ne don dole. (A wancan lokaci) kin san rumbun adana hatsi wanda akan adana gero a ciki? To a ciki ake saka yara, Uwaye mata kan ~oye yaransu a cikin manyan tukwane su rufe su, wato wai suna ~oye su daga masu kama yara don sa wa makaranta…. (Mack, 2004:19).

A lokacin da, Hausawa kan]auki duk wanda ya shiga makarantar boko kamar ya kafurta, domin haka ne ma yaran gari kan yi wa yara masu zuwa makaranta wa}a suna cewa:

'Yan makarantar bokoko
Ba karatu ba sallah,
Sai yawan zagin malam.

Sannu a hankali da tafiya ta yi tafiya sai iyaye suka fara fahimtar muhimmancin ilmin

boko, domin haka suka ri}a kai ‘ya’yansu makaranta da kansu. Wannan ya taimaka wajen bun}asar ilimin mata a }asar Hausa.

Bayan haka, daga baya gwamnati ta mayar da hankalinta wajen bun}asa ilmin mata a }asar Hausa (Arewacin Nijeriya a yau) inda ta ri}a fito da shirye-shirye domin tallafa wa mata, kamar bu]e makarantun ya}i da jahilci da bayar da tallafi na musamman ga]alibai mata da ke da sha’awar karatu da sauran hanyoyin da za su }arfafa wa iyaye gwiwa don ganin ilimin mata ya bun}asa. Ta fuskar ilimin addini kuwa, a iya cewa an sami ci gaba musamman a wannan }arni da muke ciki (na 21), domin malamai na }ungiyoyin addinin Musulunci daban- daban sun dage wajen samar da makarantun islamiyya inda ake koyar da mata da yara darussa da suka shafi addini har ma da boko da kuma sana’oi daban daban domin a sami sauyi mai ma’ana a rayuwar al’umma.

Yanzu kam, a iya cewa tubarkalla, domin mata sun fara zama daga cikin sahun gaba a cikin al’umma a }asar nan, domin yanzu haka ba wani fage na ilimi da ba matan Hausawa a ciki, haka abin yake ta fuskar kasuwanci da sha’anin mulki da sauran fannoni na rayuwa, kamar yadda Binta Zabaya ta bayyana a wa}arta mai taken “wa}ar matan Nijeriya” inda take cewa:

Matan Nijeriya!
Matan Nijeriya!
Allah yai maku, ilimi duka kun iya

Duk aikin duniya kowane aka ba ku zaku yi
Matan Nijeriya!
Malaman makaranta kun iya…

Sai dai wani abin ban takaici da wasu daga cikin matan da suka sami damar yin ilimi a }asar Hausa a yau suka sa kansu a ciki shi ne na kwasar al'adun Turawa na yin gogayya tsakanin maza da mata maimakon su yi koyi da irin rayuwar }warai da matan da suka gabata suka yi ta hanyar amfani da iliminsu wajen fafutukar gyaran halin al'umma da samar da al'umma ta }warai wadda za a ri}a alfahari da ita.

Wannan ba }aramin abin ban haushi ne ba yadda a yau, mata ke }o}arin mayar da kansu matsayin da suka kasance a zamanin duhun kai ta hanyar watsi da nauyin da Allah (S.W) ya]ora masu na reno da tarbiyyar al'umma, sun bar wannan gagarumin aiki na kula da gidajensu a hannun wasu matan wa]anda wani lokaci ba ma Musulmai ba ne, sun koma sai sharholiya da neman abin duniya, tare da amsa kiran da Yahudawa ke masu na cewa su fito su yi kafa]a da kafa]a da maza, domin a cewarsu wai "what a man can do, a woman can do better" (duk abin da namiji zai iya yi, mace ma za ta yi mafiyinsa). Wannan kururuwar iblis ce kawai, domin kowa ya sani, su kasansu Yahudawan sun sani halittar namiji da mace ba]aya ba ce, akwai abubuwan da mace za ta iya yi, namiji ba zai iya yinsu ba, haka kuma akwai abubuwan da namiji za ya iya yi amma ba su dace da halittar mace ba (kamar shugabanci da harkar tsaro),

domin haka, komai ke da iyakarsa, kuma tsayawa a iyakar shi ne zama lafiyar kowace al'umma. Da fatan matan Hausawa za su ri}a abin nan da Bahaushe kan ce "waiwaye adon tafiya" wato su ri}a waiwayawa baya suna nazarin yadda matan }warai suka tafiyar da iliminsu wajen gina al'umma ta }warai.

1.8 Gudummawar Mata A Fannin Rubutattun Wa}o}in Hausa

Mata a }asar Hausa sun da]e suna ba da gudummawarsu ta ~angaren ya]awa da bun}asa adabi, domin tun ainahin gargajiyar Bahaushe (kafin zuwan musulunci da boko) mata sun taimaka wajen bun}asar adabin baka musamman ta ~angaren tatsuniyoyi da karin magana da wa}o}i da sauran sassa na adabin baka. Haka ma abin yake a ~angaren rubutaccen adabi, domin sun yi rubuce- rubuce a fannin zube da wasan kwaikwayo.

A fannin rubutattun wa}o}i kuwa, mata sun rubuta wa}o}i da dama sai dai ayyukan nasu ko kusa ba su kama }afar na maza ba. Hakan ya faru ne saboda koma bayan da suka samu ta fuskar neman ilimi. Matan da suka sami damar samun ilimin a wancan lokaci, sun dage domin nuna halin }warai kuma abin koyi ga sauran mata, wasu daga cikin irin wa]annan mata sun ha]a da Nana Asma'u wadda malama ce kuma ta samar da wa}o}in da suka shafi addini da dama a lokacin rayuwarta. Wasu daga cikin wa}o}inta sun ha]a da; wa}ar "Sharu]]an {iyama" da wa}ar "Dawa'in tsorace – tsoracen Ubangiji" da wa}ar "Manyan zunubai masu kafirta mutum" da

wa}ar “Wa’azu” da wa}ar “Garga]i ga masu shan azumi” da sauransu. (Boyd & Mack, 1999) da (Yahya, 1989) da (Sa’id 1978). Ga ka]an daga cikin shawarar da Nana Asma’u ta ba jama’a don yin guzurin zuwa lahira a wa}arta “Wa’azu”:

Bari fa bidi’a ka kamma hanya ta Sunna,
Ita ka isak ka har ga Darul Salami.

Don fa tuba ka ba da tsarki ga bawa,
Daga zanubi shi tcira ga shiga Jahimi.

Tsari fa tsarkin wulu’u, wankan janaba,
Inda shara]i fa babu ciwo ga jisni,

Inda ciwo ka taimama don Ta’ala
Jalla ya sau}a}a ma bawa alimi.

Mai fa aikin da ya fi so Mai hukumci,
Duk ga aikinsa mai Irada Hakimi,

Duk ku zam ko bi]a ga Allahu Sarki,
Gafara ko mu sami yarda azimi.

Har wa yau, akwai matan da ke bin Nana a ~angaren rubutattun wa}o}i wa]anda suka ha]a da Maryam Fodiyo wadda ta yi wa}ar “Sharu]]an limanci” da Aisha Abdullahi Fodio da ta yi wa}ar “Rafkanuwa a cikin Sallah” da kuma sauran ‘yan uwansu da suka ha]a da Khadija Fodiyo wadda ta rubuta wa}o}i da dama daga cikinsu akwai wa}ar “Ta’aziyya” da wa}ar “Garga]i da wa}ar Mahdi” (Usman 1982, cikin Balbasa 2008:96). Sauran mata marubuta wa}o}i a }arni na19 sun ha]a da

Husaina Dabo (‘yar sarkin Kano Ibrahim Dabo) da Rabi’atu Bello da Khadija Madawakin tsangaya da sauransu. (Maimuna, (2008) da Balbasatu, (2008).

A }arni na ashirin kuwa an sami mata marubuta wa}o}i wa]anda suka ha]a da Hasana Ahmed Sufi da Hauwa Gwaram da Ru}ayyatu Sabuwa Adakawa da Raihanatu Usman da Ige Sakkwato da Laraba Bauchi da Amina Anda Funtuwa da Shema’u Abdullahi da sauransu.

1.9 Ta}aitaccen Tarihin Mata Marubuta Wa}o}in Wa’azi na {arni na Ashirin.

Nazarin tarihin mawa}i yana]aya daga cikin muhimman matakan nazarin wa}a domin yana taimakawa wajen fahimtar jigo da salon mawa}i tare da shekarun wa}a da sauran muhimman abubuwan da mai nazari zai so ya gano daga cikin wa}a. Wannan dalili ne ya sa za a kawo ta}aitaccen tarihin mata marubuta wa}o}in wa’azi na }arni daga ashirin zuwa yau, daga nan kuma za a za~i ayyukan mata biyu daga kowace shiyya ta }asar Hausa domin yin nazari.

Hassana Ahmed Sufi (1929-2011)

Mace ta farko da wannan binciken ya fara cin karo da ayyukanta ita ce Hassana

Ahmad Sufi da ke Kano. An haifi Hassana Ahmed Sufi a shekara ta 1929 a cikin garin Bichi ta jihar Kano. Hassana ta fara neman iliminta a hannun yayarta Zainabu, wadda ta ri}e ta, amma daga baya ta koma hannun mahaifiyarta Maimunatu da zama inda ta ci gaba da neman iliminta. Hassana ta fara koyarwa tana da shekara 16 a duniya a gidan mijinta na fari wanda ta aura tun tana da shekara sha hu]u. Bayan mutuwar aurenta na fari, ta auri malam Ashiru a shekarar 1955 daga baya kuma ta fita, sai ta auri wani Balarabe, har ta sami haihuwar]a]aya mai suna Suleiman (amma ya rasu daga baya). A cikin aure-auren da Hassana ta yi ne ta zurfafa iliminta musamman a fannin karatun {ur'ani da sauran litattafai na ilimi kamar Risala, domin ta yi gamon katar ta fa]a hannun mazaje masu ilimi. Har wa yau, ta yi ta koyarwa a dukkan gidajen aurenta.

Ilimin Hassana Ahmed Sufi bai tsaya ga ilimin addini ba, har ma ta sami damar shiga makarantar koyon harshen Larabci ta Kano (School of Arabic Studies), haka kuma, ta sami damar yin diploma a fannin Hausa da Larabci (1981-1983). Wannan ya ba ta damar yin aikin koyarwa a makarantun gwamnati kamar makarantar 'yan mata ta Shekara a shekarar (1968) da makarantar gidan Galadima da Makarantar Koyon Malanta ta Mata (W.T.C) da sauransu.

Ta ~angaren rubuce-rubuce kuwa, Hajiya Hassana ta yi rubuce- rubuce da dama, ta rubuta littatafai na addini cikin harshen Hausa da Larabci, daga cikinsu akwai littafin

koyon aikin Hajji da littafin *Rukunnan Musulunci* Juz,i na]aya zuwa na uku, da littafin *Tarihin Annabawa* da littafin koyon Larabci da sauransu. Ta fuskar adabi kuwa, Hajiya Hassana ta bayar da gudummawarta a fannin rubutattun wa}o}in Hausa, inda ta rubuta wa}o}i]ai-]ai har ashirin da biyar, daga cikinsu akwai wa}ar "Ilimi" da wa}ar "Harshen Hausa" da wa}o}in Ta'aziyya da sauransu. (Babba, 1980).

Wannan baiwar Allah ta kasance ta saudakar da rayuwarta wajen ilmantar da al'umma ta hanyar koyar da mata da yara abin da Allah ya sanar da ita, tare da yin rubuce – rubucen da za su taimaka wa al'umma wajen fahimtar addinin Musulunci da wayar da kan al'umma kana bin day a shafi al'amurran rayuwa ta yau da kullum. Allah ya yi wa Hassana Ahmed Sufi rasuwa a watan fabrairu na 2011. Allah ya gafarta ma ta, ya sa aikinta na alheri ya bi ta.

Hajiya 'Yar Shehu

Daga Hajiya Hassana Sufi, sai aikin ya dira kan Hajiya 'Yar Shehu. An haifi Hajiya 'Yar Shehu a [ambatta ta cikin jihar Kano, kamar Hassana Sufi, Hajiya 'Yar Shehu ta taso cikin tarbiyya da kulawa ta musamman wadda 'ya'yan malaman }warai kan samu daga iyayensu domin mahaifinta ne ya kasance malaminta na farko a duniya wanda ya fara koyar da ita karatun {ur'ani mai girma. Mahaifinta babban limami ne a unguwarsu. Da Hajiya 'Yar Shehu ta tasa, mahaifinta bai gaza ba domin ya sa ta

makarantar boko a zamanin da mafi yawan iyaye ke }yamar ilimin boko ba ga ‘ya’ya mata ba ka]ai har ma da ‘ya’ya maza. Wannan ilimi da ta yi ya ba ta damar aiki a asibiti na tsawon shekara]aya kafin daga baya ta bari ta yi aure.

Bayan mutuwar aurenta na fari ne ta koma ga aiki, inda ta yi aikin koyarwa sa’annan daga baya ta samu aiki a kamfanin jiragen sama na }asa (Nigerian AirWays). Ta da]e tana aiki da kamfanin inda ta ri}e mu}amai da dama a wannan wuri. Ta yi ritaya daga aikin a 1981, daga nan sai ta kafa kamfanin jan bulo inda ta]auki ma’aikata da dama suka ri}a aiki a }ar}ashinta.

A ~angaren adabi kuwa, Hajiya ‘Yar Shehu ta rubuta wa}o}i da dama daga cikinsu akwai: Wa}ar “Aikin Hajji” (1959) da wa}ar “Ahmadu Bello Sardauna” (1960) da wa}ar “Yabon Soja” (1967) da wa}ar “Garga]i” (1970) da wa}ar “Zamani” da wa}ar “{idayar Mutanen Nijeriya” (1973) da wa}ar “Bayani” (Bayanin ya}in Biyafara) da sauransu. Hajiya ‘Yar shehu na]aya daga cikin mambobin }ungiyar marubuta wa}o}i ta su Mudi Sipikin, wato Hikima Kulob.

Hajiya Hauwa Gwaram

An haife Hajiya Hauwa Gwaram a garin Gwaram ta cikin jihar Jigawa (a yanzu, tsohuwar jihar Kano a da) a shekarar 1940. Ta fara karatun Allo a wajen mahaifinta wanda dama Babban malami ne, ta sami damar shiga makarantar boko har ta kai aji

hu]u.

Ta ~angaren aikace-aikacen da Hauwa Gwaram ta yi kuwa, ta fara aiki a ma'aikatar ilimi ta jihar Kano inda ta koyar da mata ya}i da jahilci. Daga nan kuma ta sami damar halartar kwas a asibitin yara na Kano. Ta yi aure, tana da 'ya]aya a duniya.

Hajiya Hauwa Gwaram ta fara rubuta wa}o}i tun tana }arama, kuma ta ci gaba da samun basirar }ir}irar wa}a a lokacin da take koyar da mata ya}i da jahilci, domin a wannan lokaci a cewarta suna amfani da hanyar wa}a wajen koyar da darussan da suka shafi kiwon lafiya da tarihin }asa da sauransu, don haka ta ri}a shirya wa}o}i domin amfani da su wajen koyarwa, domin ta lura karatun ya fi shiga a wa}e.

Haka kuma, Hajiya Hauwa na]aya daga cikin wakilan fitacciyar }ungiyar nan ta marubuta wa}o}in Hausa mai suna Hikima Kulb, wadda ake yawan sa wa}o}insu a gidajen rediyo a wancan lokaci don ilmantar da al'umma. Har wa yau, ta yi aiki a }ungiyar matan Arewa, inda ta ri}a rubuta wa}o}i don ilmantarwa kan kula da lafiyar mata masu juna biyu da yara da sauran al'umma baki]aya. (Mack 2004: 18).

Ta ~angaren rubuta wa}a kuwa, Hajiya Hauwa Gwaram ta rubuta wa}o}i da dama wa]anda suka ha]a da: wa}ar Ta'aziyyar Tafawa |alewa da sardaunan Sakkwato (1966), da wa}ar "{idaya" (1972), da wa}ar "Gidan Abdu Ba}o Zu", (1973), da wa}ar "Mu ci da {asarmu" (1976), da wa}ar "Shirin Tu}i Hannun Dama," da wa}ar "Lullu~i ga Mata". (Balbasatu 2008:110).

A Hirar da Beverly Mack ta yi da Hajiya Hauwa Gwaram ta bayyana ma ta cewa a yayin da suke koyar da mata ya}i da jahilci sukan ba darussan addini da tarihin }asa muhimmanci. Domin haka ne ma ta shaida mata cewa:

> Yayin da muke aikin (ya}i da jahilci) idan na ga wani ya yi wani abin }warai ko abin mamaki a Kano, kuma na ga akwai bu}atar a adana tarihin wannan abu da ya yi, sai in rubuta wa}a a kai don adana wannan tarihi… (Mack, 2008: 20).

Hajiya Hauwa Gwaram ta ci gaba da amfani da wa}a wajen ilmantarwa da fa]akar da al'umma a kan abin da ya kamata al'umma su sani na daga harkokin duniya da lafira. Allah ya yi wa Hajiya Hauwa Gwaram rasuwa a 1998. (Allah ya gafarta mata).

Ru}ayyatu Sabuwa Nasir

Ru}ayyatu Sabuwa Nasir na]aya daga cikin matan Kano marubuta wa}o}in Hausa. An haifi malama Ru}ayyatu a shekarar 1948 a Adakawa cikin garin Kano. Ta fara karatun addini a hannun mahaifinta malam Nasiru Ahmad wanda sanannen malami ne a Kano. Ta kuma samu shiga Islamiyya inda ta zurfafa karatunta na {ur'ani tare da samun ilimin litattafan addini wa]anda suka ha]a da Hadisai da Fi}ihu da Tauhidi da Nahawu da sauransu. Malama Ru}ayya ta fara rubuta wa}o}i tun tana 'yar shekara goma sha]aya da haihuwa a 1959. Haka kuma, ta yi aure har ma tana da 'ya'ya da jikoki. Kamar sauran marubuta wa}o}i na Kano, malama Ru}ayya na]aya daga cikin mambobin Hikima Kulob. Fitacciyar wa}ar marubuciyar ita ce wa}ar Kishi wadda

take garga]in mata game da illar kishi.

Raihanatu Usman

Mace ta gaba a jerin marubuta wa}o}i ita ce malama Rahanatu Usman. Malama Rahanatu mutuniyar Maiduguri ce, wato Babarbariya ce. An haife ta a shekarar 1950 a garin Azare da ke cikin jihar Bauchi. Ta yi karatun Allo har ta sauke al-{ur'ani mai girma, haka kuma ta samu shiga makarantar koyon Larabci da ke garin Jos a 1984-1987. Ta yi aure tana 'yar shekara 12 da haihuwa inda ta auri malam Ali har ta samu haihuwar 'ya'ya biyu da shi, amma daga baya suka rabu ta sake aure, inda ta auri malam Adamu Isa Azare, a nan ma ta sami haihuwar 'ya'ya biyu sai Allah ya yi masa rasuwa, daga baya ta sake yin aure a Kano inda ta haifi 'ya'ya uku a gidan mijinta na uku. Malama Rahanatu ta yi aikin koyarwa a makarantun firamare ta Festibal da ta Jar}asa, daga baya ta koma garin Kaduna da zama. (Ahmad, 2004:30) da (Balbasatu: 119).

Malama Rahanatu ta fara rubuta wa}o}i a shekarar 1967, wa}o}in nata sun shafi fannonin addini da siyasa da al'adu da kiyon lafiya da yabo da wayar da kai da tsarin zaman tare da kishin }asa da sauransu. Daga cikin wa}o}in da ta rubuta akwai wa}ar "Ri}on Amana" da wa}ar "Ilimi" da wa}ar "Harshen Hausa" wadda ta gabatar a taron makon Hausa na ABU Zaria a 1997. Har yanzu malama Rahanatu na nan na ci gaba

da bayar da gudummawarta wajen ilmantarwa da fa]akar da al'umma.

Amina Muhammadu Anda

An haifi Malama Amina a 1953 a cikin garin Funtuwa. Sunan mahaifinta Malam Ibrahim sarkin barkono, ta tashi ne a hannun }anin mahaifiyarta wato Alhaji Muhammadu Anda Funtua, wanda ke zaune a bakin Kasuwar Mata Funtua. Ta fara karatun Islama tun tana }arama kuma ta sami damar shiga makarantar firamare inda ta samu ta yi aji biyu kawai domin ta bar garin Funtuwa a wannan lokaci ta koma Bakori hannun mahaifiyarta, daga baya ta dawo hannun kawunta sai dai ba ta sami damar ci gaba da karatu ba a wannan lokaci sai aka yi mata aure. Malama Amina ta yi aure tana 'yar shekara goma sha biyu da haihuwa tana da 'ya'ya tara amma biyu sun rasu saura bakwai.

Ta ~angaren rubuta wa}a kuwa, malama Amina ta fara rubuta wa}o}i tun tana da shekara uku da aure. Ta rubuta wa}o}i da dama wa]anda suka shafi addini da siyasa da ci gaban matasa da ci gaban }asa baki]aya, kuma tana]aya daga cikin 'yan {ungiyar Manazarta da Marubuta Wa}o}in Hausa. Ta kasance tana halartar gasar manazarta da marubuta wa}o}in Hausa inda a ranar 6/3/ 1999 ta lashe gasar da aka yi a Zamfara har ma ta sami kofin da sarkin Zazzau ya sa, wanda shi ne aka sa wa wadda ta lashe gasar sashen mata. Har wa yau, ta kasance tana]aya daga cikin 'yan {ungiyar Mata Musulmi mai suna Al-Da'awa Ila Sira]il Musta}im, (ita ce jami'ar hul]a da

jama'a ta reshen }ungiyar da ke Funtuwa).

Daga cikin wa}o}in da Amina Anda ta rubuta akwai wa}ar *Matasa* wadda ta rubuta a ranar 22/9/1971 da wa}ar "Khalifa Baba Ahmed" (30/1/1972) da wa}ar "'Yan }wallo" (19/10/1996) da wa}ar "Yabon D.P.N" (23/2/1997) da wa}ar "Ri}on Amana da wa}ar "Nagari na kowa" da wa}ar "Ta'aziyyar Matasan da suka rasu a ha]arin mota" da wa}ar "Hausa Fasaha" da wa}ar yabon "Makarantar Hizbu" da sauransu. Yanzu haka malama Amina na nan na ci gaba da karatunta na sakandire a makarantar A.T.C da ke garin Funtuwa inda take a shekarar }arshe, kuma ta shaida min cewa in dai da rai da lafiya da ta kammala za ta ci gaba da karatu domin samun Diploma a harshen Hausa da Larabci.

Shema'u Abdullahi

An haifi malama Shema'u Abdullahi a ranar 15 ga watan maris 1965 a }ofar Na'isa ta cikin garin Kano. Mahaifinta malam Abdullahi Aliyu [ansidi (wamban Zazzau) ya zauna Kano ne (a lokacin haihuwarta) sakamakon aiki da ya kai shi can a }ar}ashin Ma'ikatar Lafiya ta jihar Kano. Ta tashi a gidan magatakardan sarkin Zazzau Aliyu [ansidi a hannun yayar mahaifiyarta. Ta fara karatun allo a hannun malam Sa'idu mai 'yan makaranta na gidan Liman Durum. Ta sauke {ur'ani mai girma tana da shekara tara da haihuwa. Ta samu shiga Islamiyyar gidan Nuhu Bamalli (magajin garin Zazzau) a 1977, haka kuma ta samu shiga makarantar firamare a wannan shekara inda

ta shekara biyu kacal (1979), sai ta samu wucewa makarantar ‘yammata ta Sarauniya Amina (Queen Amina College) da ke Kaduna inda ta karanci fannin Kasuwanci (commerce). Bayan nan, ta yi Diploma a harshen Larabci a jami’ar Ahmadu Bello, Zariya a shekarar1988- 1991. Ta kuma samu komawa jami’ar domin samun digiri a harshen Larabci a tsangayar fasaha, sashen harsunan Nijeriya da Afirka daga shekarar 2002-2005, yanzu haka tana ci gaba da karatun digiri na biyu a fannin Larabci a wannan sashe.

Malama Shema’u ta yi aikin koyarwa a wurare da dama kamar makaranta Jama’atu (Jama’atu College) daga 1983 – 1992, (ita ce malama ta farko a makarantar bayan shugabar makaranta). Daga nan, sai ta koma da aiki a }ar}ashin Hukumar Ilimi ta Zariya, daga 1992 – 2006, a matsayin malamar Larabci, daga nan sai makarantar gaba da sakandire ta Amir Shehu Idris, inda take aiki a sashen fasaha na makarantar har inda muke yau.

Ta ~angaren rubutattun wa}o}i kuwa, malamar ta fara rubuta wa}o}i ne tun tana }arama, kuma ta rubuta wa}o}i da dama ya zuwa yau, wasu daga cikin wa}o}in na ta sun ha]a da: wa}ar “Ilimi” da wa}ar “Gaskiya” da wa}ar “Mace Uwar Al’umma” da wa}ar “Jami’ar Ahmadu Bello” da wa}ar “Zamani” da wa}ar “Wuri” da sauransu. Haka kuma, ta rubuta wa}o}i cikin harshen Hausa da Larabci.

Malama Shema'u ta yi aure a 1984, yanzu tana da 'ya'ya takwas, tana zaune a unguwar }ofar Gayan da ita da mai gidanta Dr. Umar Ibrahim na tsangayar Ilimi ta Jami'ar Ahmadu Bello Zaria.

Zuwaira Isah

An haifi Zuwaira Isah a 1967, a cikin garin Bauchi. Ta fara makarantar Allo a makarantar malam |oyi da ke cikin garin Bauchi, haka kuma ta sami zuwa Islamiyya da makarantar Firamare duk a garin Bauchin, daga shekarar 1974 – 1980. Ta ci gaba da karatun boko a }ar}ashin shirin ilimin Manya, bayan da ta yi aure, kuma ta yi karatu a makarantar Cibiyar Addinin Musulunci da ke garin Jos, daga nan sai ta samu shiga kwalejin Ilimi ta Jos inda ta samu takardar shaidar malanta a fannin Larabci. (Balbasatu, 2008:123).

Ta fuskar adabi kuwa, Malama Zuwaira shahararriyar marubuciya ce musamman a ~angaren litattafan zube domin duk makarancin adabin kasuwar Kano ya san da zaman Zuwaira Isah, saboda haka ne ma ta kasance]aya daga cikin 'yan }ungiyar marubuta ta }asa wato (Association of Nigerian Authors, (ANA). Ta fuskar wa}a kuwa, marubuciyar ta rubuta wa}o}i da dama, daga cikinsu akwai wa}ar "Jirgin Kabo" da wa}ar "Neman Ilimi ga]iya mace" da sauransu.

1.9 Na]ewa

Wannan babi na]auke da gabatarwa ne ta wannan bincike. A wannan gabatarwa an kawo shimfi]a da manufar bincike da dalilan da suka haifar da wannan bincike da kuma muhimmancin bincike da iyakacin bincike da kuma hanyoyin gudanar da wannan bincike.

Har wa yau wannan babi ya gudanar da sharar fage kan nazarin matsayin mata a }asar Hausa da kuma irin gudummawar da mata suka bayar musamman a ~angaren rubutattun wa}o}i. Haka kuma, aikin nan ya yi tattaki tare da kawo tarihin mata marubuta wa}o}in wa'azi na }arni na ashirin (wa]anda aka za~i wa}o}insu domin yin nazari).

WAIWAYE KAN AYYUKAN DA SUKA GABATA

2.0 Shimfi]a

Masu iya magana kan ce “waiwaye adon tafiya” abin nufi a nan shi ne komai mutum zai yi ya ri}a waiwayawa baya domin duba yadda magabata suka yi, wannan zai sa aikinsa ya yi inganci. Saboda da haka ne wannan babin ya }unshi waiwaye da sharhi a kan ayyukan da suka gabata masu ala}a da wannan batu na wa’azi a rubutattun wa}o}in mata na }arni na ashirin.

A waiwayen da aka yi, an fara da kawo ra’ayoyin masana game da ma’anar wa’azi, sa’annan aikin ya binciko ayyukan da aka gudanar kan samuwar rubutattun wa}o}in wa’azi a }asar Hausa. Haka kuma, an yi sharhin ayyukan da aka gudanar a kan rubutattun wa}o}i musamman ma wa]anda suka shafi jigon wa’azi da wa]anda suka shafi addini da sauransu . Haka kuma, an kawo sharhi kan ayyukan da aka gudanar a kan amfanin wa}a wajen kyautata tarbiyyar al’umma, da kuma ayyukan da aka gudanar kan nazarin ayyukan mata ta fuskar adabi. An shirya wannan bita ne a tsarin gabatar da kundayen bincike a farko, sai aka kawo litattafan da aka wallafa, sa’annan a }arshe aka kawo }asidu da mu}alu masu nasaba da wannan aikin. Har wa yau, an tsara kawo sharhin ne a tsarin }waryar goro, wato an]aura batutuwa masu ala}a da juna a kowace }warya. An yi wannan ne domin samun inganci a aikin.

2.1 Ma’anar Wa’azi:

Kalmar wa'azi ta samo asali ne daga kalmar Larabci ta wa'aza, wadda ke da ma'ana ta lugga da ke nufin]aga murya, amma a ma'anar ta al'ada, wa'azi na nufin fa]akarwa. A cikin }amusun nan na Larabci mai suna *Mukhtarus sihah* na Muhammad bin Abubakar bin Abdulgaffar Raziy (1979), ya bayar da ma'anar wa'azi da cewa "kalmar wa'aza na nufin nahisa, tunatarwa da garga]i. har ma ya }ara da karin magana cikin Larabci da ke cewa "Assa'idu huwa man wi'iza bi gairihi" wato mai hankali shi ne wanda ya wa'aztu da waninsa. Wannan karin magana ta yi daidai da karin maganar nan ta Hausa da ke cewa "Gani ga wane ya ishi wane tsoron Allah.

Daga wannan bayani da ya gabata, za a fahimci cewa Bahaushe ya ari wannan kalma ta wa'aza ne daga Larabci, sai ya mayar da ita 'wa'azi' wadda ke nufin fa]akarwa kamar yadda ma'anarta take a Larabci (wato ma'anar ba ta canza ba).

Masana da dama sun tofa albarkacin bakinsu game da abin da suka fahimta dangane da ma'anar wa'azi daga, cikinsu akwai:

Bargery, (1934; 1070-1071) a }amusunsa, ya bayar da ma'anar kalmar wa'azi a matsayin fa]akarwa, ko garga]i, ko kira ga dokokin addini. Haka kuma, ya bayyana cewa kalmar ta }unshi kalmomi irin su wa'azta, da wa'aztu da wa'azu.

Sa'id (1978; 98) ya bayyana wa'azi da cewa shi ne kiran jama'a ga addini da fahimtar da su abubuwan da Allah ke so su aikata su, haka bayyana musu wa]anda ba ya so domin su nisance su. Wannan shi ne abin da aka sani da amri da nahayi a

addinin Musulunci.

Malumfashi, (1984) ya bayyana wa'azi da cewa asali ko tsuttsugen kalmar daga Larabci take, (kamar yadda wasu masana suka bayyana) wadda ke nufin tunatarwa a kan abin da ke }arfafa zukata a kan ayyukan lada ko na zunubi, ko kuma yin nasiha. Ya }ara da cewa 'wa'azi' kalma ce mai ala}a da addini domin ta fannin addini ne kawai ake maganar lada ko zunubi.

Yahya, .I. Y. (1988; 54), ya bayar da ma'anar wa'azi da cewa shi ne garga]i ta yin horo da hani kan wa]ansu halaye da ba su dace da tafarkin addini ba.

{amusun Hausa, (2006; 464), a nasu bayanin sun bayyana cewa wa'azi shi ne jawabi kan abin da ya kamata Musulmi ya yi da abin da bai kamata ya yi ba ta kawo hujjoji daga {ur'ani da Sunna, da niyyar mai da al'ummar Musulmi tafarkin gaskiya. Wa'azi na nufin fa]akar da al'umma a kan hukunce-hukuncen addinin Musulunci.

Ta yin la'akari da bayanan da suka gabata, za a fahimci cewa wa'azi ya }unshi ilmantarwa da fa]akar da al'umma ta hanyar amfani da hanyoyi daban daban wa]anda suka dace da al'ummar da ake wa wa'azin. Wasu daga cikin hanyoyin da malamai kan bi wajen wa'azantar da al'umma sun ha]a da karantarwa, da tunatarwa da rubuce-rubucen wa}o}i.

Wa'azi muhimmin abu ne ga rayuwar kowane Musulmi domin ta hanyarsa ne

Musulmai kan sami ilimin abin da ya wajaba a kansu da abin da ya haramta a gare su, wato wa'azi hanya ce mafi sau}i ta ilmantar da al'umma game da hukunce-hukuncen addini da kuma azabar da Allah ya tanadar wa wa]anda suka }etare haddi. Wannan dalili ne ya sa Shehu Usmanu a wa}arsa ta Tabban Ha}i}an ya bayyana cewa:

Kui nazar 'yan uwa ku samu ku duba,
Don nasiha ku zam fa]i don muhibba,
Mui ta bin godabe mu tcere azaba,
Duk ku saurari za ni wa}a ku tuba,
Mui ta bin godabe mu tcira tabban ha}i}an.

Haka kuma a wani baitin ya }ara da cewa:

Wa'azu na anka yo da]a ku falka,
Don ka shirya ma gobe can inda za ka,
Bari zuwa yanzu-yanzu ro}o a ba ka,
Mai fa ro}o da yaf faye gobe huska,
Tai ana karkare ta tabban ha}i}an.

Ashe wajibi ne ga Musulmi mu kasance masu wa'azi da nasiha ga junanmu, domin yawan tunatarwa na hana wa mutane mantawa da dokokin Allah.

2.2 Samuwar Rubutattun Wa}o}in Wa'azi a {asar Hausa

Da yake wannan aiki ya ta'alla}a ne a kan nazarin jigon wa'azi a rubutattun wa}o}in mata na wa'azi na }arni na ashirin, aikin ya waiwaya baya ya nazarci tarihin samuwar rubutattun wa}o}in addini a }asar Hausa, domin wa'azi na]aya daga cikin manyan jigogin wa}o}in addinin Musulunci.

Rubutattun wa}o}i na wa'azi wa}o}i ne da aka rubuta domin garga]i da jan hankalin jama'a a kan muhimman al'amurran da suka shafi addinin Musulunci. Wa]annan wa}o}i sun samo asali ne daga rubutattun wa}o}in Larabci na addini wa]anda malamai suka ri}a aron tsarinsu domin rubuta wa}o}in addini cikin harshen Hausa. Masana da dama sun yi ittifa}in cewa rubutattun wa}o}in addini sun samu ne sakamakon shigowar Musulunci }asar Hausa da kuma samar da hanyar rubuta Hausa da babba}un Larabci. Wannan dalili ne ya ba malamai damar rubuta wa}o}i cikin harshen Hausa.

Sa'id (1978;12-15) ya bayyana cewa: Tarihin rubutaccen adabin Hausa yana tafiya ne tare da tarihin shigowar Musulunci a }asar Hausa. asali malaman Musulunci ne suka zo da shi, wa]anda suka shigo }asar nan ta fuskar sahara, wa]ansu don kasuwanci, wasu kuwa domin gudun ceton rai." Marubucin ya kawo hasashen da ake game da tarihin zuwan Musulunci }asar Hausa, wanda ya ha]a da hasashen da ake cewa Musulunci ya shigo }asar Hausa ne a }arni na tara sakamakon zuwan Bayajidda wanda yana]aya daga cikin Umawiyyawa wa]anda Abbasiyawa suka fatattaka lokacin da suka hau mulki.

Haka kuma, ya bayyana cewa ana hasashen Musulunci ya zo }asar Hausa ne tsakanin }arni na sha biyu zuwa na sha uku, sakamakon cinikayya tsakanin Hausawa

da Larabawa da Wangarawa. Wanda akwai tabbacin cewa Wangarawa ne suka kai Musulunci }asar Katsina da Kano, kuma sun kakkafa makarantu domin koyar da addini. A ta}aice, Marubucin ya bayyana cewa daga nan ne aka fara samun cu]anya tsakanin harshen Hausa da Larabci, wanda ya zama tushen samun rubutun ajami a }asar Hausa. Domin haka, sai aka sami damar rubuta wa}o}i a cikin Hausa da tsarin rubutun ajami a wancan lokaci.

Ra'ayin Hiskett (1975; 12 -13) na da ala}a da na Sa'id, domin shi ma cewa ya yi, rubutattun wa}o}in addini na Hausa sun samu ne sakamakon }o}arin da malamai suka yi na kawar da wa}o}in baka na Hausa da suka sa~a wa addini, a farkon kafuwar Musulunci a }asar Hausa. Haka kuma, marubucin ya bayyana cewa idan har ana son sanin tarihin samuwar rubutattun wa}o}in addini na Hausa, sai an koma zuwa ga tarihin zuwan Musulunci }asar Hausa da kuma bun}asarsa. Domin haka, sai ya yi ta}aitaccen tsokaci a kan yadda Musulunci ya shigo }asar Hausa, da kuma yadda ya watsu. Ya bayyana cewa Musulunci ya sami tsayawa da diga-digansa a }asar Hausa a wajen }arni na sha biyar, sanadiyyar namijin }o}arin wasu malamai (irin su malam Muhammad ibn Abdulkarim al-Maghili) wajen koyar da mutane addini da yin rubuce –rubucen domin ya]a addini. Wa]annan malamai sun sami wannan dama ce sakamakon ha]in kai da suka samu daga wajen sarakuna na wancan lokaci. Wannan dalili ya sa sannu a hankali sai aka ri}a samun sauyi a rayuwar al'umma a wancan

lokaci, mutane suka ri}a kar~ar addini tare da neman ilimin addinin, da haka ne aka ri}a samun malamai (‘yan }asa) suka ri}a kwaikwayar rubutun larabci wajen rubuta Hausa (ajami). Sakamakon haka ne ya sa aka sami adabin Musulunci cikin Hausa (rubutattun wa}o}i na]aya daga ciki).

Yahya (1988; 31) ya danganta samuwar rubutattun wa}o}in addini na Hausa da samuwar rubutun ajami. Ya bayyana cewa a }arni na sha bakwai an sami ci gaba da ya]uwar ilimin addini, da samuwar malamai. Kuma an sami wa]ansu rubuce-rubuce da ake kyautata zaton a wannan }arnin aka yi su, daga cikin wa]annan rubuce-rubuce kuwa akwai rubutattun wa}o}in Hausa kamar wa}ar *Shi’ir Hausa* da *Jamuya* na Sheik Ahmad Tila da wata wa}ar Hausa ta Abdurrahman Tajiddin da sauransu.

Ibrahim (1978; 93-94) ya bayyana cewa rubutattun wa}o}in addinin Musulunci sun samu ne bayan zuwan Musulunci }asar Hausa. Ya kawo hasashen da wasu daga cikin masana tarihi suka yi na cewa Musulunci ya zo }asar Hausa ne zamanin sarkin Katsina Muhammadu Korau (1320-1353) da kuma zamanin sarkin Kano Aliyu Yaji (1349-1385). Haka kuma, ya }ara da cewa Musulunci ya ha~aka ne a zamanin sarkin Kano Muhammadu Rumfa (1463-1499) da zamanin sarkin Katsina Ibrahim Maje (1494-1520). A wannan lokaci ne ake hasashen fara samun rubutattun wa}o}in addini Musulunci cikin Hausa.

Dukkanin wa]annan marubuta sun danganta samuwar rubutattun wa}o}i da tarihin zuwan Musulunci }asar Hausa, domin Musulunci ne ya zo da rubutun Larabci wanda daga gare shi ne aka samar da hanyar rubutu ta ajami (rubuta Hausa ta amfani da haruffan larabci).

Rubutattun wa}o}i na wa'azi da ake da su a hannu da aka rubuta a }asar Hausa an rubuta su wajen }arni na sha bakwai zuwa na sha takwas. A lokacin manyan malamai sun fara amfani da rubutun ajami domin rubuta wa}o}in da suka shafi addini da harshen Hausa. Wannan ya faru ne kuwa sakamakon la'akari da suka yi da yawaitar wa}o}in hululu (wa}o}in baka da suka kauce wa koyarwar addinin Musulunci) a tsakanin al'umma. Wa]annan bayin Allah (malamai) sun za~i isar da sa}onsu na wa'azi ta amfani da rubutacciyar wa}a saboda tasirin da rubutattun wa}o}in Larabci suka yi a kansu. [aya daga cikin fittatun wa}o}in addini da aka fara samu a }asar Hausa a }arni na goma sha bakwai ita ce sananniyar wa}ar nan ta Wali Abduljalil [an Masani wadda aka fi sani da suna wa}ar "Badar." A binciken da aka yi an sami baiti arba'in da takwas ne na wa}ar. Wannan wa}a na bayanin irin karon battar da Musulmin farko suka yi da kafirai a ya}in Badar wanda aka yi zamanin manzon Allah, Annabi Muhammad (S.A.W) kamar haka:

Bismillahi suna ne na Allah Ta'ala,
Za ni yabon Rasullullah, macecinmu bayi.

Na ji yabonka na da yawa na iba ka]an na yi,
Na yi wa}ar da babu shina tana ka da barci.

Nai haramar yabo da yawa, na diba ga gulbi
Gulbi mai ruwa tari, da]a sai da jirgi.

Al}ur'ani jirgi ne da ya zo da fa]i,
Shi Jibrin ya kawo shi wurin Sahibinai.

Kowah hau shi ya huta, ku san ba shi }una,
Jalla Jalala mai iko da ya yo mu mu duk,
Tun can awwalun fari, halitta ga bayi .

Na rantse da yin Allah ku san ba ni }arya,
A cikin Annabawa, ba ya tamfal Fiyayye.

Za ni yabonka Gamzaki da ka zo da haske,
Hasken naka na da yawa yana shafe rana.

Annabi kai muka wa murna cikin Annabawa,
Kai ne awwalun fari, da ka zo a baya.

Mai }udura da yai iko, da za~en ka ya yi,
Ya za~e ka tun farin halitta ga bayi.

Ya warke mu mun warke da zancen da ya wo,
Ya hana mu bin bidi'a da aikin ma'asi.

Mutan Makka sun murna da saukar Fiyayye,
Amma sai da anka kara, takubba da masu.

(Ibrahim 1978; 95-97 da Yahaya 1988; 39-42).

Wannan ka]an ke nan daga yabon da marubucin wannan wa}a (Wali [anmasani) ya yi

ga Manzon Allah Annabi Muhammadu (S.A.W) daga nan ne ya ci gaba da kawo labarin artabun da aka yi tsakanin kafiran Makka da Manzo (S.A.W) da Sahabbansa kafin a samu a tabbatar da kafuwar Musulunci a Makka.

Haka kuma, }arni na sha takwas kuwa, wa}ar wa'azi da ta shahara a wannan lokaci ita ce wa}ar *Gangar Wa'azu* wadda ake kyautata zaton Malam Muhammadu na Birnin Gwari ne ya rubuta ta (ko da yake akwai ra'ayin da ya sa~a wa haka daga masana da dama dangane da marubucinta).

Bayan Musulunci ya samu gindin zama a }asar Hausa, har ma ya mayar da }asar cibiyar neman ilimin addini sakamakon kakkafa makarantun addini da aka yi a wancan lokaci (tsakanin }arni na 12 – 15). Sannu a hankali sai al'amurra suka fara ta~ar~arewa, Musulunci ya fara shiga wani yanayi sakamakon komawar da al'umma ta fara yi ga jahilci da kafirci da maguzanci. Sarakuna suka koma wa zalunci da danniya da mulkin kama karya da sauransu. Malamai kuwa suka manta da wa'azi da neman ilimi da ya]a shi, sai fadanci. Don haka komai ya jagule, jama'a suka shiga cikin halin }a}a-nika yi.

A cikin wannan yanayi ne Shehu Usman [anfodiyo ya bayyana. Shi dai Mujaddadi Shehu Usmanu ya fito ne daga }abilar Torankawa (Fulani) wa]anda iyayensa da kakanninsa suka sauka a Maratta ta }asar Gobir tun wajen }arni na 13. Sun kuwa

zauna a wannan wuri ne domin ya]a addini. Suna ta ci gaba da harkokinsu na ilmantarwa ne aka haifi Shehu a shekarar 1754. Shehu ya fara neman iliminsa ne a wajen mahaifansa da wasu manyan malamai. Da tasawarsa bai yi wata-wata ba sai ya shiga wa'azi da koyar da addini da kuma]ora mutane kan tafarkin gaskiya. Sannu a hankali Shehu ya shahara, har ta kai ga sarkin Gobir Bawa Jan gwarzo ya janyo shi zuwa Al}alawa domin koyar da 'ya'yansa addini. A cikin]an }an}anin lokaci Shehu ya sami kar~uwa ga jama'a, sarakuna da talakawa.

Bayan mutuwar sarkin Gobir Bawa Jan gwarzo, sai]ansa Yakubu ya hawo gadon sarautar Gobir (1794 -1800). Yakubu bai da]e a gadon sarautar Gobir ba ya rasu. Sai Nafata ya gaje shi (1800 – 1802), shi ma dai shekara biyu ka]ai ya yi ya mutu. A lokacinsa ne Shehu ya fara samun matsala da sarakunan Gobir, domin Nafata ya nuna }iyayya ga Musulunci da kuma ga Shehu da mabiyansa saboda yadda ya ga Shehu na samun magoya baya a kullum. Wannan dalili ya sa Shehu ya bar Al}alawa ya koma Degel, ya ci gaba da ya]a addini, kuma ya ci gaba da samun magoya baya daga ko'ina suka ri}a kwarara zuwa Degel. Wannan abu ya da]a firgita Nafata har ya kai ga ya sanya dokoki masu tsauri ga Musulmi.

Bayan mutuwar Nafata sai]ansa Yumfa ya gaje shi (1802 -1808). Hawansa ke da wuya ya nuna ya fi ubansa }in Musulunci, domin a lokacinsa ne al'ammurra suka }ara jagulewa tsakanin masarautar Gobir da Musulmi, wanda hakan ya sa Shehu da

mabiyansa suka yi hijira daga Degel zuwa Gudu (1804) sakamakon tsananin musgunawa da yawan hare-hare da ake kai musu.

Da Yumfa ya ga haka, sai kuma ya nemi a shiri da Shehu, ya aika wa Shehu da ya dawo }asarsa a yi zaman lafiya. Shehu ya amince amma da shara]in in zai yi masa al}awarin abu biyu:

-

- Sarki ya tuba ya gyara addininsa ya zama musulmi na gari.
- Ya yi adalci cikin mulkinsa, ya maido wa jama'a dukiyoyinsu da ya }wace bisa zalunci kuma ya saki mutanen da ya]aure ba bisa ha}}insu ba.

Malamin da ya zo karanta wa Yumfa sa}on Shehu sai ya sassauya abin da aka rubuta da a takardar, maimaikon ya karanta sa}on Shehu sai ya kawo }arairayi da zage zage da za su tunzura Yumfa ya janye shirinsa na sulhu. Haka kuwa aka yi, domin da Malaman da Yumfa ya tara suka ji haka, sai suka ba shi shawarar]aukar matakin soji a kan Shehu da mabiyansa. Da ma Hausawa kan ce "Ba a mugun sarki, sai mugun bafade." Wannan dalili ne ya haddasa ya}in da aka gwabza a tafkin Kwatto, tsakanin Musulmi da Masarautar Gobir wanda daga }arshe Shehu da mabiyansa suka yi nasara, aka kashe sarkin Gobir Yumfa, aka kawar da mulkin Gobirawa, kuma aka kafa daula ta Musulunci }ar}ashin jagorancin mujaddadi Shehu Usmanu. Daga nan Shehu ya raba tutoci ga manyan almajiransa, ya umurce su da su }addamar da jihadin]aukaka kalmar Allah da jaddada addini a fa]in }asashen Hausa, wanda a }arshe duk inda suka

je sai da suka yi nasara. Har wa yau, wannan jihadi ne sanadin ha]uwar kan }asashen Hausa a }ar}ashin daula guda, wadda sarkin musulmi ke shugabanta. Wannan tsari ya ci gaba da tafiya har zuwa wannan zamani da muke ciki.

(An samu mafi yawa daga wannan bayani ne daga Sa'id: 1978;p19- 31).

A }o}arin Shehu Usman [anfodiyo da mabiyansa na ganin sun dawo da mutane kan tafarkin shari'a ne ya sa suka du}ufa wajen rubuta wa}o}in wa'azi domin koyar da addini, da kuma kawar da wa}o}in baka na hululu da suka shiga zukatan jama'a a wancan lokaci. Wasu daga cikin wa}o}in wa'azi da aka rubuta a wannan lokaci sun ha]a da:

Wa}ar "Tabban Ha}i}an" ta Shehu Usmanu

Wa}ar "Lalura" ta Shehu Usman

Wa}ar "Tunatarwa Ga Zuwan Mutuwa" ta Abdullahi Fodiyo

Wa}ar "Godaben Gaskiya" ta Nana Asma'u

Wa}ar "Ba}in Mari" ta Muhammad Tukur

Wa}ar "Alamomin }arshen zamani" ta Dikko [an Bagine

Wa}ar "Tuna Mutuwa" ta Isan Kware

Wa}ar "Halin Duniya" ta Isan Kware

Wa}ar Wa'azi da Tsoratarwa" ta Isan Kware

Wa}ar "Hawan Sira]i" ta Hassan [an Shehu

Wa}ar “Jan Mari” ta Salihu [an Zama da sauransu.

A wa}ar Tabban Ha}i}an Shehu Usmanu ya tsoratar da Musulmi a kan }in bin dokokin Allah kamar haka:

8 Wanda duk yab bi]o ga rai nai sarauta,
Don shi sam dukiya shi samo bajinta
Don shi kur]a da]a cikin masu cuta,
Masu aza dukiya garin ban sarauta,
Babu shakka su }una tabban ha}i}an.

21 Wanda yak kwance al}awal ya yi zamba,
Dud da mai rena mumini sai shi tuba,
Ya yi sa~o ina kamatai ku duba,
Mai fa bautad da]a shi shawo azaba,
Shi ka bautaw wuta fa tabban ha}i}an.

33 Masu }eta da hasada can ga gobe,
Kai su aka yi wuta idan ta yi zobe,
In fa an kai su nan da nan sai su }abe,
Har miyagu da ke zina masu tarbe,
Duk wuta za su gobe tabban ha}i}an.
(Shehu Usmanu: wa}ar Tabban Ha}i}an).

Ha}i}a Shehu Usmanu ya yi garga]i ga masu sa~o da }in bin dokokin Allah, ya yi kira gare su da su tuba su koma ga Allah.

Haka shi ma Muhammad Tukur ya yi wa’azi da tsoratarwa ga Musulmi musamman kan azabar lahira ga duk wanda ya mutu yana aikata sa~o, har yana cewa:

Mu tashi mu gaugauta shiri kada ta far muna,
Fa am bar mu ba kowa ba yashe wurin shiri.

Fa mutuwa fa za ta da mu fa can }ar}ashin }asa,
Mu zo da nadama can da kewa fa mui shiri.

Ma}wabta na can tsutsa, kunama, macijiya,
Akaifun }aruffa jan dafi babba}u }irin.

Garin nan fa ba iska fa sai ko na guguwa,
Fa mai tsananin zafi ga can ba shi cin tari.

{ishirwa da yunwa duk da zilla da firgita,
Da zurfin zufa can babu rana da ba fari.

Zaman kafiri da munafiki yaf fi }umtata,
Da wahala da }an}anci fa gwamma zama kare.

A ba su kulake har su kai }ar}ashin }asa,
A jefo su maza maza nan su komo ga Munkari.

Haka kuma, ya kawo kwa]aitarwa a kan ni'imomin da aka tanadar wa muminai wa]anda suka kyautata ayyuka, ya ce:

Da da]i ga wansu idan fa sun kyauta aikuna,
A shimfi]a zinari gadonsu na alhari.

A gudan da }orammun zuma da farin ruwa,
Da madara da haske sa turare na marmari.

Tabbas wa]annan wa}o}i sun bayar da gagarumar gudummawa wajen wa'azantar da al'umma a cikin ruwan sanyi a wancan lokaci. Haka kuma mutane sun ri}a fahimtar

addini da sanin yadda za su bauta wa Allah ta hanyar wa]annan wa}o}i.

An ci gaba da samun bun}asar rubutattun wa}o}i na wa'azi a }arni na ashirin da }arni na ashirin da]aya, domin kusan mafi yawa daga cikin marubuta wa}o}i na wa]annan lokutta sun rubuta wa}o}i na wa'azi ga al'umma, wasu daga cikin shahararrun marubuta wa}o}in wa'azi na }arni na ashirin sun ha]a da Sarkin Zazzau Aliyu [an Sidi da Aliyu Namangi da Na'ibi Suleiman Wali da Salihu Kwantagora da Abubakar Gumi da Sa'adu Zungur da A}ilu Aliyu da Ummaru Wazirin Gwandu da Bello Gi]a]awa da sauransu (wa]anda yawansu da yawan wa}o}in nasu ba zai lissafu a wannan wuri ba).

2.3 Ayyukan Da Suka Shafi Jigon Wa'azi

A ~angaren kundayen bincike, an sami ayyuka da dama da suka yi kama da wannan aiki musamman ta fuskar jigo. An sami ayyukan da aka yi nazarin jigon wa'azi a rubutattun wa}o}in Hausa, kamar aikin [angambo (1980) da Birnin-Tudu (2002) da Asma'u (2006) wa]anda suka nazarci wa'azi a rubutattun wa}o}i amma ta fuskoki daban daban. A ~angaren littafan da aka wallafa kuwa, binciken ya kawo aikin Hiskett (1975)wanda ke da makusanciyar ala}a da wannan aiki domin ya shafi tarihin rubutattun wa}o}in addinin Musulunci ne da kuma nazartar wasu daga cikin wa}o}in kamar yadda wannan aikin yake, sai dai Hiskett bai ta~o wa}o}in da mata suka rubuta ba a }arni na ashirin. Ta fuskar mu}alu kuwa, an kawo sharhi kan mu}alar

Malumfashi (1984) da Aminu (2000) wa]anda suka shafi jigon wa'azi. Har wa yau, an kawo }asidun da Bashir (2009) da Suleiman (2009) da suka rubuta a jaridar Aminiya a kan sharhi kan darussan da ke cikin wa}ar "Gangar Wa'azu."

2.3.1 Kundaye

[angambo, (1980), a binciken da ya gudanar domin neman digiri na uku, ya yi nazari ne a kan wa}o}in wa'azi na shekarar 1800 zuwa 1970. A nasa aikin, marubucin ya kawo ma'anar wa'azi da ta}aitaccen tarihin wa}o}in wa'azi, sa'annan a babi na farko ya kawo wa}o}in da suka shafi wa'azi da garga]i, sai a babi na biyu ya kawo wa}o}in da suka shafi halin duniya da tuna mutuwa, a babi na uku kuwa ya kawo wa}o}i ne da ke]auke da alamomin tashin }iyama da bayyanar Mahdi, babi na hu]u kuwa na]auke da wa}o}in da suka shafi tashin }iyama da bayanin azabar wuta da kuma bayanin rahama da da]in da ke cikin aljanna dai sauransu, wa}ar Nana Asma'u ta "Tsayin }iyama na]aya daga cikin misalan da ya kawo a wannan babin. Kowane babi na wannan aiki na]auke ne da sharhin wa}o}in wato tsari da salon da ke cikin wa}o}in tare da ratayen wa}o}in. Ya kammala wannan aiki ne a babi na shidda inda ya nuna muhimmancin wa}o}in wa'azi wa]anda ya bayyana su da cewa kusan su suka mamaye mafi yawa daga jigogin wa}o}in wannan lokaci (1800-1970).

Birnin-Tudu, (2002), a kundin bincikensa na neman digiri na uku, ya gudanar da bincike ne a kan jigo da salon rubutattun wa}o}in Furu'a (hukunce hukuncen addini) a }asar Hausa. Aikin nasa ya nazarci jigo da salon uku daga cikin wa}o}in da ya za~a domin yin nazari yayin da daga bisani ya samar da wani kundi da ke]auke da]imbin wa}o}in Furu'a masu]auke da jigogi daban daban wa]anda suka ha]a da: wa}o}i hu]u kan tsarki da wa}o}i goma sha]aya kan salla da wa}o}i hu]u kan zakka da wa}o}i tara kan aikin hajji da wa}o}i biyu kan rabon gado da wa}o}i hu]u kan aure da wa}o}i biyu kan kasuwanci da wa}o}i biyu kan haddi da kuma wa}a]aya kan ladabtarwa. Manazarcin ya yi haka ne domin ya tabbatar da hasashensa na cewa lalle akwai]imbin wa}o}in furu'a (masu]auke da jigogi daban daban) a }asar Hausa.

A aikin Asma'u, (2006), ta gudanar da bincike na neman shaidar digiri na farko, ta yi nazarin "Tsoratarwa a Cikin Wa}o}in Wa'azi na Nana Asma'u, inda aikin nata ya ta~o ma'anar wa'azi da ma'anar wa}o}in wa'azi, wa]anda ta bayyana su da cewa wa}o}i ne da ke]auke da garga]i a kan bin dokokin Ubangiji domin samun kyakkyawar makoma. Har wa yau, ta nazarci jigogin wa}o}in wa'azi wa]anda ta bayyana da cewa akwai jigon hani da horo da bushara da kuma na tsoratarwa. Haka kuma, ta yi bayanin irin dabaru ko salailan da Nana Asma'u ke amfani da su wajen isar da sa}onta na kira ga guje wa miyagun]abi'u. Irin wa]annan salailai sun ha]a da salon zayyane

da salon kamance, inda ta yi amfani da baituka daga wa}ar Nana ta Godaben Gaskiya domin kare bayananta.

2.3.2 Litattafai

Hiskett, (1975) ya yi aiki a kan tarihin rubutattun wa}o}in addinin Musulunci a }asar Hausa. A sharar fagen da ya yi a littafin, ya nuna matsayin wa}a a }asar Hausa musamman kafin jihadi, inda ya nuna cewa akwai]imbin wa}o}in baka da ke }unshe da kirari da yabo musamman ga sarakuna na wancan lokaci, sai dai wasu daga cikin irin wa]annan wa}o}i sun sa~a wa addini saboda wa}o}i ne na hululu. Domin haka, da Malamai suka zo sai suka rin}a rubuta wa}o}in addini da za su maye makwafin wa}o}in hululu. Wasu daga cikin wa}o}in bakan da ya kawo domin kafa hujja sun ha]a da wa}ar Bawa Jangwarzo (1790) da wa}ar yabon sarkin Rano da sauransu. Marubucin ya kawo wa]annan misalai ne domin ya nuna dalilin samuwar rubutattun wa}o}in addinin Musulunci a }asar Hausa (wato domin kawar da wa}o}in hululu da koyar da addini cikin sau}i).

Haka kuma, marubucin ya yi sharhi kan yadda rubutattun wa}o}in addinin Musulunci suka faro da yadda suka ha~aka (zamanin jihadi) tare da yin sharhi kan jigoginsu wa]anda suka ha]a da jigon yabon Annabi (madahu) da jigon tauhidi da jigon sira (tarihin Annabi) har ma da jigon wa'azi (garga]i) da dai sauransu. Marubucin ya kawo

misalai daga wa}o}i daban-daban domin kafa hujja a kan kowane jigo. Daga cikin misalan akwai wa}ar wa'azi ta Muhammad Tukur mai suna "Ba}in Mari".

Hiskett bai tsaya ga nazarin wa}o}in masu jihadi ka]ai ba, har ma sai da ya ta~o wa}o}in da suka samu a }arni na ashirin wa]anda suke da jigogi daban daban (ba jigon addini ka]ai ba). Daga cikinsu akwai wa}ar Bagauda da wa}ar Tarihin Ha]eja da wa}ar Tabar}o}o da sauransu.

Aikin da Hiskett (1975) ya yi bakandamen aiki ne da ya taskace rubutattun wa}o}i musamman na addini tare da nazarin jigoginsu da tsarinsu da salonsu har ma da karinsu, sai dai duk da wannan aiki bai ta~o wa}o}in mata na addini sosai ba domin in ban da Nana Asma'u ba wadda ya kawo a cikin aikin nasa.

2.3.3 Mu}alu

Malumfashi (1984) ya }alubalanci masanan da suka bayyana cewa rubutattun wa}o}in }arni na ashirin wa}o}i ne na duniya. Ya yi wannan suka ne a takardar da ya gabatar mai suna "Wa'azi a Rubutattun Wa}o}in {arni na Ashirin," wadda ya gabatar a taron }ara wa juna ilimi a Sakkwato.

Marubucin ya fara ne da kawo ra'ayoyin masana game da wa}o}in }arni na goma sha tara da na }arni na ashirin. Haka kuma, ya kawo hujjojin da yake ganin su ne dalilan da ya sa wa]annan masana suka ta}aita jigon addini ga wa}o}in }arni na sha tara kawai. Daga cikin dalilan da ya kawo akwai yi wa Musulunci banasariyar fahimta,

wato ta}aita ma'anar addini ga al'ammuran lahira kawai, ko rarrabewa tsakanin al'ammurran duniya da na lahira.

Domin }ara fito da ma'anar addini ko wa'azi (wadda ya bayyana cewa za ta iya]aukar ma'anar addini; a duba shafi na 13) marubucin ya kawo ma'anar wa'azi, sa'annan ya mayar da raddi inda ya nuna cewa Nasara ba su ci galabar raba Musulmi (Hausawa) da addininsu ba. Hasali ma tasirin Nasaran ya fi shafar 'yan boko ne kawai.

Har wa yau, marubucin ya bayyana cewa wa}o}in da ake i}irarin 'yan duniya ne, wato irinsu wa}ar Tabar}o}o ta Aliyu [ansidi da wa}ar {azama da ta Basukur na Aliyu Namangi da wa}ar 'Yanci ta Sa'adu Zungur da wa}ar Salama ta Bello Gi]a]awa da sauransu, ya ce duk mummunar fahimta ake musu, domin idan aka koma aka sake dubansu da idon basira za a taras ba abin da ya raba su da wa}o}in addini irin su wa}ar Busharar Cin Birnin Al}alawa ta Shehu da wa}ar Kalambaina ta Abdullahi Fodiyo da wa}ar "Murnar Nasarar Ya}I" ta Nana Asma'u.

Ai dama ba yadda za a iya 'raba hanta da jini' wato ba yadda za a iya raba Musulmi da addini a kowane irin hali, domin ai rayuwar baki]ayanta addini ce. Domin haka, wannan bincike ya yun}uro ne domin goyon bayan wannan ra'ayi da }ara tabbatar da shi, tare da nuna cewa ba ma zaruman wa}a ka]ai ba (maza), hatta mata wa]anda ke]ari-]ari da rubuta wa}a sun rubuta wa}o}i na wa'azi a }arni na ashirin.

A yayin da Malumfashi (1984) ya yi wannan bayani, sai shi ma Aminu (2000) ya yun}uro domin goya masa baya. Shi bai ma tsaya ga }arni na ashirin ba, domin shi cewa ya yi ma ai a bar ta batun }arni na ashirin, wa}o}in jihadi na nan daram, har ma sun doshi goshin }arni na ashirin da]aya.

Marubucin ya yi wannan bayani ne a mu}alarsa mai suna “Wa}o}in Jihadi a Goshin {arni na ashirin.” shi ma ya fara ne da ra’ayoyin masana game da wa}o}in jihadi wa]anda ya nuna cewa wasu na danganta wa}o}in jihadi ne da wa}o}in }arni na goma sha tara kawai (wato kamar su Ibrahim (1981) da Abdul}adir (1979) da sauransu.) Marubucin ya ci gaba da bayyana cewa wa}o}in jihadi na ci gaba da samuwa har a goshin }arni na ashirin da]aya domin an sami wa}o}i da dama da ke nuna hakan. Daga cikin wa}o}in jihadi na goshin }arni na ashirin da]aya marubucin ya]auki wa}ar “Ba za mu bi Kwansitushan ba” ta Rabi’u Aliyu Kano, wadda ya bayyana da cewa ko ita ka]ai ta isa hujja wajen tabbatar da cewa har yanzu ana ci gaba da rubuta wa}o}in jihadi.

Kafin sharhin wannan wa}a, marubucin ya kawo ma’anar jihadi da tarihin marubucin da jigon wa}ar, wato bijire wa tsarin mulkin }asa da kira ga koma wa tafarkin Allah. Haka kuma, marubucin ya kawo tsarin wa}ar da salon da aka yi amfani da shi wajen isar da sa}on wa}ar.

Bashir (2009) (cikin jaridar Aminiya; kundi na 4 ta 28 shafi na 24) ya yi nazari da sharhi kan darussan da ke cikin wa}ar *Gangar wa'azu,* inda ya fito da muhimman darussan da wa}ar ta }unsa musamman a baitoci na 12 na }arshen wa}ar, nasihohin da ke cikin wa}ar sun ha]a da garga]i kan masu sata da masu lu]u/ma]igo da masu caca da mashaya giya da sauransu. Wannan }asida na da ala}a da wannan bincike saboda wa}ar da aka yi sharhi a kanta wa}a ce ta wa'azi.

Sulaiman (2009) (cikin jaridar Aminiya kundi na 3 ta 49; shafi na 24), ya yi tsokaci kan ra'ayoyin masana dangane da 'ko wa ya sha'irta Gangar wa'azu,' marubucin ya kawo ra'ayi da hujjojin masanan da ke ganin malam Muhammadu na Birnin Gwari shi ne ya sha'irta wannan wa}a. hujjojin kuwa su ne:

Wa}ar tana da salon bu]ewa da salon tsarin baituka irin na rubutattun wa}o}in malam Muhammadu na Birnin Gwari, ya kuma kawo baitoci na 6,7,8 da na 152 wa]anda ya ce wa]annan baitukan na }ara tabbatar da cewa malam Muhammadu shi ne marubucin wannan wa}a. Ya kuma nuna cewa da wa]annan hujjoji, shima yana tare da masu ra'ayin cewa malam Muhammadu na Birnin Gwari ya wallafa *Gangar wa'azu*.

2.4 Ayyukan da Aka Gudanar Kan Wa}o}in Da suka Shafi Addini

A nan ma an sami ayyuka da aka gudanar kan wa}o}in da suka shafi addini, an sami

wa]annan ayyuka ne wasu a matsayin kundayen bincike wasu kuwa a matsayin litattafan da aka wallafa, wasu kuma a matsayin mu}alu ko }asidu.

2.4.1 Kundaye

Sa'id (1978) a kundin bincikensa na neman digiri na biyu da ya sa wa suna "Gudummawar Masu Jihadi Kan Adabin Hausa" ya raba aikin nasa zuwa juzu'i biyu, a juzu'i na farko ne ya yi nazari kan aikace- aikacen (rubuce –rubuce) da masu jihadi suka yi musamman ta ~angaren rubutattun wa}o}i da nazarin yadda wa}o}in nasu suka taimaka wajen bun}asa rubutaccen adabin Hausa. A sharar fagen da ya yi ya kawo ta}aitaccen tarihin adabin baka da rubutacce kafin bayyanar Shehu, har ya kawo misalan wa}o}in baka na wancan lokaci da yake ganin suna daga cikin wa}o}in da suka assasa samuwar wa}o}in masu jihadi (wato wa}o}in baka na wancan lokaci na cike ne da hululu da zuga da kirari da kambama sarakuna). Haka kuma, ya yi tsokaci a kan hasashen da ake game da shigowar Musulunci }asar Hausa. Ya yi sharhi kan yanayin }asar Hausa a zamanin bayyanar Shehu da takin-sa}ar da ya ri}a samu da sarakunan Gobir (wato daga Bawa Jangwarzo har zuwa Yumfa), da tarihin jihadin da ya yi sanadiyyar]inkewar }asar Hausa ta zama daula]aya wato daular Usmaniyya.

Marubucin ya kawo ayyukan da masu jihadi suka yi a }o}arinsu na wayar da kan

jama’a da ilimantar da su game da addini, a nan ne ya karkata aikin nasa kan wa}o}insu wa]anda ya bayyana cewa sun taimaka gaya wajen ha~aka adabin Hausa kodayake su marubutan ba manufar su ke nan ba, manufar su ita ce ceto mutane daga ~atan da suke ciki. A }o}arinsa na nazarin wa}o}in nasu ne ya sa ya]auki babi guda (babi na hu]u) ya jero jigogin wa}o}in masu jihadi da yin cikakken sharhi kan kowane jigo tare da kawo misalai daga cikin wa}o}in nasu. [aya daga cikin fitaccen jigon da masu jihadi suka fi jadadawa shi ne jigon wa’azi. A }ar}ashin jigon wa’azi marubucin ya kawo ma’anar wa’azi da hanyoyin da masu jihadi suke bi wajen isar da sa}on wa’azi kamar hanyar bayyana mugayen al’adun jama’a da kira a guje masu inda ya kawo misalin wa}ar Garga]i ga jama’ar Musulmi da wa}ar Garga]i da Tsoratarwa duk na Shehu Usmanu da wa}ar Garga]i Sarkin Gobir Bawa ta Abdullahi Fodiyo. Sai kuma hanya ta biyu da ya bayyana da cewa ita ce ta sanya wa wa}a suna mai ban tsoro, ta kuma }unshi gaskiya mai]aci wanda da jin sunan kawai ya isa mutum ya razana, a nan ya kawo misalan wa}o}i kamar wa}ar Farin Mari ta Isan Kware da wa}ar Ba}in Mari ta Muhammad Tukur da wa}ar Jan Mari ta Salihu]an Zama da sauransu. Hanya ta uku da marubucin ya kawo ita ce ta furawa bayan an ciza wato a kwa]aitar da muminai game da ni’imomin Ubangiji bayan an yi tsoratarwa, a nan ma ya kawo misalign wa}ar bulaliya ta Abdullahi Fodiyo sai hanya ta hu]u da ya bayyana ta da cewa ita ce ta nuna wa jama’a }aratowar }arshen duniya da

tashin }iyama da kuma bayyanar sharu]]an }iyama, a nan ma ya kawo misalin wa}ar Munasaba ta Shehu da wa}ar Sharu]]an }iyama da sauransu.

Ba jigon wa'azi ka]ai marubucin ya nazarta ba, har ma da sauran jigogin masu jihadi kamar jigogin tarihi, bege da yabo, alhinin mutuwa, addini, tauhidi, salla, azumi, sufanci, tawassuli, karamomi, siyasa, hijira, jihadi, mulki, hul]a da jama'a, ilimin taurari, manziloli, darrari da kuma buruzzai. Haka kuma ya kawo tsari da salon rubutacciyar wa}ar Hausa. A juzu'i na biyu na aikin nasa ne ya kawo gundarin aikace-aikacen masu jihadi na Hausa inda ya fara da kawo aikace- aikacen Shehu [an fodiyo na Hausa da na Filatanci da Larabci da aka fassara, sai na Abdullahi Fodiyo (}anin Shehu) da na Muhammadu Bello da na Nana Asma'u da na Isan Kware da na Hassan da na Maryam ' da ('ya'yan Shehu) da na Khalilu (]an Abdullahi Fodiyo) da na Sa'idu [an Bello da sauransu da dama.

Shi ma Birniwa, (1981) ya yi nasa binciken ne domin neman shaidar digiri na biyu, ya yi wannan nazari ne a kan wa}o}in da suka shafi addini inda ya yi nazari kan Imfiraji ta]aya da ta hu]u. Da farko ya fara aikin nasa ne da kawo tarihin marubucin wa}ar wato Aliyu Namangi. Daga nan kuma sai ya yi tsokaci a kan wa}o}in a matsayinsu na wa}o}in madahu. Ya nazarci Imfiraji ta]aya tare da kawo ratayenta da kuma bayanin wasu kalmomi masu tsauri da ke cikin wa}ar. Haka kuma ya yi wa

wa}ar Imfiraji ta hu]u, har wa yau, aikin nasa bai tsaya nan ba, har ma sai da ya fassara wa]annan wa}o}i da ya yi nazari daga Hausa zuwa harshen Turanci.

Al}ali,(1982), a kundinsa na digirin farko ya yi nazari a kan wa}o}in malam Bello Gi]a]awa, inda ya kawo tarihin rayuwar mawa}in da cikakken sharhi kan wa}o}insa masu mabambantan jigogi kamar jigon Ilimi da wayar da kai, da jigon wa'azi da sauransu. A sharar fagen da marubucin ya yi a kan marubuta wa}o}i a }asar Hausa, ya jero]imbin marubuta wa}o}i na }arni na ashirin daga sassa daban daban na }asar Hausa amma bai ambaci mace ko]aya ba duk da cewa akwai shahararrun mata marubuta wa}o}i.

Ikara, (1983), a kundinsa na digirin farko, ya yi binciken a kan shahararren mawa}in nan ne, wato Ummaru Nasarawa Wazirin Gwandu da wa}o}insa. A sharar fagen da mai binciken ya yi, ya kawo jerin marubuta wa}o}in }arni na ashirin na sassa daban daban da ke fa]in }asar Hausa sai dai bai ambaci mace ko]aya ba duk da cewa akwai mata marubuta wa}o}i da dama a wannan }arni. Aikin nasa ya ta~o tarihirin rayuwar mawa}in (Ummaru Nasarawa Wazirin Gwandu) da neman iliminsa da yadda ya fara rubuta wa}o}i. Haka kuma ya nazarci jigon wa}o}insa (a cikin har da masu jigon wa'azi). Ya kuma nazarci zubi da tsari da salon sarrafa harshen wa}o}in

Tsoho, (1987), ya yi aiki a kundin digirinsa na biyu ne a kan wa}ar *Kanzil Azimi*

Aliyu Namangi, inda ya fara da kawo tarihin rayuwar mawa}in. Bayan wannan sai ya yi }o}arin zalu}o da jero duk wa}o}in Aliyu Namangi, wa]anda aka sani da wa]anda ba a sani ba, sa'annan ya yi matsakaicin sharhi a kansu ta hanyar tsara su cikin jadawali. Bayan haka ne aka yi kyakkyawan tarken wa}ar Kanzil Azim wadda wa}a ce mai tsawon gaske (baiti dubu biyu) kuma wa}a ce wadda ba a tattara ta wuri]aya ba, don haka wannan aiki ya taimaka wajen samun wa}ar a rubuce tare da adana ta don maganin salwantarsu.

Dunfawa, (1990), a bincikensa na neman digiri na biyu, ya gudanar da bincike kan gudummuwar masu]ari}a wajen ha~aka rubutattun wa}o}in Hausa. A binciken da ya gudanar, ya ta}aita aikin nasa ne a kan manyan]ariku guda biyu na }asar nan, wato]ari}ar Tijjaniyya da]ari}ar {adiriyya, inda ya fito da tarihin wa]annan]ariku a }asar Hausa, tare da cikakken sharhi a kan]imbin wa}o}in wa]annan]ariku ta hanyar nazarin jigonsu da tsarinsu da kuma tasirin wasu wa}o}in a kan masu]arika (kamar wa}o}in madahu) da sauransu.

Habibu, (2001) a kundinsa na digirin farko ya yi nazari ne a kan "Bun}asar Rubutattun Wa}o}in {arni na Ashirin," a cikin aikin nasa ya kawo jigogin wa}o}in }arni na ashirin wa]anda suka ha]a da jigon garga]i da na fa]akarwa da na soyyaya da na siyasa da jigon ilimantarwa da na yabo da na sha'awa da addini da sauransu. Har wa yau, aikin nasa ya yi bayani kan irin jigogin da ake samu a wa}o}in

addini wa]anda suka ha]a da jigon wa'azi da na madahu da na zuhudu da na ta'aziyya da fi}ihu da sauransu, aikin nasa bai tsaya nan ba domin ya kawo misalai daga wa}o}i daban daban domin kafa hujja. Daga cikin wa}o}in da ya kafa hujja da su a ~angaren wa}o}in addini akwai wa}ar Komawa ga Allah ta Lawal mai turare da wa}ar Yabon Annabi ta Shehu Al}alanci da sauransu.

2.4.2 Litattafai

Furniss, (1995), ya yi ta}aitaccen sharhi a kan aikace aikacen da aka yi musamman a kan wa}o}in jihadi da rubutattun wa}o}i na }arni na ashirin. A littafin nasa ya ta~o aikin Hiskett (1975) da aikin Muhammad (1979) da aikin Birniwa (1981) da Yakawada (1987) da dai sauransu, (wa]annan aikace aikacen duk an yi su a kan rubutattun wa}o}i ne). Ya kuma yi tsokaci a kan yadda wa}o}in jihadi suka faro kamar wa}ar *Ba}in Mari* ta Muhammad Tukur da Wa}ar *Ma'amare* ta Shehu Mujaddadi da dai sauransu. Har wa yau, bai tsaya nan ba, ya yi sharhi a kan wa}o}in wasu daga cikin mata marubuta kamar Nana Asma'u da Hauwa Gwaram da dai sauransu. Sai dai ba ya fito da aikin nasu ba ne a matsayinsu na mata marubuta ba, ya]ungume su ne a cikin marubuta wa}o}i ko dai na jihadi ko kuma na }arni na ashirin.

Junaidu, (2007), ya rubuta wani littafi mai suna *Tsarabar Waziri Buhari da Waziri Junaidu ga Manazarta wa}o}in Hausa.* Wannan littafi ya ta~o asali da tushen

rubutattun wa}o}in Hausa da kuma ma'anar ita kanta wa}ar da ta}aitaccen tarihin samuwar rubutattun wa}o}i a }asar Hausa. Bayan haka, littafin ya kawo ta}aitaccen tarihin Waziri Muhammadu Buhari da Waziri Junaidu da kuma tarihin rubuce-rubucensu da nasarorin da suka samu a rayuwa. Haka kuma, an yi sharhin wasu daga cikin wa}o}in marubutan, daga cikin wa}o}in waziri Muhammadu Buhari akwai wa}ar *Haba rai* da wa}ar *Jiya mini [an uwa* da wa}ar *Godiya ga Allah* da sauransu. Daga cikin na waziri Junaidu kuwa akwai wa}ar Ya rabbana agazan da wa}ar *Amincewa ma Allah, mai da al'amari garai* da sauransu. Wannan littafi na nuni da yadda zuriyar Shehu Usmanu suka ci gaba da rubuta wa}o}i musamman a kan jigogin addini tun daga }arni na sha tara zuwa wannnan lokaci da muke ciki.

2.4.3 Mu}alu

Hiskett, (1984) a aikin da ya gabatar kan Tsinkayar Hoton Haske a wa}o}in Begen Annabi, ya yi amfani da ayyukan I.Y Yahaya da A. Rufa'i, inda ya fito da wasu fitattun wa}o}i domin fito da bege a cikin wa}o}in,]aya daga cikin wa]annan wa}o}i ita ce wa}ar Nana As'ma'u mai suna *Qasida fi Madh Al-rasul* wadda ta }unshi tsantsar bege ga Ma'aiki (S.A.W), Haka kuma, ya ta~o wa}ar *Ma'amare* ta Shehu Usmanu da wa}ar *Muhammadu* ta Asim Degel (da sauransu) duk da nufin fito da jigon haske da ke tattare da begen Ma'aiki.

Aminu, (2005), ya gabatar da ma}alarsa mai taken "Reformism as a theme in Hausa

Religio-Political Poetry" ya yi bayanin yadda marubuta wa}o}in tajdidi suka du}afa rubuta wa}o}i domin ganin an jaddada addini tare da tabbatar da tsarin mulkin musulunci wanda suka nuna cewa shi ka]ai ne ya fi dacewa da al'ummar Musulmi. Da ga cikin mawa}an da marubucin ya za~i wa}o}insu don yin sharhi sun ha]a da Abdulmumini Abubakar Bauchi da Aliyu Rabi'u Kurna da Bashir [an]ago da Musa Kano da kuma Ibrahim Musa Gwagwarwa. Har wa yau, marubucin ya ta~o muhimman sa}onnin da ke cikin wa}o}insu kamar jaddada muhimmancin neman ilimi da kira ga musulmi ta su ha]a kai su kawar da mulkin zalunci da kuma kira ga gyaran halin al'ummar Musulmi, sai dai fitaccen jigon wa}o}in nasu shi ne siyasa, domin marubuta wa}o}in sun yi koyi da salon marubuta wa}o}in }arni na sha tara ne wajen kira ga kawar da gwamnatin kafirci da kuma kira ga bijire wa 'yan shi'a wadda suka bayyana ta a matsayin ~ata babba.

Aminu, (2005) bai gajiya ba wajen nazarin rubutattun wa}o}i musamman wa]anda suka kira ga shugabanci irin na Musulunci, domin a wannan karon ma nazari ya yi a kan irin gudummawar da marubuta wa}o}in Hausa suka bayar wajen tabka muhawarar tabbatar da shari'ar musulunci a Nijeriya. Marubucin ya yi wannan sharhi ne ta hanyar nazari da sharhin wa}ar "'Yan Nijeriya Mu bi addinin Allah ya gyara }asata" ta Ahmad Muhammad {araye wanda mamba ne a }ungiyar fafutukar tabbatar da shari'a mai suna JTI. Daga cikin abin da marubucin ya yi tsokaci a kansu

a cikin wannan ma}ala akwai tarihin kafuwar daular Usmaniyya wadda ita ce ta fara aza harsashin shari'ar Musulunci a }asar Hausa, sai kuma ya yi bayanin matsayin shari'ar Musulunci bayan zuwan Turawan mulkin mallaka da dalilan da suka hana]orewar shari'ar Musulunci a Nijeriya da kuma yadda mutane suka ri}a fafutukar ganin an tabbatar da shari'a a zamanin mulkin Demokra]iyya na 1999. Haka kuma, daga cikin abubuwan da marubucin ya tsakuro daga wa}ar akwai kwa]aitar da Musulmi da mawa}in ya yi game da falalar shari'ar Musulunci da kuma nuna cewa shari'ar Musulunci ta Musulmai ce kawai.

Wa]annan mu}alu da }asidu na da ala}a ta }ut- da -}ut da wannan aiki domin mafi yawancinsu sun shafi rubutattun wa}o}in addinin musulunci ne a }asar Hausa, inda aikin ya yi hannun riga da su shi ne a nan za a nazarci fannin rubutattun wa}o}in mata na wa'azi ne a }arni na ashirin.

Mukhtar, (2006), ya yi bayanin yadda rubutattun wa}o}i suka adana siyasar Nijeriya, a cikin mu}alarsa mai suna. Aikin nasa ya yi nazarin wa}o}in siyasa tun daga }arni na sha tara inda aka kawo misalan wa}o}i irinsu wa}ar "Murnar Nasarar Ya}i" ta Nana Asma'u da wa}ar "Murnar cin birnin Al}alawa" ta Abdullahi Fodiyo da wa}ar "Zuwan Annasara" ta Attahirun Ahmadu, marubucin ya nuna cewa wa]annan wa}o}i sun }unshi tsarin siyasa irin ta Musulunci.

Haka kuma, ya kawo asali da tarihin ginuwar wa}o}in siyasa na zamani (bayan

mulkin mallaka) tare da sharhi kan wa}o}in siyasar da aka samu a wannan zamani irinsu wa}ar “Maraba da ‘Yanci” ta Na’ibi Suleiman wali da “Arewa Jumhuriya ko Mulukiya” ta Sa’adu Zungur da “Arewa Jumhuriya Kawai” ta Mudi Sipikin da sauransu. Har wa yau, takardar ta yi cikakken sharhi kan tarihin kafuwar jam’iyyun siyasa a }asar nan. A ta}aice dai wa}arta fito da siyasar jiya da yau ta hanyar nazarin rubutattun wa}o}in Hausa. Kuma sanin kowa ne cewa siyasa na]aya daga cikin al’amurra na addini, hasali ma kalmar siyasar Balarabiyar kalma ce. Domin haka ne ma aka sami nasaba tsakanin wannan mu}ala da wannan aiki, da]in da]awa kuma marubucin ya ta~o wa}o}in mata domin ya kawo misalai daga wa}ar Nana Asma’u.

2.5 Ayyukan Da Aka yi kan Wa}o}in Kyautata Tarbiyya da Gyaran Al’umma.

A nan an sami kundaye da aka rubuta a kan nazarin wa}o}in da suka shafi kyautata tarbiyya da gyaran halin al’umma. Wa]annan ayyuka sun ha]a da aikin Dunfawa, (2002) da Muhammad da Ahmad (1996) da kuma Muhammad (2006).

2.5.1 Kundaye

Dunfawa, (2002) a kundinsa na digiri na uku ya yi bincike a kan matsayin “wa}a a tunanin yara” inda a aikin nasa ya yi kyakkyawan nazari kan }wa}walwar yara da yadda take kar~ar wa}a da kuma yadda take tace ta domin turawa ga hankalin yara don amfaninsu. Haka kuma, marubucin ya ta~o matsayin yara a cikin al’umma da

kuma nazarin tarihin samuwar wa}o}in yara a }asar Hausa wato wa}o}in baka da rubutattu. Bayan haka, an kawo yadda ake shirya wa}o}in yara da kuma fitattun jigogin wa}o}in yaran kamar jigon tarbiyya da na ilmantarwa da na samar da nisha]i da garga]i da sauransu. Ba a nan wannan aiki ya tsaya ba har ma sai da ya kawo tsarin da salon wa}o}in yara tare da kwatanta wa}o}in yara na baka da rubutattu don gano wa]anda yara suka fi fahimta, kuma an kwatanta tsarin wa}ar baka da rubutacciya. A }arshe marubucin ya yi ratayen wa}o}in baka na yara da rubutattu, wa]anda suke shiryawa da kansu da wa]anda ake rubutawa dominsu. Wannan aiki na da dangantaka ta kusa da wa}o}in wa'azi saboda ya }unshi wa}o}in tarbiyya da ilmantarwa da kuma garga]i/fa]akarwa.

Muhammad da Ahmad (1996), a kundin ha]in gwiwa na digirin farko, sun yi aikin ha]in gwiwa ne a kan gudummawar marubuta wa}o}in Hausa wajen kyautata tarbiyyar mazauna birane (musamman na Kano da Kaduna). A binciken nasu sun fito da irin gudummawar da marubuta wa}o}i ke bayarwa wajen kyautata tarbiyyar mazauna birane, daga cikin wa}o}in da suka nazarta akwai wa}ar *Sangartaciyya* ta Baba Maigya]a da wa}ar "Tarbiyyar 'yan Musulmi" ta Nasiru Garba Ahmed da wa}ar "Karuwa Motar Kowa" ta Mukhtar Ahmad Garba da wa}ar "{waya da 'yan {waya" ta Nasiru Garba Ahmad da wa}ar "Mashaya Giya" ta Garba Likoro da wa}ar "Dogaro da Kai" ta Muhammad Gwale da wa}ar "Zaman duniya" ta Abubakar Ladan Zariya

da sauransu. Haka kuma, manazartan sun nazarci jigo da tsari da salon wa]annan wa}o}in.

Muhammad, (2006), ya yi nazari ne a kan “wa}a a matsayin makami na canza]abi’un al’umma” inda ya yi bayanin yadda ake amfani da wa}a ta baka da rubutatta wajen canza]abi’un al’umma musamman kan abin da ya shafi auren dole da sa sutura ta kirki da fa]akarwa da ilmantarwa a kan muhimmancin ilimin zamani da harkar }idaya da sauransu. Daga cikin misalan wa}o}in da ya kafa hujja da su a rubutattun wa}o}i akwai wa}ar *Tabban Ha}i}an* ta Shehu Usmanu da wa}ar *{idaya* ta Hauwa Gwaram da wa}ar *Ilimi* ta Mu’azu Ha]eja da sauransu.

2.6 Ayyukan Da Suka Shafi Nazarin Adabin Mata (Musamman Rubutacciyar Wa}a).

Wannan bincike ya ci karo da ayyukan da aka gudanar a kan nazarin adabin mata musamman ma rubutacciyar wa}a. An sami wa]annan ayyuka ne wasu a matsayin kundayen bincike wasu kuma a matsayin litattafan da aka wallafa.

2.6.1 Kundaye

Gambo, (1986), a kundin digirinta na farko ta yi nazari ne kan sannaniyar marubuciyar rubutattun wa}o}in nan wato, Hajiya Hassana Ahmed Sufi, a inda ta yi nazari kan tarihinta da neman iliminta da ayyukanta wa]anda suka shafi rubutattun wa}o}i. Ta nazarci jigogin wa}o}in da tsarin wa}o}in da kuma salon sarrafa

harshensu.

Suleiman, (2004), a kundinsa na digirin farko ya gudanar da aikinsa ne a kan Rahanatu Usman da wa}o}inta. A binciken da ya yi, ya kawo tarihin mawa}iyar da sharhi a kan wa}o}inta masu mabambantan jigogi kamar jigon addini da jigon siyasa da jigon kiyon lafiya da dai sauransu.

Ita kuwa Balbasatu (2008), a kundin digirinta na uku, ta fito da irin gudummawar da mata ke bayarwa wajen bun}asar adabin Hausa, ta yi haka ne ta hanyar nazarin aikace aikacen mata a manyan sassan adabin Hausa, wato wa}a, zube da wasan kwaikwayo. Marubuciyar ta zayyano ayyukan da mata suka yi a wa]annan sassa na adabi.

A aikin Binta (2008), a kundin digirinta na farko ta gudanar da bincikenta a kan rubutattun wa}o}in mata inda ta za~i uku daga cikin mata marubuta wa}o}i(wa]anda suka ha]a da Hauwa Gwaram da Hajiya ‘yar shehu da Ru}ayyatu .S. Adakawa) ta nazarci jigogin wa}o}in nasu. Jigogin sun ha]a da ta’aziyya da jigon yabo da jigon ilimi da sauransu.

Maimuna (2008), a kundin digirinta na biyu ta yi nazari ne a kan rubutattun wa}o}in mata a Kano. Sharer fagen da ta yi a aikin, ta ta~o fitattun mata marubuta wa}o}i da irin ayyukan da suka yi. Irin wa]annan marubuta sun ha]a da Nana Asma’u da Maryam Fodiyo da Aisha Fodiyo da sauransu. Bayan haka, ta yi sharhi kan matsayin

mata dangane da ilimi da al'ada inda ta fito da ayyukan shahararrun mata marubuta wa}o}i na Kano kamar su Hajiya Hassana Sufi da Hajiya Ladi Soron-]inki da Hauwa Gwaram da dai sauransu. Har wa yau, marubuciyar ta yi nazarin yanayi da sigogin rubutattun wa}o}in. Wannan aiki nata ya shafi mata marubuta wa}o}i na Kano ne, sai dai ta kawo misalai daga wa}o}in mata marubuta na }arni na sha tara.

2.6.2 Litattafai

A nan an kawo ayyukan Mack da Boyd (1999) da wanda Mack (2000) ta yi. Sun yi magana ne a kan mata marubuta wa}o}in Hausa, sai dai inda muka raba gari da su shi ne ba su nazarci wa}o}in marubutan ta fuskar jigon wa'azi ba, duk kuwa da kawo misalan wasu daga cikin wa}o}in marubutan na wa'azi.

Mack da Boyd, (1999) sun yi kyakkyawan aiki kan shahararriyar malamar nan ta }arni na sha tara, wato Nana Asma'u]iyar Shehu Usmanu [an fodiyo. A littafin nasu, sun kawo cikakken tarihin Nana Asma'u da irin matsayinta a zamaninta. Har wa yau sun yi sharhi kan rawar da mata suka taka a yayin jihadin Shehu Mujaddadi. Sun ta~o matsayin mata (a Afirka) ta fuskar ilmi da ilmantar da al'umma. Aikin nasu bai tsaya nan ba, sun kawo]imbin aikace-aikacen Nana Asma'u (wa}o}in da ta rubuta cikin harshen fillanci da Hausa).

Mack da Boyd (2000), sun sake rubuta littafi kan Nana Asma'u mai suna *One Woman's Jihad; Nana Asma'u Scholar and Scribe.* inda suka kawo tarihin

marubuciyar tun daga tsattsonta har zuwa iyalanta (maigidanta da ‘ya’yanta). Sun bayyana irin aikace-aikacen da ta gudanar wa]anda suka shafi ilimin addini, kamar irin aikace-aikacen da ta gudanar wajen ilmantar da mata da kuma al’umma baki]aya. A wannan karon ma aikin nasu bai tsaya ga ba da tarihin wannan baiwar Allah ba, sai da suka kawo tarihin]aular Usmaniyya da matsayin]ari}ar {adiriyya a {ur’ani da Sunna da yadda Shehu Usmanu da iyalansa suka ri}i sufanci a zamaninsu. Har wa yau, sun bayyana yadda Nana Asma’u ta rubuta wa}o}i daban-daban kuma ta ri}a]aukar wasu daga cikin wa}o}in wa’azi tana tahamisinsu don ta taimaka wajen fa]akar da al’umma musamman a kan azabar lahira. Sun kawo misalin wa}ar Muhammad Tukur wadda ya sa wa suna ‘Tsoro’ wadda Nana ta]auka ta yi wa tahamisi (}arin]ango uku a saman kowane baiti) domin bayyana matsayin azabar lahira.

Mack, (2004) ta rubuta littafi mai suna *Muslim Women sing Hausa Popular Song* wannan littafi ya yi magana ne a kan wa}o}in matan Hausawa wa]anda suke yi a bukukuwansu (kamar bikin aure ko suna) da kuma wa}o}in da mata ke rubutawa don ba da gudummawarsu a ~angaren wa’azi. Marubuciyar ta]auki shahararrun mata mawa}a da marubuta wa]anda suka yi zamani a tsakanin 1966 zuwa1980. Daga cikin mata mawa}a da ta nazarta akwai Hajiya Barmani Choge da Binta Zabaya da Hauwa mai Duala da Hajiya Fati da Maizargadi, a cikin marubuta kuwa, marubuciyar ta nazarci ayyukan Hauwa Gwaram da Hajiya ‘Yar Shehu.

Har wa yau, marubuciyar ta bayyana cewa mata a arewacin Nijeriya ana shirya wa}o}i ne mafi yawa a kan jigogin da suka fi shafar su kamar matsayin mata a cikin al'umma da mata da Musulunci da jigon tarihi da siyasa da kula da lafiya da sauransu. Sai dai marubuciyar ba ta fito fili ta nuna cewa mata musamman marubuta na rubuta wa}o}i ne da niyyar wa'azi da fa]akar da al'umma a kan abin da ya shafi addini, duk kuwa da irin misalan wa}o}in da ta kawo masu nuna hakan, kamar wa}ar 'Wa'azi' ta Hajiya 'Yar Shehu da wa}ar 'Garga]i ga masu shan }waya' da sauransu.

Hauwa (2006), ta fito da wani littafi da ta kira: *Gender and Citizenship, Hausa Women's Political Identity from the Caliphate to the Protectorate.* A cikin wannan littafin nata ta ta~o matsayin mata a }asar Hausa daga }arshen }arni na sha tara zuwa }arni na ashirin da]aya, haka kuma ta ta~o matsayin da tsarin mulkin }asa ya ba mata musamman a dokar farko ta'yancin zama]an }asa ta Nijeriya. Har wa yau, ta nuna yadda mulkin mallaka ya yi tasiri a rayuwar matan Hausa, ta kuma yi bayanin matsalolin da ke wa mata tarna}i wajen hana su shiga a fafata da su a harkokin siyasa tun a }arni na sha tara zuwa }arni na ashirin. Daga cikin wa]annan matsaloli da ta zayyano akwai tasirin addinin Musulunci wanda bai ba mata cikakkiyar damar shugabanci ba, ta nuna cewa wannan ne ma ya sa ba a sami mace ko da guda ba a cikin shugabannin da suka yi jagoranci a zamanin Shehu Usmanu. Ta nuna cewa Shehu ya yi kira ga mata da su dage wajen neman ilmi da harkar kasuwanci amma

bai }arfafa masu yin shugabanci ba. Har wa yau, ta bayyana cewa dama tun fil a zal al'adun da Hausawa ba su tanadar wa mata yin shugabanci ba, don haka aka bar mata a baya wajen shiga a dama da su a harkokin siyasa.

Marubuciyar ta kawo irin rawar da mata suka taka a lokacin jihadin Shehu [anfodiyo inda ta bayyana ficen da Nana Asma'u ta yi wajen bayar da gudunmuwar kula da lafiyar wa]anda suka sami rauni a fagen ya}i da kuma kula da kayayyakin ya}i da abinci da sauransu. Sai dai ba ta fito da irin aikace-aikacen (rubuce-rubuce) da Nana Asma'u ta yi ba musamman ta ~angaren wa'azi da ilmantar da al'umma.

Mu}alu

A mu}alar da Mack, (1985), ta rubuta mai suna "Hausa Women Poets: Ghost Writer's." ta kawo hirar da ta yi da mata marubuta wa}o}in Hausa inda suka tattauna game da abin da ya shafi wa}a da rubuta wa}a. Ta yi wannan hira ne da shahararrun marubutan nan na }arni na ashirin wato Hajiya 'Yar Shehu da Hauwa Gwaram. Mack ta tambayi wa]annan bayin Allah ma'anar wa}a da bambancin wa}ar baka da rubutatta da kuma bambancin marubuta da mawa}a, inda dukkanin su suka shaida mata cewa akwai bambanci tsakanin mawa}a da marubuta, domin mafi yawan mawa}a maro}a ne yayin da mafi yawan marubuta ba suna rubuta wa}a ba ne domin neman ku]i, sai dai domin ilmantar da jama'a. Haka kuma, sun shaida mata cewa yawanci akan gaji wa}ar baka ne (ko ro}o) amma rubuta wa}a baiwa ce da ba a

gadonta. Da ta tambaye su game da dalilan da suka sa marubuta maza suka yi wa marubuta mata zarra ta fuskar rubuta wa}a kuwa, sai Hauwa Gwaram ta shaida mata cewa dalilan da suka hana mata yin fice a fagen rubuta wa}a bay a rasa nasaba da al'ada da kuma addini. Mata ba su da 'yancin da namiji ke da shi na gwagwarmaya da sanar da al'umma abin da yake aiwatarwa, amma ba wai domin matan bas u da fasaha ba ne. Mack ta }ar}are wannan hira ne da tambayarsu hanyoyin da suke bi wajen isar da sa}onninsu da ke }unshe a wa}o}insu, inda Hauwa Gwaram ta ba ta amsa da cewa sukan yi amfani da irin wa]annan wa}o}i ne wajen koyar da mata musamman a ajin ya}i da jahilci.

Har wa yau, Mack, (1986) ta }ara rubuta wata mu}ala mai suna " Songs From Silence: Hausa Women's Poetry" inda ta yi bayanin dalilan da suka sa a yau al'umma ba su cika]aukar mata a matsayin marubuta wa}o}i ba, saboda halin da matan suka shiga na kulle tun bayan jihadi (}arni na ashirin), domin mata ba su da dammar fitowa su bayyana irin fasaharsu musamman ta fuskar wa}a. Haka kuma, ta bayyana cewa mata sun fukanci }arancin ilimin rubuta wa}a. Sai dai ta bayyana cewa duk da haka, an sami 'yan }alilan da kan rubuta wa}o}i musamman a kan halin da suke ciki, da kan abubuwan da ke damun al'umma baki]aya.

Neil, (1988) ta rubuta wata mu}ala mai suna "Changing Female Role in Northern Nigeria: A Study of Women's Oral and Written Poetry." Ta nazarci gudummawar mata

mawa}a da marubuta wa}o}in Hausa wajen bun}asa rayuwar al'umma. A cikin wannan mu}alar ta kawo ma'anar wa}a da bambancin da ke tsakanin wa}ar baka da rubutacciya. Ta kuma yi tsokaci a kan yadda Nana Asma'u da Hauwa Gwaram suka yi amfani da wa}a wajen ilmantar da al'umma. Haka kuma, ta kamanta ayyukan Hauwa Gwaram na koyar da mata ya}i da jahilci ta amfani da wa}a kamar yadda Nana Asma'u ta yi amfani da wa}a ta koyar da mata (musamman 'yan taru) yadda za su gudanar da ibada, da kuma yadda za su isar da wannan sa}o ga sauran mata ta amfani da wa}a.

Har wa yau, marubuciyar ta waiwayi mata mawa}a irinsu Maimuna Barmani coge da Binta Zabaya inda ta bayyana }o}arinsu na nisha]antar da jama'a ta hanyar wa}o}insu da kuma }ara wa mata }warin gwiwar neman ilimi da shiga a dama da su a sauran fannoni na rayuwa.

2.7 Na]ewa

Wannan babi ya tarraro ayyuka da suke da ala}a ta kusa ko ta nesa da wannan aiki. Daga cikin ayyukan da aka kawo akwai bayanin masana dangane da ma'anar wa'azi

da tarihin samuwar rubutattun wa}o}in wa'azi a }asar Hausa. Har wa yau, an yi bitar ayyukan da aka rubuta kan nazarin jigon wa'azi a rubutattun wa}o}i sai dai marubutan sun tsaya ne ga nazarin wa}o}in marubutan }arni na goma sha tara. Haka kuma, aikin ya binciko ayyukan da aka nazarci jigogin wa}o}in addinin musulunci. Har wa yau, babin ya kawo nazarce- nazarce da aka gudanar a kan rubutattun wa}o}in mata amma ba a yi katarin samun wanda ya nazarci jigon wa'azi a wa}o}in mata ba musamman ma marubutan }arni na ashirin.

Wannan nazari da aikin ya gudanar ya }ara tabbatar da cewa akwai bu}atar gudanar da wannan bincike kenan, kuma wannan ya sa an sami haske a kan yadda ya kamata a shirya gudanar da wannan bincike domin Hausawa kan ce "Daga na gaba akan ga zurfin ruwa."

BABI NA UKU: Jigogin Wa}o}in Mata na Wa'azi a {arni na Ashirin

3.0 Shimfi]a

Wannan babi ya }unshi sharhi ne a kan jigogin wa}o}in mata na }arni na ashirin. Da

farko an fara da kawo ma’anar jigo daga wajen masana daban daban, sa’annan aka kawo ma’anar jigo a rubutattun wa}o}i. Har ila yau, babin ya }unshi nazari da sharhi kan jigogi ko sa}onnin da mata suka fi isarwa a wa}o}insu wanda ya ha]a da fa]akarwa kan muhimmancin neman ilimi da fa]akarwa kan muhimmancin ri}on amana da garga]i kan rayuwar yau da kullum (juyin zamani) da fa]akarwa ga mata a kan lullu~i da uwa-uba fa]akarwa kan kishi. An fito da wa]annan jigogi ne ta hanyar kafa hujja da wa}o}in mata na }arni na ashirin.

3.1 Ma’anar Jigo

Kalmar jigo kalma ce mai bakandamiyar ma’ana a Hausa, kamar yadda Bargery, (1934) da Muhammad (2001) da {amusun Hausa (2006) [angambo (2007) da Bunza (2009) suka bayyana.

A fassarar da Bargery (1934) ya yi wa kalmar jigo, ya bayyana ta da cewa kalmar za ta iya]aukar ma’anar abin rataye kaya ko ma’anar shugaba ko kuma turke.

Shi kuwa Muhammad (2001) cewa ya yi jigo na nufin gangariyar muhimmin sa}o ko manufar mawa}i. Ra’ayin Muhammad (2001) ya so ya yi daidai da na [angambo (2007) domin shi ma fassara jigo ya yi a matsayin sa}o, manufa ko abin da wa}a ta }unsa, wato abin da take magana a kai.

Yayin da Muhammad (2001) da [angambo (2007) suka kalli ma’anar jigo ta fuskar nazarin wa}a, shi kuwa {amusun Hausa (2007) tattaro ma’anonin wannan kalma ya yi

kamar haka: jigo na nufin itatuwan da ake kafawa su tallafi gugar ban ruwa, haka kuma, jigo na nufin shugaba ko shisshike ko turke ko kuma sa}o na musamman da marubuci ke }o}arin bayyana wa jama'a a }agaggen labari ko wasan kwaikwayo ko kuma a wa}a.

Bunza (2009) shi ma bin diddi}in kalmar ya yi ta hanyar kawo ma'anoni daban daban kamar haka:

> Kalmar jigo ta samo asali ne daga sunan wani abu na ban ruwa a lambu wanda ake amfani da shi wajen]ebo ruwa a rijiya ko rafi don zuba wa kuyyar shuka, daga nan kalmar ta ci gaba da riki]a ta ba da ma'anar shugaba ko jagora ga wani abu na musamman ko manufar wani abu ko ginshi}in abu wanda idan babu shi ba zai tsaya da }afafunsa ba.

A ta}aice dai jigo a fannin adabi na nufin gundarin sa}on da ake son isarwa ga jama'a a magance ko a rubuce. Duk wani abin da mutum ya }ir}ira a matsayin adabi wannan abu na da manufar }ir}irarsa, manufar na iya zamantowa ilmantarwa ko fa]akarwa ko nisha]antarwa ko wayar da kai, wannan manufa ita ake kira jigo.

3.1.1 Jigo a Rubutattun Wa}o}in Hausa

Marubuta wa}o}i na amfani da wa}a a matsayin kafar isar da sa}onni daban daban, hasali ma da wannan kafa ce marubuta wa}o}in }arni na sha tara suka yi amfani

wajen cimma manufarsu ta ya]a addini, wadda ta kai su ga sauya tunanin al'umma musamman domin tunkarar }alubalensu na kafa daular addinin Musulunci. Wannan dalili ne ya yi sanadin yin jihadin da ya jaddada addinin Musulunci a }asar Hausa.

Wannan ya nuna cewa kafar adabi kafa ce da za a iya amfani da ita wajen ya}i cikin ruwan sanyi, kuma har a yi nasara a ya}in fiye da yadda za a yi nasara in an yi ya}i da kansakali, domin Sa'adu Zungur ya bayyana wannan kafa (wa}a/adabi) da cewa:

> Harshe shi ne kansakali
> Mashi kuwa al}alami na gari (wa}ar 'Yanci).

3.2 Jigogin Wa}o}in Mata na Wa'azi a {arni na Ashirin

Mata sun yi koyi da mutanen }warai, domin suna daga cikin jinsin mutanen da suka za~i isar da sa}onninsu ta hanyar rubuta wa}a. Daga cikin sa}onnin da mata suka isar ta fuskar rubutattun wa}o}i akwai sa}o ko jigon wa'azi wanda fitaccen jigo ne a rubutattun wa}o}in Hausa, sai dai shi kansa wa'azin yana tattare da wasu jigogi na musamman wa]anda suka ha]a da jigon ilmantarwa da jigon tsoratarwa game da lahira da jigon horo da hani (wato horo ga aikata kyawawan aiki kamar ri}on amana da shiga ta }warai ga mata; lullu~i) sai kuma hani ga munanan ayyuka kamar kishi da karya da zama cikin jahilci da sauransu. Jigo na farko da wannan babi zai yi tsokaci a kai shi ne jigon ilimi:

3.2.1 Ilimi

Wannan kalma ta ilimi ta samo asali ne daga Balarabiyar kalmar nan ta *ilmu* wadda ke

nufin ‘sani’ sai Bahaushe ya yi mata ‘yar kwaskwarima ya mayar da ita ta zamo ‘ilimi’. Ilimi muhimmin abu ne a rayuwar]an Adam domin shi ne abin da yake tabbatar da mutumtakar mutum kuma da shi ne Allah (s.w) ya fifita]an Adam a kan sauran bayinsa.

Bahaushe mutum ne mai martaba ilimi tun a da har zuwa yanzu. Za mu iya tabbatar da matsayin ilimi a wajen Bahaushe ta hanyar la’akari da karin maganar Hausa wadda ke fayyace tunani da fasahar al’ummar Hausawa. Daga cikin karin maganar da suka fito da matsayin ilimi a wurin Bahaushe sun ha]a da:

“ilimi gishirin zaman duniya”

Wannan karin magana na nuna cewa rayuwa ba ilimi tamkar miya ce ba gishiri wadda ba mai iya shanta sai wanda ta zame wa dole.

Haka kuma, wani abin burgewa ga ilimi shi ne ba a gadonsa ko satarsa ko }watarsa da }arfin tsiya, kullun yana nan tare da mai shi. Hausawa sukan }ara da cewa:

“Ilimi, farkonka ma]aci, }arshenka zuma”

Da]in ilimi ga mai shi ya fi zuma domin ilimi kan magance babbar cutar da zuma ba ta magancewa wato jahilci. Domin haka, Bahaushe mutum ne mai }o}arin neman ilimi da horo ga neman ilimi, saboda Hausawa kan ce

“{aramin sani }u}umi ne”.

Jigon ilimi fitaccen jigo ne a rubutattun wa}o}in Hausa domin marubuta da dama sun

yi amfani da jigon ilimi a wa}o}insu, kamar a wa}ar “Tabban Ha}i}an” ta Shehu Usmanu ya yi horo da a nemi ilimi, haka shima Aliyu Namangi ya bayyana muhimmancin neman ilimi a wa}arsa ta “Imfiraji.*”* shi ma malam Bello Gi]a]awa Sokoto ba a bar shi a baya ba domin ya yi wa}a sukutum kan ilimi wadda ya kira da “Darajjar Ilimi” haka kuma shahararren fasihin nan wato A}ilu Aliyu, shi ma ya yi fitattun wa}o}i a kan ilimi wa]anda suna]aya daga cikin wa}o}in da suka sa ya yi fice a sahun marubuta wa}o}in Hausa, wa]annan wa}o}i kuwa su ne wa}ar “{alubale da wa}ar “Kadaura Babbar Inuwa.”

Wannan dalili ne ya sa wasu daga cikin mata suka ga akwai bu}atar su ma su bayar da gudummawarsu wajen kira ga jama’a maza da mata da su tashi tsaye su nemi ilimi. Daga cikin wa}o}in da aka samu wa]anda ke]auke da jigon ilimi sun ha]a da wa}ar “Ilimi” ta Hassana Sufi da wa}ar “Rashin Ilimi” ta Raihanatu Usman da wa}ar “Ilimi” ta Ladi Soron]inki da wa}ar “Ilimi*” ga]iya* mace ta Zuwaira Isah da wa}ar “Ilimi” ta Shema’u Abdullahi da sauransu. A nan za a]auki wa}ar “Ilimi” ta Hassana Sufi da wa}ar *“*Ilimi” ta Shema’u Abdullahi domin fito da jigon ilimi a wa}o}insu, an kuwa yi haka ne domin ta}aitawa da samun damar nazarin sauran jigogin wa}o}in wa’azi na mata.

Wa]annan marubuta wato Hassana Ahmed Sufi da Shema’u Abdullahi sun fito da jigon ilimi ne a wa}o}insu ta hanyar nuna muhimmancin ilimi ga]an adam tare da

wajibcin nemansa ga kowane mutum. Da farko sun fara ne da kira ga jama'a a kan su tashi su nemi ilimi domin samun ingancin rayuwa, sai dai sun shawarci masu neman ilimi da su fara gabatar da neman ilimin addini kafin sauran nau'oin ilimi na zaman duniya, domin shi ne za ya zame masu babban ginshigi ko turken da za su kafa sauran ilimin da za su nema.

Hassana Sufi ta bayyana cewa

5 Ilimi iri biyu ne tamkar da kuka sani,
Ilimi na Addini da na zamani Ilimu.

6 To zan yi zance a kan ilimi na Addini,
Shi ne abin a gabatar mai bi]ar Ilmu.

Ita kuwa Shema'u Abdullahi cewa ta yi

24 Ilimi ko yana fa da fannoni,
Wanda ba shi iyaka al'ilmi.

12 Ilimi fa na tsoron Arrabbu,
Shi ne manufa fa a gun ilimi.

Mawa}an sun bayyana cewa wannan kira da suke yana da asali domin horo ne na Manzon tsira Annabi Muhammadu (S.A.W), domin ya bayyana a cikin hadisi cewa neman ilimi farilla ne ga kowane musulmi namiji da musulma mace. wato ba a]auke wa kowa wajibcin nemansa ba, matu}ar dai mutum na raye kuma yana da hankali. Hassana Sufi ta bayyana cewa:

8 Manzonmu mai daraja ya ce mu nem Ilimi,
Ko da a birni na Sinu mu je mu nem Ilmu.

9 Ya ce farilla Musulmi duk ya nem Ilimi,
Dukkan Musulma farilla ne ta nem Ilmu

A ~angaren Shema'u Abdullahi kuwa, ta nuna wajibcin neman ilimi kamar haka:

22 Har ma fa Rasulu ya wo nuni,
Kowa fa ya tashi ya san ilimi.

23 Farilla ce ita kan namiji,
Har ma mace je ki bi]o ilimi.

Mawa}an sun ci gaba da warware jigon ilimi ta hanyar bayyana muhimmancinsa ga jama'a kamar yadda Hassana Sufi ta bayyana:

10 Ai ilimi zuma ne haka malamai suka ce,
Ilimi ado ne a ya jama'a mu nem ilmu.

11 Ilimi da shi muka san Allah fa ya jama'a
Da Annabawa Ma'aika masu son ilmu.

Wato a nan Hassana Sufi ta bayyana cewa ilimi abin ado ne ga mai shi, domin matu}ar kana da ilimi to za ka zama mutum mai }ima da daraja a idon jama'a. Hasali ma ado da ilimi ya fi ado da zinari da lu'u- lu'u ga jahili. Kuma ta bayyana cewa dole sai da ilimi za a bauta wa Ubangiji ma]aukakin sarki domin Allah da kansa cewa ya yi "Ka san ni kafin ka bauta mini, domin in ba ka san ni ba yaya za a yi ka bauta mani." (Hadisil {udusi).

Hassana Sufi ta ci gaba da bayyana muhimmancin neman ilimi wajen kyautata ibada

kamar haka:

12 Ilimi da shi ake sanin faralu da masaminu,
Da mustahabu da makaruhu da maharumu.

13 In babu ilimi da mai aka bauta Allahu,
Ba ka san ibada ba, gafilu je ka nem ilmu.

14 Sallah Alwala da wanka ya ake yin su,
Ba za ka san yin su ba sai ka bi]o ilmu.

Ha}i}a wa'azi a kan kyautata ibada na]aya daga cikin manufar marubuta wa}o}in Hausa, kyautata ibada kuwa ba ta yiwuwa sai da ilimi, domin haka ma Shema'u Abdullahi ta bi bayan Hassana Sufi wajen bayyana muhimmancin ilimi musamman a fannin ibada kamar haka:

25 Ilimi da yawa ya ruwan kogi
Yo nin}aya a cikin ilimi.

26 Fanni na furu'a kan farko,
Shi ne na ibada uwar ilimi.

27 Sallah, azumi har ma zakka,
Har Hajji ka je ka cikin ilimi.

28 Shi tauhidi ba ya samo
Sai an bi tafarkin yin ilimi.

29 Don ita bautar Allah ku sani,
Ba a yi sai fa a kan ilimi.

30 Ba a kwaikwayo da yin bauta
Sai an yi bi]an neman ilimi.
31 Farilla, sunna mun sansu

Da mustahabi a cikin ilimi.

32 Makaruhi ba a sani shi ma
Bare fa haram sai an ilimi.

Haka dai Shema'u Abdullahi ta ci gaba da zayyano muhimman sassa na ibada da ke bu}atar neman ilimi domin saninsu, kamar sanin al}ur'ani da Hadisi da sauransu. Kamar yadda mawa}an suka yi tarayya wajen bayyana muhimmancin neman ilimi musamman na addini wanda zai taimaka wajen sanin addini haka ma suka yi tarayya wajen nuna fifikon ilimi da mai ilimin a kan sauran abubuwa. Hassana Sufi ta bayyana fifikon da mai ilimi ke da shi kamar haka:

15 Da sani fa Adamu babanmu ya]aukaka ai,
A kan Mala'ikatu jama'a mu nem Ilmu.

16 Allah ya ce su yi sujudi gare shi dukansu
Suka yi ta sai Ibilisu uban ma}i Ilmu.

Yayin da Hassana Sufi ke bayyana fifikon da Allah ya yi wa 'yan Adam a kan sauran halittu ta hanyar ba mu ilimi, ita kuwa Shema'u Abdullahi ta nuna cewa in dai har fifiko kake so a cikin al'umma to fa sai ka yi ilimi, domin duk matsayin da mutum ya kai ba zai yi daraja ba ko ya ce ya fi wani sai fa wanda ya yi ilimi kuma ya yi aiki da shi. Ga abin da take cewa:

6 Ba mai iya cewa ya fi ka,
In har fa ka tashi ka san ilimi.

7 In ka so ka hau kan mai gaba
Taso maza jeka kawo ilimi.

8 In ka yi ku]inka ya {aruna
Ba ka daraja sai kai ilimi.

9 In ka yi sarautar]an Dauda
Sulaiman tashi bi]o ilimi.

10 Ko kai kyawun]an Ya'a}uba
Shi Yusufu, jeka bi]o ilimi.

11 Shi ko ilimin]an Bal'ama,
Shi ba shi da }ima sai zulmi.

A wa]annan baituka da suka gabata, mawa}iyar ta nuna cewa mutum bai kaiwa }ololuwar daraja sai da ilimi, domin in ta}amarsa dukiya ko sarauta ko kyawu matu}ar ba ya da ilimi to sun zama na banza. Haka kuma ta nuna cewa ba wai yin ilimin ka]ai ke kai mutum ga daraja da samun tsira ba, a'a har ma sai ya yi aiki da shi, domin tarin ilimi ba aiki da shi ta yadda Allah ya umurta to lalle ya zama irin ilimin ta}adarin bawa, wato Bil'ama (]an Ba'ura) wanda ya yi i}irarin rubuta nasa }ur'anin wai a cewarsa shi ma ana saukar masa da wahayi.

Ita ma Hassana Sufi ta nuna aibun irin ilimin nan da ba ya da amfani, wato ilimin da aka yi shi ba domin Allah ba sai domin riya, ta kuwa bayyana haka ne a cikin wa]annan baitocin kamar haka:

28 Allah ka ba mu yawan ilmi da aiki da shi,
Ilimin da ba aikatawa ya zame zulmu.

29 Duk wanda ya nem sani domin a ce wane,
Aibunsa, ka ji yai riya mai bi]ar Ilmu.

30 Ita ko riya rushe aikin wanda yai ta take,
Mai hankali kar ka yarda, ka je ka nem ilmu.

31 Haka wanda ya nem sani domin ya san girma,
Koko ya san arziki kaitonsa mai Ilmu.

32 Ya ~ata iliminsa kan abu }an}ani kaito
Abin da ba zai da]e ba a gunsa ba daumu.

33 Kamar ya shafa farar }asa a]akinsa
Kuma sai ya hura haya}i ka ji mai Ilmu.

34 Iliminsa ya zan hujja a kansa ya jama'a,
A gobe ran lahira zai sha yawan nadamu.

Wannan bayani na wa]annan mawa}a na nuna cewa ba wai kawai suna kira a kan neman ilimi ba ne ka]ai, har ma da garga]i a kan yadda ya kamata a sarrafa ilimin da aka yi, ta hanyar amfani da shi a hanyar da ta dace, domin ka da ya zamanto abin nan da Sa'adu Zungur ya ce:

Iliminsu kamar rawaninsu yake
[aure-]auren banza ba nazari.

(Wa}ar 'Yanci)

Saboda tarin ilimi ba aiki da shi ya zama kaya ga mutum, domin sai an tuhume shi a ranar da ba ya da hujjar kare kansa.

Wa]annan mawa}a sun ci gaba da kira ga jama'a da su daure su tashi su nemi ilimi na addini da na zamani wanda zai taimaka wa rayuwarsu a nan duniya da gobe }iyama.

Hassana Sufi ta bayyana cewa:

36 Maza da mata mu tashi tsaye mu]au himma,
Manya da yara mu san burin mu san ilmu.

37 Ilimi yana kau da kuwa babu dai gefe,
Sai wanda bai samu yin sa ba duk mu nem ilmu.

Ita kuwa Shema'u Abdullahi cewa ta yi:

63 Zama a wuri]aya kar fa ka yi,
|ulla fa ka waye gun ilimi.

16 In ka so ka tashi ka je Chaina,
Domin ka bi]o shi a can ilimi.

34 Sana'a ma neman sa'a,
Ba a katari sai an ilimi.

35 Har ma ciniki da irin nashi,
Fannoni duk fa cikin ilimi.

A yayin da mawa}an suka mayar da hankali wajen kira da a dage a nemi ilimi saboda muhimmancinsa, Shema'u Abdullahi ta ci gaba da bayyana }ima da darajar ilimi kamar haka:

64 Darajanai ba ka iyakance,
A kan komai shi al'ilmi.

65 Shi ke gadinka bai rabuwa,
Shi haske ne kuma al'ilmi.

66 In ka]iba ka ga ya }aru,
Bai }arewa ga mazo ilimi.

67 Ba ka ije ilimi can a gida,

Da abinka kake yawo ilimi.

Haka dai mawa}iyar ta ci gaba da nuna }imar da ilimi, kamar yadda ta nuna cewa ba a satar sa kuma ba a gadon sa, yana nan tare da mai shi a kowane lokaci.

A yayin da Shema'u Abdullahi ta dage wajen bayyana }ima da darajar ilimi, ita kuwa Hassana Sufi bayyana ha}}in da ke kan iyaye na bai wa 'ya'yansu ilimi. Ta kuma garga]i iyaye a kan illar rashin ba 'ya'ya mata ilimi, wa]anda yawanci ake]ora wa talla maimakon a bar su su je su nemi ilimi. Ta yi wannan bayanin ne kamar haka:

38 'Ya'ya fa ha}}insu na nan kan iyayensu,
Su sa su hanyar karatu don su san Ilmu.

39 Amma yawancin mu ba a kula da 'yan yara,
Tun ba a ce mata ba, sai ta girma ba Ilmu.

40 Sai dai a ce "zo ki]au tallar, ki je ki yi man,
Mu san abin hidda kunya", ba batun ilmu.

41 "To in ba kiy talla ba, da me za a sayi,
Kayan da zan kai ki]aki," ka ji matanmu.

43 Ta gantale, ta lalace duk a kan titi,
Tallar da ba ta }ulla komai, sai yawan jurmu.

Haka dai Hassana Sufi ta ci gaba da warware wa}arta ta nuna aibun talla musamman ga 'ya'ya mata, tare da jawo hankalin iyaye musamman mata da su guji]ora

wa]iyansu mata talla, domin talla ba ta ta~a kawo masu wani arziki sai dai lalacewa kamar yadda ta nuna a wannan baitin:

44 Ba arziki muka samu ba a lalace
Don |abura babu girma ga rashin ilmu.

45 Ban ce neman halal yana da laifi ba,
Ina nufin duk abin da ake a nem Ilmu.

Tabbas rayuwa ba ta tafiya daidai sai da ilimi. Daga wa]annan wa}o}i biyu masu suna iri]aya wato wa}ar *"ilimi"* ta Hassana Sufi da wa}ar "Ilimi" ta Shema'u Abdullahi, mun ji yadda mata suka fito da jigon ilimi ta hanyar wa'azi a kan muhimmancin neman ilimi. Mun ji yadda mawa}an suka yi kira a kan neman ilimi ta hanyar nuna muhimmancinsa da fifikon mai ilimi a kan sauran mutane da }ima da darajar da ke cikin ilimi da kuma illar rashin kula da ilmin yara musamman mata, da sauransu.

3.2.2 Ri}on Amana

Ri}on amana na]aya daga cikin kyawawan]abi'u masu muhimmanci a cikin kowace al'umma ta duniya. Al'ummar Hausawa mutane ne da aka sani da gaskiya da ri}on amana. Hausawa suna matu}ar girmama amana tare da kare amanonin da aka dan}a masu, ta dukiya ce ko zance ko ta wani abu daban.

Wannan hali na al'ummar Hausawa ya sa suka yi fice wurin fatauci da sha'anin mulki a da, domin a da za ka ga an ha]a ayarin matafiya an za~i wani mutum mai gaskiya da

ri}on amana an na]a shi shugaban wannan ayarin (madugu) wanda shi ne ke da alhakin kula da dukiya da kuma jama'ar da ke tare da shi a wannan tafiyar, wani lokaci ma har maza kan bayar da amanar matansu ga madugu domin kai su garuruwansu ko inda suka yi bu}atar zuwa. Wannan ya nuna kenan tun kafin zuwan Musulunci Bahaushe mutum ne mai ri}on amana, kuma akan girmama masu gaskiya da ri}on amana.

Addinin Musulunci addini ne da ya yi horo a kan ri}on amana, hasali ma kyawawan]abi'u na sahun farko da Musulunci ya yi horon kowane Musulmi da aikatawa. Har wa yau, Manzonmu Manzon Allah Annabi Muhammad (S.A.W) mutum ne mai gaskiya da ri}on amana tun yana yaro. Wannan fice da ya yi da wannan hali ya sa Larabawa suka yi masa la}abi da Al'amin (Amintacce). Haka kuma, gaskiyarsa da ri}on amanarsa ne ya sa Sayyida Khadija ta amince da shi a kan kasuwancinta har ma ta nemi ya aure ta saboda ba ta ta~a ganin mutum mai gaskiya da ri}on amana irinsa ba.

Sanin muhimmancin ri}on amana ya sa wasu daga cikin mata mawa}a suka ga cewa akwai bu}atar su tunatar da jama'a domin su farga. Daga cikin matan da suka yi wannan }o}ari akwai Malama Raihanatu Usman da Amina Muhammadu Anda

Funtuwa wa]anda kowace daga cikinsu ta rubuta wa}arta kuma aka yi sa'a suka sa wa wa}o}in suna iri]aya wato wa}ar "Ri}on Amana".

Mawa}an sun fito da jigonsu na bayyana muhimmancin ri}on amana ta hanyar kira ga jama'a da su dage a kan ri}on amanonin da aka dan}a masu, Raihanatu Usman ta bayyana cewa:

4 Haka nan Khadijatu da Ai'sharmu,
Da Hafsa, Zainabu sun kira mu,
Mu kama hanya mui ta kanmu,
Mu daina zaluntar fa kanmu,
Amma fa sai mu ri}e amana.

Yayin da Rainatu ke danganta kiran da take da matan Manzo (S.A.W) ita kuwa Amina Anda cewa ta yi:

4 Mazanmu har da mata,
Ni ga ni zan kwatanta,
Domin mu zan fahimta,
Mu bar zaman ba}inta,
Mu rirri}e amana.

5 Mu tashi koda yaushe,
Mu zan hawa ya taushe,
Mu rirri}e shi reshe,
Ganye idan ya bushe,
{arshen ta cin amana.

6 ku zo mu kama hanya,
Cikinta babu jinya,
Amma akwai biyayya,
Duk sai ku zo mu juya,

A kan ri}on amana.

Amina Anda ta yi nasiha a kan yin biyayya ga horon Ubangiji na ri}on amana wanda wajibi ne ga kowa ya nemi ilimi domin sanin ita kanta amanar. A ci gaba kuma, Raihanatu Usman ta bayyana nau'o'in amanar da za a iya ba mutum wadda kuma in har an ba shi to ya zama wajibi a kansa ya ri}e ta da gaskiya, ga abin da take cewa kamar haka:

5 Ta dukiya ce ko mu}ami,
Wajen zama ne kar mu nemi,
Yardar mutane don mu sami,
Darajoji ko ko mu}ami,
Allahu ya hana cin amana.

6 Ko ta zance an yi sirri,
Mui }o}ari mu rufe asiri,
Dukkan mutane ban da sharri,
Mu zam muna neman fa khari,
Mui }o}arin tsare dai amana.

Bayan Raihanatu Usman ta yi bayanin nau'o'in amana da akan ba mutane wa]anda ya wajaba su ri}e hannu bibiyu, sai Amina Anda ta yi bayani kan mutanen da kan nemi mulki ko mu}ami, cewa su kula domin amanar al'umma za ta hau kansu, kuma in har suka kuskura suka kasa ri}ewa to za su yi ba}in cikin abin da suka jawo wa kansu. Kamar yadda take cewa:

11 Mai tattalin sarauta,
A kanka sai ta hurta,
Ganin ka za ka huta,
Ina ko za ka huta?
Sai ka ri}e amana.

12 To sai ku zo ku daina,
Cuta a kan amana,
In kun }iya ku daina,
{arshenta za ku zanna,
Da ba}in cikin amana.

Raihanatu Usman ta yi garga]i ga shuwagabanni a kan su kula da amanar al'ummar da suke mulki da kuma al}awurran da suka]aukar wa al'umma kamar yadda ta ce:

11 Shugabanni masu mulki,
Su zam fa lura a kan fa aiki,
Na yau da kullum su]au mataki,
Ri}on amana ku tsara aiki,
Kullun ku }arfafa dai amana.

12 Allahu shi ya aza ku mulki,
Ba ku da iko sai ku]auki,
Ri}on amana ku gyara aiki,
Kui taka-tsantsan a kan fa mulki,
Don kar ku zam maciya amana.

13 Al}awari da kuke ta]auka
Na ayyuka, to kar ku shuka-
Mugun tunani kar ku shuka,
Aiki marar kyau za ku kuka,
Da kanku domin cin amana.

Har wa yau, mawa}an sun tunatar da al'umma a kan ranar da za su tsaya gaban ubangijinsu wanda ya yi horo da ri}on amana, ranar da maciya amana za su shiga halin }a}a-nika yi. Ga abin da Raihanatu Usman take cewa:

Mu tuna fa za mu tsaya gabansa
Sarki Gwani don ba kamarsa,
A duniya haka lahirarsa,
Mutum aljan da mala'ikunsa,
Shi ne ya ce mu ri}e amana.

Ita kuwa Amina Anda cewa ta yi:

Wallahi duk mu koma
Ga jallah mu yi nadama,
Mu }ara ba da himma,
Sannan mu daina gaba,
Mu rirri}e amana.

Wa]annan baituka da mawa}an suka kawo nasiha ce ga masu cin amana inda suka nuna cewa suna da damar da za su yi nadama su tuba su koma ga Allah kafin ranar da za ta zo nadama da tuba ba za su yi amfani ba.

Malama Raihanatu Usman ta bugi jaki ta bugi taiki a wannan wa}a domin ba ga shugabanni kawai ta yi kira ba, har ma da talakawa da sauran jama'a maza da mata yara da manya. Ga abin da take cewa a wa]annan baitocin kamar haka:

Mu ma talakawa da namu,
Allahu ya]ora su kanmu,
Domin su zam gyaran halinmu,
Amma mukan no}e wuyanmu,
Dan kar mu]au kayan amana.

Wannan fa wa}a Bakandama ce,
Ta ha]a kowa ta kasance,
Don ba ta }yale masu }wace,
Da masu cin kayan matacce,
Har ma da masu cinyewar amana.

22 Sarki kake ko Hakimi ne,
Police kake ko Lebura ne,
Dafto kake ko malami ne,
Har ma direbobi ku gane,
Allahu ya hana cin amana.

23 Al}ali har Lauya ku gyara,
Soja da Police duk ku lura,
Aikinku na matu}ar lalura,
Ku yi hattara fa saboda nera,
Don kar ku zam maciya amana.

25 Da masu kanti har tireda,
Har ma ma'auna da masu sai da-
Kaya na]aki da yanka leda,
Har masu gyara da masu walda,
Allahu ya hana cin amana.

26 Har masu sai da abinci duka,
Da 'yan dako in kunka]auka,
Kayan mutane kar ku yanka,
Ku]in da ba kai har ku shuka,
Rashin mutunci da cin amana.

27 [inki kake ko ko sukola,
Shara kake kar kai salula,
Ka share nan can ya yi illa,
Kai }o}ari lamarin kasala,
Domin tsananta ri}on amana.

30 Malam na allo na kira ka,
Almajiran fa da anka ba ka'
An tattara an baka duka,
Uwa uba sun }aunace ka,
Don haka sai ka ri}e amana.

31 Ka san iyaye sun yi }wazo,
Sun gazgato Allah da Manzo,
Ka sanar da su Allah da Manzo,
Su zamo suna ladabi da }wazo,
Koyar da su fa ri}on amana.

28 Dukkan sana'o'in da za mui,
Mui }o}ari mu ga mun yi komai,
Da zuciya]aya kar mu nemi,
Cutar da kowa don mu sami,
Yarda ta Allah don amana.

Tir}ashi! Lalle kam wannan wa}a ta ci sunanta na Bakandamiyar wa}a, domin ta tattaro dukkanin wa]anda ya kamata a yi wa nasiha a kan ri}on amana wanda ya ha]a tun daga kan shugabanni da talakawa da ma'aikata da 'yan kasuwa da masu kowace irin sana'a kamar]inki da wanki har ma da 'yan dako ba a bar su a baya ba sai da aka ja kunnensu aka tunatar da su game da muhimmancin ri}on amana.

Malama Raihanatu Usman ba ta tsaya nan ba, ta juya da garga]inta zuwa ga mata domin yin kira gare su a kan ri}on amana da kyautata]abi'u da kula da ibada da kuma bin aure sau da }afa, ga abin da take cewa:

33 Mata ku karka]e kunnuwanku,
Ku gyara salla kui ta kanku,
Ku kama aure ban da shakku,
Ku tsarkake kuma zuciyarku,
Allah ya sa mu ri}e amana.

34 Ta mijinmu har da ta ‘yan uwansa,
Na nesa kusanci kar mu }osa,
Idan yana da uwa mu gaisa,
A waje na taimako kar mu }osa,
Mu ri}e fa Al}awarin amana.

35 ‘Ya’yan miji kuma kar ku }i su,
Ha}}in abinci tufa mu ba su,
{annen miji kuma duk mu so su,
Yayye da kakanni dukansu,
Kar dai mu yarda mu bar amana.

36 Yi tarbiyyar yaranki jimla,
Ki zamo fa ba kya yin kasala,
Wajen training har da salla,
Da koya aiki har sukola,
Koyar da su fa ri}on amana.

37 Dukkan fa aiki sai mu gane,
Tsarki na zuci ake bi]a ne,
Idan aka sa riya ya yi muni,
Komai muke yi ba sukuni,
Wajen fa Allah mu kayuta }auna.

38 Sannan idan kinvsa hijabi,
Ki tsarkake niyya ki dubi,
Zance na Allah, kar ki dubi
Aiki na masu riya da aibi,
Don su fa ba sa kyauta }auna.

39 A gida ki rufe jikinki,
Ki sanya riga ki]aura kanki,
Ki tsarkake suturar jikinki,
Har ma jikinki saboda ha}}in
Mijinki ki ri}e amana.

40 Ki zamo natsatstsa wajen kalami,
Kwantar da murya ki san mu}ami,
Irin na mata masu kalami,
A hankali domin su sami
Rahama ta Allah don amana.

Wannan wa}a ta Rahanatu Usman ba ta tsaya ga jigon ri}on amana ka]ai ba, har ma sai da ta ta~o nasiha a kan wasu batutuwan da suka shafi mata kamar tsafta da kula da tarbiyyar yara da shiga ta }warai (lullu~i) da kuma kyautata dangantaka tsakanin mata da ‘yan uwan mazajensu da ladabi da biyayya ga miji da sauransu. Bayan da mawa}iyar ta gama nasiha da garga]i ga mata, sai ta ga akwai bu}atar yin nasiha ga maza domin jawo hankalinsu a kan ha}}o}in matansu da ke kansu wanda sai kowa ya tsare ha}}in]an uwansa ne sannan za a zauna lafiya.

Ga abin da take cewa:

41 Ku ma maza sai ku sanya lura,
Don kar ku yarda ku zam garara,
Kun]au amana don ku aura,
Kui hattara kuma ku bar Gadara,
Kui ji tausayinsu saboda }auna.

42 Sutura abinci tufa ku ba su,
Sannan ku }arfafa tarbiyyarsu,
Wajen zama ilimi ku ba su,
A waje na kwana kar ku }i su,
Don Allah dai ku ri}e amana.

Har wa yau, Raihanatu Usman ta ta~o irin rawar da hukuma take takawa wajen kula da al'ummarta ta hanyar kyautata rayuwar mutane da samar masu da abubuwan jin da]i. Ga abin da take cewa kamar haka:

17 Kun san hukuma uwa uba ne,
Kowa tana so yay sukuni,
Domin hakan nan ta sanya tsani
Maza da mata mu san sukuni,
Sannan mu tsai da ri}on amana.

18 Hukuma Allah ya taimake ki,
Tsarin da kinka yi kin yi aiki,
Don ko'ina kin sanya birki,
Domin mutane su gyara aiki,
Har ma fa kin hana cin amana.

19 Kin ansa al}awari ga Allah,
Don haka ba kya yin kasala,
Dukkan wurare masu illa,
Kin bincika har kin yi jimla,
Gyaran mutane har mazauna.

20 Al}arya ce ko fa }auye,
Duk makarantu don su waye,
Ga asibitoci don su warke,
Kin yo rijiyoyi dan ki janye,
Halin }azanta, sannu Inna.

Ha}i}a wa]annan wa}o}i guda biyu na Raihanatu Usman da Amina Muhammadu Anda wa}o}i ne na wa'azantarwa ga kowa da kowa, masu mulki da wa]anda ake mulka, maza da mata yara da manya. Marubutan sun ta jaddada kira ta hanyar jawo hankali a kan muhimmancin ri}on amana, sai dai duk da haka sun ta~o wasu

batutuwan (jigogi) wa]anda suke da muhimmanci a rayuwar al'umma kamar ladabi da biyayya da tarbiyya da kyawawan]abi'u da tausayi da sauransu.

3.2. 3 Zamani

Zamani lokaci ne da mutane kan samu kansu a ciki, wanda yake haifar da sauye-sauyen abubuwa tun daga]abi'u da al'adu da zamantakewa da samar da sabbin abubuwa. Irin wannan sauyi da akan samu shi ake kira da sauyin zamani, wannan sauyin na iya zama mai kyau (wanda kan samar da ci gaba ta fuskar kimiyya da fasaha da sauran fannoni na rayuwa) ko mara kyau (musamman wanda kan haifar da ta~ar~arewar tarbiyya da wuyatar abubuwa). Hajiya 'yar Shehu ta yi wa}a a kan yadda zamani ya haifar da ta~ar~arewar tarbiyya musamman ga mata, ta kuwa bayyana haka ne ta hanyar zayyano matsalolin da aka samu sakamakon sauyin zamani kamar haka:

2 Allahu na fara wa}a ta da sunanka,
Ka ije bala'i da sharrin nan na zamani.

5 Kai agaji a gare mu ka kange addini,
Kana katsa aikin magaucinmu shai]ani.

6 Don keta haddi a aure sun yawaita }warai,
Har ma wa]ansu mutane babu imani.

7 Haka nan malamai manya ku tashi tsaye,
Aikinku ne ku tsare ha}}i na Rabbani.

8 Don ko abin ya kamata a bayyana shi ku ji,
In kun bari wata rana za a zub da jini.

A nan mawa}iyar ta nuna cewa ha}}in malamai ne su sa ido tare da tabbatar da cewa mutane na bin sunnar ma'aiki sau da }afa, idan har aka ga wata ~araka a cikin al'umma, to a jawo hankalin malamai don su fa]akar da jama'a don dawo da su kan hanya madaidaiciya (kamar yadda aka bayyana a muhimmanci binciken nan cewa ana sa ran ya amfani malamai masu wa'azi domin sannin matsalolin al'umma da yin fa]akarwa a kansu) . To ga shi mawa}iyar tana kokawa a kan wasu munanan]abi'u da suka kutso kai cikin al'umma sakamakon sauyin zamani, irin wa]annan]abi'u sun ha]a da cin zarafin mata da keta haddin aure wanda ba }aramin bala'i ba ne ga }asa. Domin haka, mawa}iyar ta yi kira ga malamai da sarakuna da su tashi tsaye domin kare ha}}in Ubangiji da ceto al'umma daga halaka. Haka kuma, ta ci gaba da zayyano irin]abi'un da ake da suka shafi keta haddin Ubangiji kamar haka:

10 Kan tituna kwararo lungu da banzaye,
Ya kai shararai gumakai babu imani.
11 In sun ga mata na aure sai su dinga kira,
Ke Binta, ke Hajiya har ma da fige zani.

12 In anka sami ta kirki ba ta tankawa,
In sunka sami shararu su sa~i Rabbani.

13 Allah tsare mu da su amin ku ce jama'a
Mata maza har da yara masu imani.

To malamai da sarakai ga wasi}ata,
Na dur}usa a gabanku na ba ku don ku gani.

In kun karanta ku]au ha}uri saboda kure,
Almajirarku nake don kar ku zarge ni.

Domin fa]ar Rabbi ne ku anka ba kiwo,
Daidai muke da makafi wa]anda ba su gani.

Ku za ku ja mana gora har ku kai mu gari,
Ku fitar da mu daga sharrin nan na sha]ani.

Har wa yau, mawa}iyar ba ta gajiya ba sai da ta ci gaba da zayyano irin abubuwan ~atancin da ke faruwa a wannan zamani kamar haka:

Don ko abin ya wuce haushi da mamaki,
Manyan mutane a kan titi da kaftani.

Sun raina Sunnar Rasulu Nabi'u Manzonmu,
Wallahi ba su cikawa ma da imani.

Ga karuwai 'yan uwansu ba su }aunarsu,
Sun bi babban abokin nasu shai]ani.

Sun bi shi ya kai su gun matan da ba su fita,
Da rana sai ko dare yayin da ba' a gani.
To sai ka gansu suna wa sauri suna ta kira,
Wai su ga shararan mutane jinnu shai]ani.

In ka gaya masu Allah ya haramta zina,
Har ma na mata na aure ya fi ma muni.

To sai su ce maka wai ai yanzu an ci gaba,
Allahu shi ne ya kawo wanga zamani.

Bayan da mawa}iyar ta yi bayanin yadda zina ta yi }amari a cikin al'umma har ma ta

ha]a da matan aure, sai ta juya akalar garga]in nata ga su kansu matan, domin jawo hankalinsu a kan guje wa fa]awa ga halaka, sa'annan ta shawarce su da su ri}e amanar aure da ke kansu, ga abin da take cewa:

30 Garga]ina ga mata masu bin sunna,
Ku tsare amana ta aure har da addini.

31 Ku ri}e mazanku ku daina kula banzaye,
Ma}iyan Rasulu abokan nan na shai]ani.

32 Su sun ~ace ba su kunya ba su jin tsoro,
Ya ku shararai magautan nan na adanani.

33 Me za su ba ku ya amfane ku nan duniya?
Har za ku cutar da kanku ku sa~i Rabbani.

34 Har ma ku cuci mazanku ku ~ata aurenku,
Kuma ran }iyama ku tashi cikinsu fattani.

35 Don Allah domin ma'aiki na yi ro}on ku,
Mu daina kallon gadajen nan na zamani.

36 Mu daina kallon su kumbobi gami da kabord,
Su ne suke sa wa]ansu su bi shi shai]ani.

37 Kun dai ji }aulinsa Jallah wa Azza inda ya ce,
Ku duba }arshen izzazul kwaga bayani.

Idan aka yi la'akari da wa]annan wa}o}i, za a tarar cewa wa'azin da marubutan ke yi a wa}o}insu ya fi shafar mata da matsalolin da matan ke fama da su. Ga shi dai mun ji yadda Hajiya'Yar Shehu take ta garga]i a kan cin zarafin aure da ake a wannan

zamani.

Har wa yau, mawa}iyar ta ci gaba da garga]i ga mata da su cire son abin duniya da kwa]ayi a rayuwarsu har ma ta danganta garga]in nata da tunasarwa a kan surar nan mai tsoratarwa wadda ke bayanin yadda tashin }iyama za ta kasance (Suratul Zalzala). A ~angaren Shema'u Abdullahi kuwa, wa}arta ta zamani bayani ta yi kan matsayin lokaci wajen kawo sauyin zamani, sa'annan ta yi kira ga jama'a da su yi kyakkyawan amfani da lokacinsu wajen yin abubuwan da suka kamata a rayuwa. Ta yi wannan bayani ne tun a baituka na farko na wa}ar kamar haka:

1 Zamani riga ne,
Ko in ce wando ne,
Sa shi ko sutura ne,
Ko ka bar shi kasance.

2 Sa'ar mutum yayinsa,
Girman mutum aikinsa,
{ashin mutum shayinsa,
{wazon shi shi zai zarce.

A nan mawa}iyar na nuna cewa ya kamata kowa ya yi shirin tafiya da zamani (wato zamanin da yake ciki) musamman ta hanyar tashi tsaye da yin ayyukan da za su kawo ci gaba a cikin al'umma wanda wannan aiki ko }o}ari na mutum zai sa mutum ya yi fice har ya samu girma da daraja a idon al'umma,

Haka kuma, mawa}iyar ta ci gaba da bayanin matsayin zamani a wajen al'umma kamar haka:

3 Lokaci yanayi ne,
Zuwa yake ya yane,
Juyi yake ka gane,
In ya zo ya }wace.

4 Taso maza kai aiki,
Ko ko je gun]inki,
Ya'alla ko kai mulki,
Ko a bar ka a kwance.

A nan, marubuciyar ta nuna cewa duk wanda bai tashi ya nemi abin yi ba to tabbas za a bar sa a kwance ya zama mantau a cikin al'umma, wato kowa ya manta da shi ba mai kula shi bare ya yi hul]a da shi. Daga nan kuma sai ta ci gaba da cewa:

5 Zamani hatsarinsa,
Kuruciyya matsayinsa,
Ilimi ya zam matsarinsa,
Allah ya sa mu dace.

6 Lokaci na tafiya,
Ayyuka na rakiya,
Zuciya sa niyya,
Kul ka bar ta ta kubce.

Hausawa dai kan ce "{uruci dangin hauka…" A wannan wa}a, mawa}iyar ta nuna matsayin }uruciya a wajen mutane, wato lokacin }uruciya lokaci ne mai hatsari ga matasa wanda in ba a yi hankali ba sai matasa su shiga wani hali na kaico ba domin komai ba sai don suna ganin cewa ai yanzu zamaninsu ne, za su iya yin duk abin da

suka ga dama. Amma kuma mawa}iyar ta nuna cewa neman ilimi kan zama kariya ga }uruciyar mutum, don haka ta yi kira ga matasa da su tashi tsaye su nemi ilimi. Har wa yau, ta jaddada muhimmancin amfani da lokaci yadda ya kamata, wato a koyaushe mutum ya zama mai tsara abin da zai yi da lokacinsa tare da tabbatar da ka yi amfani da lokacin a kan abin da ya dace.Bayan haka, mawa}iyar ta bayyana baiwar da Allah (S.A.W) ya yi wa bayinsa ta hanyar tsara musu lokuttan rayuwarsu kamar haka:

7 Dare makwancin bawa,
Lokacin hutawa,
Duhun ciki sa natsuwa,
Zo ka kwanta huce.

9 Rana tsawo sha aiki,
Cikinta za ai girki,
Yininta ne sha mulki,
Komai kake ka zarce.

11 Da yamma ne za a cale,
Kowa ya tsale ya }yale,
Ai walwala ai tsalle,
Mu yi su ranmu a huce.

12 Sai alfijir sa ni'ima,
Haskensa ne sa zamma,
In yai tsawo sa himma,
Ka tashi nan gaggauce.

Wa]annan baituka masu bayanin muhimmancin karkasa lokacin]an Adam sun yi daidai da fa]ar Ubangiji ma]aukakin sarki a inda yake cewa.

…Kuma muka sanya dare (ya zama) sutura?

Kuma muka sanya yini (ya zama) lokacin neman abincinku?

(Naba'i aya ta 9-10)

Lalle kam lokaci muhimmin abu ne a rayuwa, domin haka ma Allah (S.A.W) ya yi rantsuwa da shi a wurare daban daban a cikin al}ur'ani mai girma.

Har wa yau, mawa}iyar ta ci gaba da bayyana yadda akan samu kwanaki zuwa shekaru har zuwa }arni duk }ar}ashin lokutta. Ga abin da take cewa:

13 Kwana bakwai sha }irga,
Mako guda ka jirga
Komai muke ma farga
In mun ~ace ta kubce.

20 Su shekaru masu yawa,
Guda-guda masu hawa,
{arni suke komawa,
Yayin su ne za su fice.

21 Ga damina ga rani,
Kaka ake yin sha'ani,
Ai ta ka]i har da gini,
Yayin biyan duk rance.

Wannan na nuna tsarin lokutan Bahaushe a shekara, wato kwana bakwai ke bayar da mako, mako hu]u su bayar da wata, wata goma sha biyu su bayar da shekara, shekaru]ari su bayar da }arni. Sa'annan akwai yanayin damina da rani wato lokacin shuka da lokacin kai amfanin gona gida (kaka). Wa]annan lokuta ne masu matu}ar muhimmanci a wajen Bahaushe, domin lokacin damina ne ake tattalin abin da za a ci

a shekara. Kuma daga arzikin da ya samu na amfanin gona ne zai yi gini, ya yi aure ya yi shagulgula daban daban.

3.2.4 Lullu~i Ga Mata

Lullu~i shiga ce da mata ke yi domin rufe jikinsu yayin da fita waje ta kama su, shi dai lullu~i wajibi ne ga kowace mace musulma wadda ta kai munzalin balaga. Allah ma]aukacin sarki ya umurci mata da su rufe jikinsu yayin da za su fita waje ko kuma yayin da suke tare da mutanen da ba muharramansu ba, wannan horo kuwa ya zo ne a cikin Al}ur'ani mai girma inda Allah ya umurci matan Annabi da sauran mata da su suturta tsiraicinsu.

Lullu~i na]aya daga cikin kyawawan]abi'un da Musulunci ya kawo wa mata wanda ya kare mata daga cin zarafi da matsalolin da sukan shiga a sakamakon bayyana tsiraicinsu. Ha}i}a lullu~i babbar kariya ce ga mata domin haka ma Shehu Mujaddadi ya sa shi a cikin muhimman }udurorin da ya nemi sarkin Gobir (Bawa Jan Gwarzo) da ya lamunce wa Musulmi a kan a bar su su ri}a yi. Haka kuma Shehu da almajiransa sun yi tsayuwar daka wajen ganin mata sun ri}a lullu~e jikinsu domin kare kansu daga fa]awa cikin halaka.

Wannan kyakkyawar]abi'a ta fara rauni tsakanin mata, domin mata sun fara watsi da kariyar da Allah ma]aukakin sarki ya tanadar musu. Domin wasu mata sun za~i su ri}a yawo tamkar tsirara da sunan gayu ko wayewa. Wannan dalili ne ya sa Hauwa

Gwaram ta ga akwai bu}atar yin wa'azi ga mata domin tunatar da su matsayin da Allah ya yi musu da kuma dokokin da Allah ya sa musu na rufe al'aurarsu a gaban wa]anda ba muharramansu ba, al'urar mace kuwa ta }unshi dukkan jikinta in banda fuskarta da tafukan hannayenta.

Fitaccen jigon wannan wa}a shi ne nuna muhimmancin lullu~i ga mata. Baya ga haka, wa}ar na]auke da }ananan jigogi a kan abubuwan da suka shafi mata. Mawa}iyar ta fara da kira ga mata da su ri}a yin lullu~i yayin da fita ta kama su, ta bayyana cewa:

4 {addara in ta kira ki,
Kin fito waje za a gan ki,
Sai a gan ki da lullu~inki,
Dena nunin kyawun jikinki,
Lullu~i na kyau ga mata.

5 In kina waje ko a]aki,
[aure kai zai kyau gare ki,
Yafa]an gyale sai]iyarki,
San mutunci gun zamanki,
Lullu~i na kyau ga mata.

6 Kun ga mataye na sunna,
Ba su kwance zani su zauna,
Kishiyoyi 'yan uwana,
Ba fa]a balle hiyana,
Lullu~i na kyau ga mata.

A wa]annan baituka, mawa}iyar ta hori mata da su ri}a lullu~i, kuma in har za su yi lullu~in to su yi shi yadda ya dace ba wai su nemi]an gyale wanda za a ri}a ganin jikinsu su ce wai sun yi lullu~i. Ta bayyana cewa irin wa]annan gyaluluwan da suke

sawa sai dai yaran da ba su isa hukunci ba wato wa]anda ba su balaga ba. Haka kuma mawa}iyar ta hori mata da su zauna da abokan zamansu (kishiyoyi) lafiya ba fa]a ba gaba domin haka aka san mata na sunna na yi. A baya (baiti na uku) mawa}iyar ta yi Allah wadai da irin jahilan matan nan masu sakin jiki a kan hanya wai su nan za su ba yara nono, ga abin da take cewa:

3 Zan bayanin masu goyo,
Kan suna tafiya da goyo,
Sai su kwance zane su juyo,
[a ya sha mama su juya,
Lullu~i na kyau ga mata.

A baiti na biyu ma cewa ta yi:

2 Dariya da ganin tsiraici,
Gum musulmi fasi}anci,
Kori yau da cim mutunci,
Ko }azaf ko jahilanci,
Lullu~i na kyau ga mata.

Lalle wa]annan munanan]abi'u ne da ya kamata mata su guda, ya kamata mata su dage su nemi ilimi domin ya}ar jahilcin da ke damunsu musamman ma a kan abin da ya shafi lullu~i. Har wa yau, ma mawa}iyar ta ci gaba da cewa:

7 Mummuna mai son ta tsira,
Ita ce ta kula da gyara,

Ba ta yin yawo tsirara,
Ba ta ro}on masu nera,
Lullu~i na kyau ga mata.

8 In kina da rabo ki tuba,
Karuwa da giya da taba,
Kar su ja ki ki shan azaba,
Sai ki hanzarta ki tuba,
Lullu~i na kyau ga mata.

A nan mawa}iayar ta yi kira ga mata da su tuba su gyara halayensu kuma su kyautata]abi'unsu musamman kula da gyara ibada da kuma kawar da kai daga kwa]ayi, in dai har suna so su tsira a gobe }iyama. Haka kuma, ta nuna cewa ba wa]annan ne ka]ai ya kamata mata su gyara ba har ma da kiyayewa a kan dokokin Allah musamman a kan abin da ya shafi aure, ga abin da take cewa:

9 Daina yin aure da idda,
Lalubo Kalmar shahada,
Yi }o}arin koyon ibada
Kar ki zan mai ~oye ada,
Lullu~i na kyau ga mata.

10 Ya kamata ku zo ku tuba,
Tun macewa bai taho ba,
Nemi aure kar ki duba,
Yaudarar mai ba ki taba,
Lullu~i na kyau da mata.

Mawa}iyar ta jaddada kira ga mata da su ri}i aure da kyau, kada su ri}a aure yayin da iddarsu ba ta cika ba. Kuma ta jaddada kira ga mata da su ri}a neman ilimi a ko

yaushe tare da neman gafarar Ubangiji. Haka kuma, mawa}iyar ta fa]i dalilinta na yin wannan wa}a kamar haka:

11 Mun ga gyara ya wuyata,
Yanzu ~arna ta yawaita,
Masu gyara sun }aranta,
Gaskiya kuma ta wuyata,
Lullu~i na kyau ga mata.

Da wannan dalili ne na yawaitar ~arna da }in gaskiya da kuma }arancin masu fa]akarwa ya sa mawa}iyar ta shirya wannan wa}a don yin wa'azi a kan jigon lullu~i ko Allah ya sa mata su ji nasiharta kuma su yi amfani da ita. Domin haka ma ta ci gaba da kira kamar haka:

12 Mui ta himma kar mu ta~e,
Dan hali ke sa a ra~e,
Masu zamba ku je ku ra~e,
Gaskiya fa]inta ra~e,
Lullu~i na kyau ga mata.

13 'Yan musulmi mui du'ai,
Don mu samu rabo ga A'i
Mui du'a'i kan bala'i,
Jahili ba ya du'a'i,
Lullu~i na kyau ga mata.

14 Kun ga mataye na kirki,
Ko kamar waje ko a]aki,
Ba su }aunar bata aiki,
Tattalinsu zama a]aki,

Lullu~i na kyau ga mata.

Haka dai Hauwa Gwaram ta yi ta yin nasiha ga mata a kan su koma wa Allah su zauna a]akunansu, in kuma har fita ta kama su to su fita cikin shigar da ta dace. Har wa yau, mawa}iyar ta tsoratar da jama'a a kan ranar tashin }iyama, ga abin da take cewa:

16 Sai ku tsoraci ran hisabi,
Za a watsowar kitabi,
Masu kyau da na masu aibi,
Zuciyar da ta goya gaibi,
Lullu~i na kyau ga mata.

17 Za a ce mu karanta aiki,
Da mukai a fagge da]aki,
Karuwai da karanta aiki,
Lahirarku saboda mulki,
Lullu~i na kyau ga mata.

18 Duk abin da ka ~ata aiki,
Za a bi shi sashi a sashi,
Ko gurin da ka ~ata taki,
Ko ga sa~o ko ga shirki,
Lullu~i na kyau ga mata.

19 Na yi kuka nai nadama,
Zan bayanin garga]inmu,
Na yi kuka nai nadama,
Tausayin kai babu himma,
Lullu~i na kyau ga mata.

A nan an sami jigon tsoratarwa game da ranar hisabi, ranar da za a]auki ayyukan mutane a auna su]aya bayan]aya, domin haka mawa}iyar ta yi kira ga mutane baki]aya da su kyautata ayyukansu, kuma su kawar da sa~o da shirka in har suna so su sami tsira daga azabar lahira. Haka kuma, ta }ara garga]in mata a kan su koma ga

Allah kamar yadda ta bayyana cewa:

20 ‘Yan uwa mata ku ji mu,
[an bayanin garga]inmu,
Mai rabo ce za ta ji mu,
Fan]ararra sai ta }i mu,
Lullu~i na kyau ga mata.

21 Duk abin da ya zo gare mu,
Jalla gyara kwanciyarmu,
Zunubanmu da suke gare mu,
Sauwa}e wahala gare mu,
Lullu~i na kyau ga mata.

Hausawa dai kan ce “ciwon ‘ya mace na mace ne.” tabbas Hajiya Hauwa Gwaram ta tabbatar da wannan magana ganin yadda ta damu da halin da mata ke ciki na ~ata da karya dokokin Ubangiji, har ta yi ho~~asa ta]auki al}alami da takarda ta rubuta wa}a domin wa’azantar da mata game da muhimmin abin da ya shafi rayuwarsu wato lullu~i. Ha}i}a wannan wa}a cike take da nasiha da garga]i tare da tsoratar da mata game da halin da za su iya samun kansu sakamakon watsi da lullu~i, kuma ta yi kira gare su da su ja}i jahilci su kyautata ibada kuma su bi mazajensu, su zauna da kishiyoyinsu lafiya, sa’annan su guje wa ru]in duniya don samun tsira duniya da lahira.

3.2. 5 Kishi

Kalmar kishi kalma ce mai bakandamiyar ma’ana, wato tana da ma’anoni da dama.

Kalmar kishi na iya]aukar ma’anar kishin zuci ko kishin kai ko kishin sauri ko kuma]abi’ar kishi da aka san [an Adam da ita.

Kishi na aukuwa ne yayin da mutum ya fahimci cewa ana nema a yi tarayya a kan abin da yake so kuma yake gurin mallaka shi ka]ai.(Bugaje, 2009).

A }asar Hausa an fi danganta kishi ga mata. Wannan ba ya rasa nasaba da yawan aukuwar kishin da ake samu tsakanin mata sakamakon al’adar Bahaushe ta auren mace fiye da]aya.

Mawa}a da dama (musamman mata) sun yi wa}o}i a kan kishi, wasu daga cikin mawa}an sun yi wa]annan wa}o}i ne a baka wasu kuma a rubuce, kuma sun yi su ne domin kira ga mata da su rage zafin kishi. Ru}ayyatu Sabuwa Nasir na]aya daga cikin mata marubuta wa}o}in Hausa da ta tsara wa}a a kan jigon kishi.

Ta fara isar da sa}on ta hanyar jawo hankali kamar haka:

8 Bayan haka ga manufata,
A bisa kishi na yi ta,
Domin abin kam ya }azanta,
Hassada kushe da }eta,
Fa]uwa ne gaskiya.

9 ‘Yan uwana kun ga kishi,
Bai da amfani a bar shi,
Shin ko kun san ma’anarshi
Ha]ama son kai da }yashi,
Da rashin bin gaskiya.

Mawa}iyar ta nuna cewa kishi ba shi da wani amfani ga mata domin ba abin da yake

nunawa sai son kai da ganin }yashi da kuma rashin bin gaskiya, domin su mata sun gasgata cewa Allah ma]aukakin sarki ne ya ba maza damar auren mace fiye da]aya, domin haka in suka nuna zafin kishi a kan wannan batu to sun nuna }in gaskiya kenan.

Domin haka ma ta }ara bayani da cewa:

10 Tun da Allah ne ya tsara,
Lamarin kishi mirara,
Shi ya yarda maza su tara,
Jumlar mata su tara,
Adadi ya wuce]aya.

11 Kun ga dai jumla na aure,
Hu]u cif cif za su tare,
Inda ko har }warare,
{war}warori ne }warare
Dan a gane a jiya.
12 Rabbu ya yardam masu,
Don haka mu ma mu bi su,
Sau da hannu mu bar musu,
A tsakaninmu da kuma su,
Ba fa]a ba tankiya.

A nan, mawa}iyar ta tunatar da mata game da umurnin Ubangiji da ya yi a cikin {ur'ani a kan adadin matan da namiji zai iya aure wanda ya kama daga biyu zuwa hu]u, sai dai in ba zai iya yin adalci ba sai ya tsaya ga]aya ko abin da hannun damarsa ta mallaka (baiwa). Saboda haka, in dai har mata sun san da wannan, ba abin da ya dace illa su bi dokokin Ubangiji ba jayayya.

Ha}i}a akwai bu}atar a sami mata su ri}a wa'azi ga mata 'yan uwansu musamman a kan mas'aloli irin wa]annan (batun kishi) domin }ila wa'azantarwar ta fi shigarsu

ganin cewa ‘yar uwarsu mace ce wadda ta san matsalolinsu ke yi masu nasiha. Wannan dalili ne ya sa malama Ru}ayyatu ta }ara zage damtse da bayar da himma wajen }ara jawo hankalin mata a kan wannan batu kamar haka:

13 Mu yarda da hukunci,
Na ilahu mahalicci,
Shi ka]ai ne maka]aici,
Ku mu bar sha’awar ka]aici,
Rabbana shi ne]aya.

14 Ku mu bar }in tarayya,
Shi ka haifad da hamayya,
Tun da Allah ne]aya,
Ba abokin tarayya,
A garai ba kishiya.

15 Mu mutane babu makawa,
Tarayyarmu da ‘yan uwa,
Mu ababen haihuwa,
Ai saboda haka kuwa,
Dole ne mui tarayya.

A nan mawa}iyar tana jawo hankalin mata a kan su guji }in abokiyar zama domin Allah ya yi]an Adam domin ya yi tarayya da]an uwansa wurin taimakekeniyar rayuwa. Ta yi kira ga masu }in kishiya domin su zauna su ka]ai, da su tuna fa cewa ka]aici sifa ce ta Allah wanda shi ka]ai ne ba ya da abokin tarayya kuma duk wanda ya nemi ya]auki wannan siffar ta Ubangiji ya sa a kansa to lalle ya]auko wa kansa abu mai girma (Allah ya kyauta). Saboda da haka, sai marubuciyar ta ci gaba da nasiha da jaddada muhimmancin bin dokokin Allah a kan kome tare da bin gaskiya

domin samun zama lafiya. Ga abin da take cewa:

17 Duk a daina gaganiya,
A bi turbar lafiya,
Ai zama na halaliya,
Ba fa]a ba tankiya,
Ko sabo ma da]iya.

18 Don su tashi da son zumunci,
Cikin ha]in kai da aminci,
Ba ba}in }uduri a zuci,
Wanda kan ce ‘yan ubanci,
Ya fi kyau haka gaskiya.

Lalle in har mata suka bi shawarar da marubuciyar nan ta bayar to za su kawo }arshen mummunar al’adar nan ta ‘yan ubanci a }asar Hausa inda ‘yan uwa ke nuna }in juna wai domin uwayensu ba]aya ba. Idan har aka yi amfani da wannan nasihar, ‘ya’ya za su tashi da zumunci da son juna da }auna da tausayi da kuma ha]in kai da zama na ciyar da juna gaba. Lalle wannan nasiha ta }unshi babban al’amari wanda matu}ar aka yi amfani da ita, za ta haifar da kyakkyawan sauyi a rayuwar al’umma baki]aya. Domin ganin an cimma wannan manufa ne ya sa marubuciyar ta ci gaba da jaddada manufarta ta }ara kira da jawo hankali kamar haka:

20 To fa don haka ya zamanta,
Rage kishi ya wajabta,
A kasance da nagarta,
Don]iya sa yi zumunta,
Halisan ba wariya.

21 ‘Yan uwa abin da ya fi,
Kar mu]au kishi da zafi,
Kar a ha}a rami da zurfi,
Na mugunta na ga ya fi,
Kyau a zauna lafiya.

22 ‘Yan uwa abin da ya fi,
A aje kishi a huta,
Kun ga sa kai ya fi bauta,
Wahala zakkar jiki ta,
Wohoho }ajageniya.

23 Lokaci ya yi gare mu,
Da za mu lura da kammu,
Don mu nemi abin fa kammu,
Mu bar bata lokacinmu,
Ai ga kishin kishiya.

24 Shi fa kishi wahala na,
Kuma kullum fargaba,
Kuma koma baya na,
‘Yan uwa da za a gane,
‘yar uwa ce kishiya.

Malama Ru}ayya ta nuna aibun kishi tare da ba mata shawarar abin da ya dace su yi da lokacinsu a maimakon kishi. Haka kuma, mawa}iyar ta jawo hankalin mata da cewa:

26 Mui wa kanmu fa]a da kammu,
Du}ufarmu bi]ar mu ilmu,
Kyautatawa ga mazan mu,
Kyauta halin rayuwarmu,
Ya fi kishin kishiya.

27 Duk zukata za su natsu,
Hankula don kar su motsu,
Duk ku daina mutsu-mutsu,
Ai karatun ta natsu,
Ko }wafa tag a zuciya.

28 Wahala jawur tsayayya,
Duk a yarda da gaskiya,
Bin miji ne shiriya,
Ba fa wai }in kishiya,
Ko }wafa ta ga zuciya.

29 Duk a bar su ka da a ~ace,
A tuna dai kar a mance,
Duk abin da mutum ya shifce,
To yana nan fa rubuce,
Ran gamommu da gaskiya.

Tabbas wannan batu gaskiya ne, domin haka ‘yan uwa mata ya kamata a yi amfani da wannan nasiha ta Ru}ayyatu Sabuwa Nasir domin ganin an samu tsira duniya da lafira, tare da samun zaman lafiya da kwanciyar hankali a dukkan gidajen aure.

3.3 Na]ewa

Wa]annan wa}o}i da aka yi sharhi a kansu sun bayyana tunanin mata marubuta game da abin da suke ganin ya kamata al’umma (musamman mata) za su gyara domin samun zaman lafiya da kwanciyar hankali da kuma samun tsira duniya da lahira. Kuma sun yi kira ga malamai da shuwagabanni da su kula da tarbiyyar al’umma, su ci gaba da wa’azi ga mata musamman a kan abubuwan da suka shafi matan.

Kamar yadda muka gani daga cikin sa}onnin da suke isarwa akwai batun neman ilimi inda aka sami marubuta biyu (Hajiya Hassana Sufi da Shema'u Abdullahi) suka rubuta wa}o}i musamman don fa]akar da mutane game da muhimmancin neman ilimi. Haka kuma akwai batun ri}on amana, inda aka sami Raihanatu Usman da Amina Muhammadu Anda suka rubuta wa}o}i domin isar da sa}o game da muhimmancin ri}on amana. Har wa yau, an sami wa}o}i biyu da ke magana kan zamani sai dai suna da mabambantan sa}onni da suke isarwa, wa}a ta farko ita ce wa}ar zamani ta Hajiya 'Yar Shehu da kuma wa}ar Zamani ta Shema'u Abdullahi. A batun sa}onnin da suka ji~anci mata ka]ai kuwa, akwai wa}ar Lullu~i da Hauwa Gwaram ta rubuta da kuma wa}ar kishi da Ru}ayyatu Sabuwa Nasir ta rubuta wadda ke bayanin aibun kishi ga mata.

BABI NA HU[U: TSARI DA SALO A RUBUTATTUN WA'AZI NA MATA NA {ARNI NA ASHIRIN

4.0 Shimfi]a:

Wannan babi ya }unshi sharhi ne a kan tsari da salon da ke }unshe cikin rubutattun wa}o}in mata na wa'azi na }arni na ashirin. Za a nazarci tsarin ne da salo daga wa}o}in da aka za~a domin yin nazari. A farko an kawo ma'anar tsari da misalai daga wa}o}i da kuma ma'anar salo da kayan cikinsa da kuma misalan salo daga wa}o}in

da aka za~a domin nazari a wannan fage.

4.1 Ma'anar Tsari a Wa}a

Yakawada (1983), ya bayyana tsari da cewa shi ne siffa ko yadda wani abu yake. Tsari a wa}a na nufin yadda marubuci ya shirya wa}arsa a rubuce. Tsarin rubutacciyar wa}a ya samo asali ne daga tsarin rubutattun wa}o}i wa]anda kan zo da abubuwa kamar haka:

4.1.1 Mabu]i Da Marufi

Mabu]i: yana nufin yadda mawa}i ya fara rubuta wa}arsa. Mafi yawa daga cikin marubuta wa}o}in Hausa na amfani da salon nan na masu jihadi wa]anda a mafi yawan lokaci sukan fara bu]e wa}arsu ne da ambaton Allah ko godiya ga Allah da salati ga Manzo (S.A.W), kamar a wa}ar Tabban Ha}i}an ta Shehu inda a baiti na farko yake cewa:

Mui yabo 'yan uwa ga Sarki ha}i}an,
Jin}ayi aggarai da kyauta ha}i}an,
Talikai sun sano sanin nan ha}i}an,
Gode Allah mai sarauta ha}i}an,
Dai da ya i ma kowa tabban ha}i}an.

Haka kuma, akan sami wasu mawa}an da kan bu]e wa}o}insu da tsarin da suka ga dama, misali wa}ar {alubale ta A}ilu Aliyu da ta fara da tsari kamar haka:

{ulun }ulufit, abu dun}ule,
{alau na }ale, }alubale.

Mafi yawa daga cikin mata marubuta wa}o}in wa'azi na amfani da tsarin nan na

marubutan }arni na sha tara, wato bu]e wa}a da ambaton Allah da kirari ga Manzo Annabi Muhammadu (S.A.W). kusan mafi yawa daga cikin wa}o}in da aka nazarci jigonsu a wannan aiki sun fara ne da wannan tsari, sai dai akwai ‘yan }alilan da suka bijire wa wannan tsarin. Daga cikin wa]anda suka ari tsarin marubutan }arni na sha tara akwai wa}ar ilimi ta Hassana Ahemd Sufi wadda ta bu]e wa}arta kamar haka:

1 Bismilla na fara wa}a ta da Allahu,
A cikin sifofin Ta’ala har akwai ilmu.

2 Ina salati ga Manzon namu mai falala,
Mun ji an ce fa shi ne Madinatul Ilmu.

3 Da alihi masu girma haka daraja,
Da sahabai masu girma sadatul Ilmu.

Ita ma Shema’u Abdullahi ba a bar ta a baya ba, domin ita ma tsarin mabu]inta ke nan a wa}arta ta ilimi kamar haka:

1 Da sunan Allah nai niyya,
Wa}a zan yo ta a kan ilimi.

2 Tsira da aminci kan [aha,
Manzonmu Muhammadu maso ilimi.

3 Ya }ara sonsa da yardarsa,
A kansu sahabbai mazo ilimi.

Har wa yau, Amina Muhammadu Anda ma ta yi amfani da tsarin mabu]i na bu]e wa}a da yabon Ubangiji kusan a dukkan wa}o}inta, babban misali shi ne a wa}arta ta “Ri}on Amana” inda ta bu]e wa}ar kamar haka:

1 Bismillah za ni fara,
Wa}ar da za ni tsara,
Don ga ta za ni rera,
Allah ka ban basira,
Wa}ar ri}on amana.

2 Farkon yabonmu Allah,
Don ba kamar shi Allah,
Ya wahidun Ta'ala,
Ka hana ni jin kasalah.
Wa}ar ri}on amana.

Wa}ar da ta bijire wa wannan tsari ta]auki tsari na daban na nuna gwanintar harshe ita ce wa}ar *Zamani* ta Shema'u Abdullahi wadda ta fara kamar haka:

1 Zamani riga ne,
Ko in ce wando ne,
Sa shi ko sutura ne,
Ko ka bar shi kasance.

Daga wannan misalai da muka gani za mu iya cewa kusan mafi yawa daga wa}o}in mata na wa'azi sukan bu]e wa}o}insu da ambaton Allah da salati ga ma'aiki, sai dai 'yan }alilan da akan samu da suke farawa da wani tsarin mabu]i na daban.

Marfi/makulli: yana daga cikin tsarin rufe wa}a ko kammala wa}a da Hausawa suka aro daga tsarin rubutattun wa}o}in Larabawa. Shi ne baitukan da mawa}i ya kammala wa}arsa da su. Mafi yawa daga cikin marubuta wa}o}in Hausa kan rufe wa}arsu da addu'a da kuma godiya ga Allah, wani lokaci akan sami tarihin wa}ar a marfin wa}a, kamar abin da ya shafi sunan mawa}i da adireshinsa har ma da ramzin wa}ar (shekarar da aka yi wa}ar). Wannan tsari kuwa ya fara yin fice ne a wajen marubuta

wa}o}in }arni na sha tara.

Mafi yawa daga cikin wa}o}in wa'azi na mata sun yi amfani da fitaccen tsarin rufe wa}a da marubuta wa}o}in }arni na sha tara suka fi amfani da shi, domin cikin wa}o}i takwas da aka nazarta a wannan aiki bakwai daga cikinsu sun }are da tsarin addu'a da godiya ga Allah da kuma sunan mawa}iya. Misali a wa}ar "Ilimi" ta Hassana Sufi, ta rufe wa}arta ne da addu'a da tarihin wa}ar kamar haka:

83 Allah dasa mana bishiyar ilmu, amina,
'ya'yanta su yi ta zuba a Nijeriyar tamu.

84 Hassana'u 'yar Ahmed ita tai yi ta ran juma'a,
Almajira nake ni ce mai batun ilmu.

85 To malamai sai ku gafarce ni kan kuskure,
Kun san halin jahilai Allah ya yafe mu.

86 Baiti tamanin da shida na rufe wa}a,
Allah ta'ala ina ro}o ka ban ilmu.

Haka kuma, Raihanatu Usman ta rufe wa}arta da yabo ga Manzo (S.A.W) da sallama tare da bayyana sunanta kamar:

44 Mu so Muhammadu]an Amina,
Domin fa shi ya ri}a amana,
Ya ba da mamakin amana
Ta]ora dutsen mu gane,
Rannan ya zan suna Aminu

46 Na]an ta}aita 'yan Uwana,
Domin mu gane mui ta murna

Mu zam muna ha]a kai da }auna,
Ga masu mulki ban da raina
Abin da sunka yi don amana.

47 Nai sallama zan dakata ne,
Raihana ‘yar Usman ku gane,
Ta yo rubutu ta }arfafa ne,
Gami da wannan zamani ne,
Allah ya sa mu ri}e amana.

Hajiya ‘Yar Shehu ta rufe wa}arta mai suna *Zamani* da tsarin da sauran mawa}an suka yi amfani da shi kamar haka:

38 Tamat bihamdullahi nan na sa aya,
Allah tsare mu da sharri nan na zamani.

39 Sunanta mai tsara wa}a sai a ce Hajiya,
‘Yar Shehu ce la}abi Kano a birni masu zamani.

4.1.2 Tsarin Layukan Wa}a:

Tsarin layukan wa}a na]aya daga cikin muhimman abubuwan da ake la’akari da su a nazarin tsarin rubutacciyar wa}ar Hausa. Mafi yawan lokaci akan sami wa}o}i masu matsakaitan layuka (wato wa]anda ba su da tsawo kuma ba su da gajarta), kuma akan sami dogaye da gajerun layukan wa}a. mafi yawa daga cikin wa}o}in da aikin nan ya nazarta na]auke ne da matsakaita da kuma gajerun layuka kamar yadda za a iya gani daga misalan baituka da suka gabata.

4.1.3 Yawan Baitoci a Wa}a: wannan ma na]aya daga cikin abin da ake la'akari da shi a nazarin tsarin wa}a, wato ana duba adadin baitukan da wa}a ta }unsa, misali kamar wa}ar ilimi ta Hassana Sufi tana]auke ne da baituka tamanin da shida kamar yadda ita kanta ta bayyana a baiti na }arshe na wa}ar kamar haka:

86 Baiti tamanin da shida na rufe wa}a
Allah Ta'ala ina ro}o ka ban ilmu.

Ba kowane mawa}i ke ambaton adadin baitukan wa}arsa ba a cikin wa}a, sai dai wasu daga cikin mawa}an na yin haka ne domin in mutum ya sami wa}ar ba cikakkiya ba, zai nemi sauranta.

4.1.4 Ginin Layukan Baiti: wannan na nufin yadda marubucin wa}a ya tsara baitocin wa}arsa. Wa]annan baitoci na iya zuwa kamar haka:

Gwauruwa – wa}a mai layi]aya

'Yar tagwai – wa}a mai layi biyu

{war uku – wa}a mai layi uku

{war hu]u- wa}a mai layi hu]u

{war biyar ko Muhammasa – wa}a mai layi biyar.

Haka kuma, akan sami wa}a ta zamo an mata tarbi'i ko tahamisi. Tarbi'i na samuwa ne a inda aka]auki wa}a 'yar tagwai aka yi ma ta }arin layuka biyu a samanta ta zama layuka hu]u a kowane baiti. Tahamisi kuwa na samuwa ne a inda aka]auki wa}a {war

uku aka yi }arin layuka biyu a saman na farkon ta zama layi biyar a kowane baiti.

A wa]annan wa}o}i da aka nazarta, an sami wa]anda suka zo a matsayin ‘yar tagwai.

Misali wa}ar Hassana Sufi ta “Ilimi” ginin layukanta ya kasance kamar haka:

84 Hassana’u ‘yar Ahmed ita tai yi ta ran juma'a,
Almajira nake ni ce mai batun ilmu.

85 To malamai sai ku gafarce ni kan kuskure,
Kun san halin jahilai Allah ya yafe mu.

Haka kuma, an sami wa}a mai ginin layuka hu]u kamar a wa}ar Shema’u Abdullahi ta “Zamani”.

13 Kwana bakwai sha }irga,
Mako guda ka jirga
Komai muke ma farga
In mun ~ace ta kubce.

20 Su shekaru masu yawa,
Guda-guda masu hawa,
{arni suke komawa,
Yayin su ne za su fice.

Har way au, an sami wa}o}in da suka zo da ginin layuka biyar (Muhammasa) kamar a wa}ar “Ri}on Amana” ta Raihanatu Usman da wa}ar “Lullu~i Ga Mata” ta Hauwa Gwaram da wa}ar “Kishi” ta Ru}ayyatu Sabuwa Nasir. Misali, a wa}ar Kishi:

26 Mui wa kanmu fa]a da kammu,
Du}ufarmu bi]ar mu ilmu,
Kyautatawa ga mazan mu,
Kyauta halin rayuwarmu,

Ya fi kishin kishiya.

4.1.5 Amsa – Amo

Amsa –amo ya samo asali ne daga wani abu da Larabawa suke kira da suna }afiya. Amsa-amo na nufin tsarin ga~a da marubucin wa}a ya }are kowane baiti na wa}arsa da shi. A Hausa ana da nau'i biyu na amsa- amo, wato akwai amsa-amon gaba akwai kuma amsa-amon kari. Amsa-amon gaba shi ne amsa-amon da gabar }arshe ta wa}a ke }arewa da shi a kowane baiti. Dunfawa (2003) ya kasa amsa-amon ga~a gida hu]u kamar haka:

Babban Amsa-amo(amsa-amon waje): shi ne amsa-amon da mawa}i ya gina wa}arsa a kan wata ga~a wadda dole kowane baiti na wannan wa}ar ya }are da ita.

{aramin amsa-amo(amsa-amon ciki): shi ne ga~a da layukan cikin kowane bati (mai fiye da layi biyu) ya }are da shi. Ana samun }aramin amsa-amo ne a wa}ar mai }war uku ko hu]u ko biyar, amma ba a samunsa a wa}a mai }war]aya ko biyu. Misalin }aramin amsa-amo shi ne kamar haka:

41 Ku ma maza sai ku sanya lura
Don kar ku yarda ku zam garara
Kun]au amana don ku aura
Kui hattara kuma ku bar gadara
Ku ji tausayinsu saboda }auna.

42 Sutura abinci tufa ku ba su
Sannan ku }arfafa tarbiyarsu

Wajen zama ilimi ku ba su
A waje na kwana kar ku }i su
Don Allah dai ku ri}e amana.

A nan a lura da ga~ar }arshe ta kowane layi da aka ja wa layi ita ake nufi da }aramin amsa-amo ko amsa-amon ciki, misali mun ga layuka hu]u na baitin farko sun }are da ra, yayin da baiti na biyu layuka hu]u mai bi masa ya }are da sa. Haka kuma, idan an lura da layi na biyar na wa]annan baituka za a ga sun }are da (na) wanda shi ne babban amsa-amo ko amsa-amon waje wanda shi ne kowane layin }arshe na kowane baiti a wa}ar ya }are da shi.

Amsa-amon farawa: shi ma nau'in amsa-amo ne da mawa}a ke amfani da shi wajen tsara wa}arsu. Akwai hanyoyi biyu da ake samun irin wannan amsa-amo, hanya ta farko ita ce, a inda mawa}i ke son amfani da wani sauti a matsayin amsa-amonsa, sai ya fara kawo wannan sauti ya zama }aramin amsa-amon baitinsa na farko kuma ya ci gaba da amfani da shi a matsayin babban amsa- amon na wa}ar gaba]aya, misali:

1 Ya ilahi mai niya
Ga ni na]au anniya
Ba ni bu]i in iya
Garga]i kan duniya.

2 Don Nabiyuka Hamidu
Shugabanmu Muhammadu
Annabinmu Muhammadu
Wanda shi ne sayyidu
Gun halitta bai]aya.
(A}ilu Aliyu: *Duniya rawar 'yanmata*)

Nau'i na biyu na amsa-amon farawa shi ne a inda mawa}i ya za~i sautin da yake so ya kawo a matsayin babban amsa-amonsa ya kawo shi a ga~ar farko na baitin farko na wa}arsa kamar haka:

1 Kafilun, ishi bayinka
Ka ishe ni da girmanka
Ka fa]i na kiraye ka
Ka ji na fa]i sunanka
Kai da kaya duk naka.

2 Rabbana, ka yi min bu]i,
Nai nufin wani]an ta]i,
Wanda babu ciki mur]i,
Damina in ta fa]i,
Duk mu ka san albarka.
(A}ilu Aliyu: *Damina mai albarka*)

Wannan tsari na amsa- amon farawa tsari ne mai matu}ar birgewa da nuna tsantsar hikima da basira da kuma }warewar marubucin wa}a, haka kuma wannan tsari na nuna baiwar da harshen Hausa ke da ita na jujjuya sautika yadda mutum ke bu}ata kuma a sami cikakkiyar ma'ana a wa}a.

Amsa-amon Karin sauti: na nufin hawa da sauka na murya a ga~ar }arshe na kowane baitin wa}a ko]iyan wa}a (a wa}ar baka). Ana samun wannan nau'in amsa – amo ne

a rubutacciyar wa}a da wa}ar baka. Manazarta rubutattun wa}o}in Hausa ba su cika nazarin wannan nau'in amsa-amo ba saboda ba shi cikin matakan nazarin rubutattun wa}o}in larabci wanda daga su ne aka sami na Hausa. An fi amfani da wannan amsa-amo wajen nazarin karin wa}o}in baka na Hausa inda masana suka gano cewa kowace wa}a na da amsa-amon karin sauti guda]aya da wa}ar ke }arewa da shi.

4.2 Kari

Kari na]aya daga cikin abubuwan da ake amfani da su wajen tsara wa}ar Hausa. Kari na nufin raujin da murya kan yi yayin rera wa}a. Kari ne ya bambanta wa}a da magana ta yau da kullun.

Karin wa}a ya shafi sauti ne da tsarinsa da kuma yadda ake sarrafa shi a cikin wa}a. Karin wa}a ya shafi nazarin arulin wa}a inda ake nazarin ga~o~in wa}a da }afafuwan wa}a da kuma abubuwan da kan wakana a wa]annan }afafuwa su haifar da sauyi (kamar zihafi da sakiya).

Ana nazarin karin rubutacciyar wa}ar Hausa ne ta amfani da karuruwan wa}o}in Larabci, wannan kuwa ya faru ne saboda rubutattun wa}o}in Hausa sun samo asali ne daga rubutattun wa}o}in Larabci, kuma tsarin ga~o~in kalmomin Hausa iri]aya ne da na Larabci, wato kamar yadda a Hausa ake da tsarin ga~a nannauya da sakayau, haka ma ga~o~in Larabci ke zuwa da nannauyar ga~a da kuma sakayau.

Rubutattun wa}o}in Hausa na amfani da karuruwa goma sha hu]u da ta aro daga cikin karuruwa sha shidda da ake amfani da su a rubutattun wa}o}in Larabci wa]anda ake samu daga ha]uwar }afafuwa goma wa]anda suka ha]a da:

Fa'uulun	0 00 00	(}afa ta]aya),
Mafaa'ilun	0 00 00 00	(}afa ta biyu),
Mafaa'alatun	0 00 0 0 00	(}afa ta uku),
Faa'ilaatun	00 0 00 00	(}afa ta hu]u)
Faa'ilun	00 0 00	(}afa ta biyar)
Mustaf'ilun	00 0 00 00	(}afa ta shida)
Faa'ilatun	00 0 00 00	(}afa ta bakwai)
Mutafaa'ilun	0 0 00 0 00	(}afa ta takwas)
Maf'ulaatu	00 0 00 0	(}afa ta tara)
Mustaf'ilun	00 00 0 00	(}afa ta goma)

Wa]annan su ne }afafuwa goma wa]anda kan zo da wa]annan alamomi da aka gani wa]anda ta hanyarsu ne ake samun karin wa}a, wato sukan fito a wa}a su maimaita kansu su samar da kari ko kuma wata }afa ta ha]u da wata ta samar da kari. Karuruwan da akan samu daga wa]annan }afafuwa a rubutattun wa}o}in Hausa sun ha]a da:

1- Muta}arab 2- [awil

3- Hazaj	4- Wafir
5- Mutadarak	6- Rajaz
7- Basi]	8- Munsarih
9- Ramal	10- Madid
11- Hafif	12- Kamil
13-Mu}talib	14- Mujtass
15- Sari’	16- Mudari’

Mata marubuta wa}o}in wa’azi na amfani da wannan tsari na }afafuwan Larabci domin su samar da kari a wa}o}insu, misali a wa}ar Ri}on amana ta Raihantu Usman an sami karin (Kaamil) na goma sha biyu ya fito a wa}ar inda aka sami }afa ta takwas (mustaf’ilun) ta maimaita kanta a wa}ar kamar haka:

\- - v - - - v - -

Ya Rabbi na ro}e ka Allah,
v - - - v v - v - -
Ka taimake ni na bar kasala,
- - v - - v - - - -
Zan yo nasiha ga masu daula,
v - v - - v - v - -
Maza da mata mu bar dalala,
v - v - v v – v - -
Mui }o}ari mu ri}e amana.

A wannan baiti, an nuna yadda }afa ta takwas ta maimaita kanta ta samar da kari mai suna Kaamil, sai dai an sami illa da ke ratsa kafa ta takwas mai suna ilmari.

Bayan haka, akan sami wasu marubuta da ba su amfani da tsayayyen kari a wa}o}insu sakamakon }arancin ilimin tsara wa}a ko kuma rashin sanin yadda karuruwan suke, kamar yadda Hajiya ‘Yar Shehu ta bayyana wa Mack, (1985) a hirar da ta yi da ita kamar haka:

> Wasu marubuta ba su yi wa wa}arsu kari, don haka sai a sami irin wa]annan wa}o}i suna }arewa ba tare da tsayayyen kari ba, amma duk da haka ba a cewa wa}ar ba rubutacciya ba ce. Abin da ke haifar da irin wannnan shi ne rashin ilimin rubuta wa}a da ke damun wasu daga cikin marubutan. (Mack, B.B. (1985: 39)

Ha}i}a an sami irin wannan matsala a wa}o}in da aka nazarta, domin an sami wa}o}in da suka }are ba tare da tsayayyen kari ba kamar haka:

\- - v - - v - - v v - - -
Bismilla na fara wa}a ta da Allahu
v v - v- - v - - - v - - -
A cikin sifofin ta’ala har akwai ilmu.

v – v – v v - - v - v - -
Ina salati ga Manzonmu mai falala,
\- v - - v - - v - - v - - -
Mun ji an ce fa shi ne Madinatul ilmu

(wa}ar Ilimi ta Hassana Sufi)

v - - - - - - - -
Da sunan Allah nai niyya
\- - - - v v - v v -
Wa}a zan yo ta a kan ilimi.
\- - v v - - - - - -

Tsira da aminci kan]aha,

- - v v - v v v - v -

Manzonmu Muhammadu maso ilmi

(wa}ar Ilimi ta Shema'u Abdullahi)

Idan aka yi la'akari da misalan baitukan da aka kawo daga wa]annan wa}o}i, za a lura cewa wa}o}in ba su]auke da tsayayyen kari daga karuruwan larabci da ake amfani da su a Hausa.

4.3 Salon Sarrafa Harshen Wa}o}in:

Masu iya magana sukan ce "Salo asirin wa}a." Salo a nazarin adabi na nufin dabarun jawo hankali da marubuta ke amfani da shi domin }awatar da wa}o}insu. Wa}a ba salon sarrafa harshe tamkar miya ce ba gishiri.

Masana da dama sun tofa albarkacin bakinsu dangane da ma'anar salo, irin wa]annan masana sun ha]a da Bargery (1934) da Abraham (1962) da Yahya (2001) da {amusun Hausa (2006) da [angambo (2007) da sauransu.

Bargery (1934: 891) ya ce salo na nufin sabon yayi ko sabon launi ko yanayin rawa ko wayau da sauransu.

Abraham (1962:772) ya bayar da ma’anar salo ta ~angare biyu, ~angare na farko na nufin }ir}iro hanyar yin wani abu ko yanayin wani abu. |angare na biyu kuma na da ma’anar dabara ko fasaha ko wayo ko gwaninta.

Shi kuwa Yahya (2001) cewa ya yi salo na nufin dabara ko hanya mai yin kwalliya ga abu domin abin ya kwarzanta ko ya bayyana. Haka kuma, ya ci gaba da cewa, salo a wa}a na nufin duk wata dabara ko hanya a cikin wa}a wadda aka bi domin isar da sa}o. ita wannan irin hanya na yi wa wa}a kwalliya ta yadda sa}on wa}ar zai isa ga mai saurare ko karatu.

{amusun Hausa (2006:385) ya bayyana salo da cewa shi ne yayi ko sauyi ko launi ko fice.

[angambo (2007) ya bayyana ma’anar salo da cewa shi ne hanyoyi ko dabarun isar da sa}o. Haka kuma ya }ara da cewa salo wani yanayi ne da ya }unshi za~i cikin rubutu ko furuci.

4.3.1 Ire-iren Salon da Ake Samu a Wa}a

Akwai nau’o’in salo guda biyar da a mafi yawan lokaci ake samu musamman a rubutacciyar wa}ar Hausa. Irin wa]annan salo sun ha]a da:

Mi}a}}en salo: wannan nau’in salo ne da ke isar da sa}o kai tsaye cikin sau}i,

ba }a}ale bare a wahalar da mai karatu ko saurare.

Salo mai karsashi/mai armashi: wannan na'in salo ne da mawa}a ke amfani da shi a wa}o}insu don nuna birgewa da }warewa da na}altar harshen da suke wa}ar. Mafi yawan lokaci akan sami }arangiya da adon harshe da dama a irin wannan salon.

Raggon salo: shi ne a inda aka sami mawa}i ya yi amfani da salo mara gamsarwa a wa}arsa.

Salo mai tsauri: wannan nau'in salo ne mai wuyar fahimta ga makaranci ko mai saurare haka kuma irin wannan salo yana da wahalarwa da wuyar ganewa wani lokaci ma yakan sa a kasa fahimtar sa}on wa}ar.

Wa]annan su ne wasu daga cikin nau'o'in salo da suka yi fice a rubutattun wa}o}in Hausa. Daga cikin wa]annan nau'o'in salo, mata marubuta wa}o}in wa'azi sun fi amfani da mi}a}}en salo a wa}o}insu, wannan kuwa bai rasa nasaba da sa}on da suke isarwa ga jama'a (wa'azi), domin su masu nasiha ne, ba sa nufin su nuna birgewa ko iya wasa da harshe, illa dai sukan yi amfani da wasu 'yan dabaru na cikin salo da za su taimaka masu wajen samun sau}in isar da sa}onsu ga jama'a. wa]annan dabaru sun ha]a da:

4.3.2 Tubulan Ginin Salo

Siffantawa: wannan na]aya daga cikin tubulan ginin salon sarrafa harshe wanda ke siffanta abu a zuciyar mai karanta wa}a ko mai saurare.

Yahya (2001) ya bayar da ma'anar siffantawa kamar haka:

> Salon siffantawa faffa]an salo ne da ya tara surori ko sifofin da mawa}i ke bu}atar mai karatu ko sauraren wa}arsa ya kalle shi da idon zuciyarsa ko saurarensa; salon siffantawa hoto ne da kalmomi suka kawo da ma'anoninsu.

Har wa yau, marubucin ya bayyana cewa nau'in salon siffantawa ya kasu gida biyu kamar haka:

Kamance: shi ne nau'i na biyu na siffantawa. Kamance na samuwa ne a inda aka bayyana siffar wani abu ta hanyar kwatanta shi da wani abun daban, a nan ana amfani da wasu kalmomi da ke nuna kamanci, irinsu; kamar, awa, i, ya, daidai da, wuce zarce gota]ara da sauransu. Misali:

Da sahabai masu girma *sadatul ilmu*

A wa}ar ilimi ta Hassana Ahmad Sufi ta yi amfani da wannan salo kamar haka:

32 Ya ~ata iliminsa kan abu }an}ani kaito
Abin da ba zai da]e ba a gunsa da daumu.

33 *Kamar* ya shafa farar }asa a]akinsa,
Kuma sai ya hura haya}i ka ji mai ilmu.

A baiti na talatin da uku mawa}iyar ta yi amfani da *Kamar* wadda kalma ce ta siffantawa ta hanyar kamance.

Haka ita ma Shema'u Abdullahi ta yi amfani da wannan salo a wa}arta ta ilimi kamar haka:

8 In ka yi ku]inka *ya* {aruna

Ba ka daraja sai kai ilimi.

25 Ilimi da yawa *ya* ruwan kogi,
Yo nin}aya a cikin ilimi.

A wa]annan misalai mun ga yadda mawa}iyar ta yi amfani da kamance na *ya,* a wa]annan baituka don kwatanta ku]in mutum da na shahararren mai ku]in da aka ta~a yi a duniya wato {aruna, haka kuma ta yi amfani da *ya,* wajen kwatanta yawan ilimi wato kamar ruwan kogi yake (wanda bai da iyaka ga ganin idon mutum).

Jinsintarwa: Yana]aya daga cikin tubulan ginin salo inda ake]aukar wata daraja ko]abi'a ko hallayya ta abu a ba wani abin da ake magana a kansa. Akan sami jinsintarwa iri uku kamar haka:

Mutuntarwa: Ana samunta a inda aka]auki hali ko daraja ko]abi'a ta mutum aka ba wani abu wanda ba mutum ba. Misali a]auki hali na mutum kamar magana ko tafiya a ba rana ko duniya ko wani abu makamancin haka, misali a wa}ar Ri}on Amana ta Raihanatu Usman ta yi amfani da wannan salo kamar haka:

16 Kun san hukuma *uwa uba* ne,
Kowa tana so yay sukuni,
Domin hakan nan ta sanya tsani,
Maza sa mata mu san sukuni,
Sannan mu tsai da ri}on amana.

17 Hukuma Allah ya *taimake ki,*
Tsarin da *kinka* yi *kin* yi aiki,
Don ko ina kin sanya burki,

Domin mutane su gyara aiki,
Har ma fa *kin* hana cin amana.

18 *Kin* ansa al}awari ga Allah,
Don haka ba *kya* yin kasala,
Dukkan wurare masu illa,
Kin bincika har *kin* yi jimla,
Gyaran mutane har mazauna.

19 Al}arya ce ko fa }auye,
Duk makarantu don su waye,
Ga asibitoci don su warke,
Kin yo rijiyoyi dan ki janye,
Halin }azanta sannu *Inna*.

A nan mawa}iyar ta]auki wata daraja ta mutum (musamman mace) ta ba hukuma.

Dabbantarwa: shi ma yana]aya daga cikin salon jinsintarwa inda ake]aukar wani hali ko]abi'a ko daraja ta dabba a ba mutum. misali a wa}ar *Zamani* ta Hajiya 'Yar Shehu ta yi amfani da wannan salon kamar haka:

16 Domin fa]ar Rabbi ne ku an ka ba *kiwo*
Daidai muke da makafi wa]anda ba su gani.

A nan an sami salon dabbantarwa inda aka]auki]abi'a ta dabba aka ba mutum, wato dabba ita aka san ana kiwo a zahiri ba mutum ba.

Abuntarwa: Hanya ce da ake amfani da wani hali ko]abi'a ko daraja ta wani abu mara rai a ba abu mai rai musamman ma mutum. ana iya amfani da wannan salo wajen nuna kyawawa ko munanan]abi'u na mutum, misali a wa}ar Zamani ta Hajiya 'Yar Shehu ta yi amfani da wannan salo kamar haka:

10 Kan tituna kwararo lungu da banzaye

Ya kai shararai *gumakai* babu imani.

A nan marubuciyar ta]auki mummunar sifar nan ta gumaka (kowa ya san gumki wani abu ne mara rai da ke aje wuri]aya gingirim) ta kwatanta mummunar halayyar mutanen da ke neman mata musamman matan aure.

Alamci: Hanya ce da ake amfani da wata kalma domin bayyana wani abu ta hanyar ba ta wata alama ko suna da zai tsaya a maimakonsa, misali Kalmar lahira a kira ta da gobe ko kalmar sarauta a kira ta da rawani da dai sauransu. Hassana Sufi ta yi amfani da wannan salo a wannan baitin kamar haka:

57 Allah ya saka musu }warai da alheri,
Ya sa a gobe su zan mazauna gidan Na'amu

A nan mawa}iyar ta yi amfani da kalmar gobe wajen alamta kalmar lahira.

Har wa yau, an sami alamci ko alamtarwa a wannan wa}a ta Hassana Sufi kamar haka:

83 Allah dasa mana bishiyar ilmu amina,
'Ya'yanta su yi ta zuba a Nijeriyar tamu.

Adon harshe: A nan marubuci na amfani da abubuwa irin su }arangiya da sa~i-zarce da amsa kama da aron harshe da karin magana da gugar zana da sauransu.

{arangiya: hanya ce ta luguden kalmomi ko casar kalmomi a cikin wa}a, wato marubuta na amfani da wannan salo ne wajen maimaita wasu sautika a cikin baitin wa}a wanda zai haifar da wani ado na musamman ga wannan baiti har ma ga wa}a baki]aya. Misali, a wa}ar Zamani ta Shema'u Abdullahi ta yi amfani da wannan salo

kamar haka:

23 Second guda }iftawa
Shi ~al~alin ~allawa
Shi wal}iyar wul}awa
Tsawon ciki sa }ifce.

A wannan baiti an sami maiman sautin /~/ da sautin/ l/ da kuma sauti /w/ wanda ya haifar da }arangiya a baitin.

Sa~i-zarce: A nan in mawa}i ya]auko wata magana a baiti sai bai kammala ta ba a wannan baitin sai a baiti na gaba, shi ake kira da sa~i-zarce. Misali a wa}ar Raihanatu Usman ta Ri}on amana ta yi amfani da salon sa~i-zarce kamar haka:

33 Mata ku karka]e kunnuwanku
Ku gyara salla kui ta kanku
Ku ka ma aure ban da shakku
Ku tsarkake kuma zuciyarku
Allah ya sa mu ri}e amana.

34 Ta mijinmu har da ta ‘yan uwansa
Na nisa kusanci kar mu }osa
Idan yana da uwa mu gaisa
A waje na taimako kar mu }osa
Mu ri}e fa al}awarin fa amana.

A nan in an lura za a ga akwai ala}a tsakanin wa]annan baitukan, wato sauran sa}on na farko (B-33) na }unshe ne a cikin baiti na biyun (B-34). Har wa yau, an sami salon sa~i- zarce a wa}ar Ilimi ta Hassana Sufi, kamar haka:

74 Zubairu har abu Ubaidata namu,
Da Abdulrahamanu su ne wa]anda Manzonmu.

75 Yai musu albishir da gida na Aljanna,
Tun suna duniya, to kun ji manyanmu.

Kamar yadda aka yi bayanin yadda ake samun sa~i-zarce, nan ma mun ga yadda aka]auko magana tiryan-tiryan a baiti na saba'in da hu]u amma sai a baiti na saba'in da biyar aka ida ta.

Karin magana: marubuta kan yi amfani da karin magana a wa}o}insu don ta taimaka musu wajen isar da sa}o da kuma nuna }warewa a harshe, misali: a wa}ar *kishi* ta Ru}ayyatu Sabuwa Nasir, ta yi amfani da karin magana kamar haka:

29 Duk a bar su kada a ~ace,
A tuna dai kar a mance,
Duk abin da mutum ya shifce,
To yana nan fa rubuce,
Ran gamommu da gaskiya.

A nan mawa}iyar ta yi amfani da karin maganar nan da ake cewa "Duk abin da mutum ya shuka, shi zai girba, wato duk abin da ka yi shi za ka tarar a kowane lokaci. Kuma baya ga karin magana, akwai salon alamci a wannan baiti, inda ta ce "Duk abin da mutum ya shifce" wato an alamta aikin mutum da shifce.

Salon Hira wannan nau'in salon a]aya daga cikin dabarun da mata marubuta wa}o}in wa'azi na }arni na ashirin suka yi amfani da shi a wa}o}insu. An riski wannan salo ne a wa}ar Hassana Sufi ta "Ilimi," inda ta kawo hira tsakanin hankali

(a}lu) da kuma ilimi (ilmu) kamar haka:

20. Wata rana da ilmu da a}alu an yi ‘yar hira,
Wa ye mafi]aukakarsu a}alu ko Ilmu.

21. Ilimi ya ce ni na fika hankali ya cane,
Na fi ka domin da ni aka san shi Allahu.

22 Ilimi ya ce ni na fi domin da ni a cikin
}irgar sifofin Ta’ala kun ji dai Ilmu.

23. Sai hankali ya bi ya sauwa ilmu fifiko,
Nan suka }ulla abota hankali ilmu.

Aron harshe wannan na samuwa ne a yayin da marubuci ya aro wasu kalmomi daga wasu harsuna domin burgewa ko kuma domin lalura (a inda in ba wannan kalmar suka sa ba wa}ar za ta kare). Mafi yawa daga marubuta wa}o}in addini na yin aro ne daga larabci wani lokacin ma har daga harshen Turanci ko Yarbanci ko Filatanci da sauransu.

Wa]annan wa}o}i da aka nazarta a wannan aikin cike suke da aron harshe daga larabci, kuma akwai wasu ‘yan tsiraru da suka yo aro daga harshen turanci. Misalin aron harshe a harshen Larabci a wa]annan wa}o}i sun ha]a da:

3 *Wa’alihi wasahabinsa*
Kaza mutane masu son sa….
(wa}ar Ri}on amana ta Raihanatu Usman).

1 *Bismillahi Kabiri,*
Nai yabon Allah *}adiri*,
Assami’u gwani basiri,
Assataru Asshakuru

Godiyar mu gaba]aya.

2 Kai ka cancance ra nuru
Alimun ma fis suduru,
Ahasun fardun Gafuru,
La sharikalaha Habniru
Mahaliccin kulliya. (wa}ar Kishi ta Ru}ayyatu S. Nasir).

28 *Ya malikal malakutu*
Kai ne ka yo ya}utu… (wa}ar Zamani ta Shema'u Abdullahi).

Wa]annan kalmomi da aka yi wa alamar tafiyar tsutsa sune ka]an daga cikin]imbin aron harshen da aka samu daga harshen larabci a wa]annan wa}o}i.

Haka kuma akwai]imbin kalmomin larabci wa]anda za mu iya kiransu da kalmomin fannu wa]anda in dai a wa}a ta addini ce to lalle tabbas za a same su bare kuma a wa}a ta wa'azi. Irin wa]annan kalmomi da suka ratsa wa]annan wa}o}I sun ha]a da:

Bismilla (Farawa da sunan Allah)

Jalla (Sunan Allah)

Shahada (Amincewa)

Ibada (bauta wa Allah)

Idda (}ayyadaddun watanni da bazawara kan yi kafin ta }ara aure)

Hisabi (hukuncin ranar lahira)

Kitabi (littafi)

Gaibi (~oyayyen abu da ba a iya gani)

Du’a’i (addu’a)

Khairi (alheri)

{adiri (sunan Allah)

Rabbu (sunan Allah)

Ilmu (ilimi)

A}alu (hankali)

Furu’a (hukunce-hukuncen addini)

Faralu (wajibi)

Wa]annan su ne ka]an daga kalmomin Larabcin da aka tsinto daga wa]annan wa}o}i da aka nazarta a cikin wannan aiki.

Har wa yau, an sami kalmomin aro daga turanci wanda marubutan suka aro domin su nuna cewa su ma sun ratso zamanin ilimin boko har ma sun]an ta~a ilimin daidai gwargwado. Misali a wa}ar Shema’u Abdullahi ta “Zamani” an sami kalmomin aro daga turanci kamar haka:

23 *Second* guda }iftawa
Shi ~al~alin ~allawa
Shi wal}iyar wul}awa
Tsawon ciki sa }ifce.

Ita ma Raihanatu Usman ta yi aron kalmomi a Turanci, a wa}arta ta Ri}on Amana:

22- Al}ali har lauya ku gyara,

Soja da *Police* duk ku lura,
Aikinku na matu}ar lalura,
Ku yi hattara fa saboda nera,
Don kar ku zam maciya amana

Ga ka]an daga cikin kalmomin aro na turanci da aka riska daga wa]annan wa}o}i da aka nazarta:

Training	(horo)
Office	(ofis)
Police	(]ansanda)
Solder	(soja)
Lawyer	(lauyer)
Doctor	(likita)
Welder	(walda)
London	(Landan)
Machine	(masin)
Second	(da}i}a)

Wa]annan nau'o'in salo su ne dabarun jawo hankali da mata marubuta wa}o}in wa'azi suka yi amfani da su a wa}o}insu don nuna na}altar harsunan da suke wa}ar da su da kuma }o}arin tafiya daidai da zamani musamman a fagen marubuta wa}o}i.

4.4 Na]ewa

Wannan babi ya yi nazari ne da sharhi a kan jigo da tsari da kuma salon sarrafa harshe a rubutattun wa}o}in mata na wa'azi daga }arni na ashirin zuwa yau. An za~i wa}o}i takwas daga cikin wa}o}in da aka tattara, wa]annan wa}o}i sun ha]a da:

Wa}ar Ilimi ta Hassana Ahmed Sufi

Wa}ar Ilimi ta Shema'u Abdullahi

Wa}ar Ri}on Amana ta Raihanatu Usman

Wa}ar Ri}on Amana ta Amina Muhammadu Anda

Wa}ar Zamani ta Hajiya 'Yar Shehu

Wa}ar Zamani ta Shema'u Abdullahi

Wa}ar Lullu~i ta Hauwa Gwaram

Wa}ar Kishi ta Ru}ayyatu Sabuwa Nasir.

Har wa yau, an nazarci wa}o}in da suka fi shafar nasiha a kan mata don ganin yadda marubutan suka ba da gudummawarsu wajen gyara tarbiyyar mata 'yan uwansu, domin Hausawa kan ce "ciwon 'ya mace na mace ne."

Babi na Biyar: Kammalawa

5.0 Shimfi]a

Wannan babi shi ne babin kammalawa a wannan aiki, wato shi ne babin da aka na]e tabarmar wannan bincike, wannan ya nuna cewa “komai ya yi farko, to yana da }arshe ban da ikon Allah. Don haka, wannan babi ya }unshi waiwaye a kan abin da aka gudanar a wannan aiki tare da kawo ka]an daga cikin sakamakon abin da aikin ya samu, haka kuma za a bayar da shawarwarin da suka dace wajen gudanar da bincike irin wannan.

5.1 Na]ewa

Za a na]e wannan aiki mai taken “Wa’azi a Rubutattun Wa}o}in mata na Wa’azi daga }arni na ashirin ta hanyar waiwayar irin abin da aka gabatar a aikin, wato za a kawo abin da aikin ya }unsa a ta}aice.

Wannan aiki ya faro ne da hasashe da aka yi cewa mata na rubuta wa}o}i kuma daga cikin wa}o}in da suke rubutawa akwai wa}o}i na wa’azi. Dama an san cewa a baya (}arni na sha tara) an sami mata da suka rubuta wa}o}i na addini wa]anda a ciki akwai na wa’azi, domin haka sai aka yi tunanin shin mata sun ci gaba da wannan }o}ari ko kuwa sun bar ma maza (wa]anda dama kowa ya san shahararsu a

wannan fage). Domin gano amsar wannan tambaya ne ya sa aka }uduri niyyar gudanar da wannan aiki. Bayan niyyar da aka yi ta yin aikin, sai wasu tambayoyi suka ci gaba da karakaina a kan mai gudanar da wannan bincike, irin wa]annan tambayoyi kuwa sun ha]a da:

Mene ne matsayin mata a }asar nan, (a da da yanzu)?

Shin har yanzu ana samun mata marubuta wa}o}i?

In ana samu, a kan me suke rubuta wa}o}in nasu?

A wane wuri suke zaune?

Yaya suke ya]a wa]annan wa}o}i in sun rubuta?

Shin suna }o}arin shiga }ungiyoyin marubuta wa}o}i?

Wa]anne irin matsaloli ne suka tarna}e wa]annan mata da har ba a jin]uriyarsu sosai?

Wa]anne irin jigogin wa'azi matan suka fi damuwa da su a wa}o}insu?

Wa]anne irin salailai ne mata ke amfani da su wajen rubuta wa}o}insu na wa'azi?

A }o}arin samun amsar irin wa]annan tambayoyi da makamantansu ne Allah ya sa aka kai ga cimma nasarar kammala wannan aiki. Sai dai kafin a fara aikin an fara ne da nazarin ayyukan da suka gabaci wannan aiki wa]anda aka gudanar musamman a kan rubutacciyar wa}a da kuma kan mata. A wannan ~angare ne aka nazarci ayyukan da aka tattaro na matakan neman takardun shaidar digiri tun daga na farko da na biyu har zuwa na uku. Haka kuma, an nazarci litattafan da aka wallafa masu ala}a da

wannan aiki, wato litattafan da suka shafi nazarin wa}a da wa]anda aka wallafa a kan abin da ya shafi mata da makamantansu. Har wa yau, aikin ya tattaro mujallu da mu}alu da }asidu masu ala}a da wannan aiki tare da gudanar da kyakkyawan nazari a kansu. Duk an yi wannan ne domin samun abin da za a yi guzuri da shi na daga bayanan masana da malamai da manazarta, ta yadda za a gane yadda za a fuskantar da al}iblar aikin.

An gudanar da shimfi]a ga wannan aiki ta hanyar kawo manufar aikin da dalilin gudanar da aikin da muhimmancin aikin da hanyoyin da aka a gudanar da aikin har ma ta iyakacin aikin. Daga nan kuma, sai aka juya kan nazarin matsayin mata a }asar Hausa da kuma nazarin irin gudummawarsu a fagen rubutattun wa}o}in Hausa. Daga nan sai aka kawo ta}aitaccen tarihin mata marubuta wa}o}in wa'azi a }asar Hausa (musamman ma wa]anda aka za~i wa}o}insu domin yin nazari).

Bayan haka, aikin ya nazarci jigogin wa}o}in mata na wa'azi a babi na uku. An za~i wa}o}i takwas domin nazarin jigonsu, an sami biyu masu jigon ilimi sai wasu biyun masu jigon ri}on amana sai kuma wa}o}i biyu a kan zamani amma suna]auke da mabambantan jigogi, sai wata wa}ar a kan jigon lullu~i ga mata da kuma mai]auke da jigo kan illar kishi musamman ga mata.

A babi na hu]u aka nazarci tsari da salon sarrafa harshen wa}o}in. an yi sharhi kan mabu]i da marfin da mawa}an suka yi amfani da su a wa}o}insu da kuma yawan

baitukan kowace wa}a da tsarin kowane baiti na kowace wa}a da amsa-amon wa}o}in da yanayin ginin baitukan wa}o}in da sauransu. Har wa yau, an nazarci salon da matan ke amfani da shi a wa}o}insu inda aka lura cewa matan sun fi amfani da mi}a}}en salo wajen rubuta wa}o}in nasu, saboda salo ne da ke da sau}in isar da sa}o ga jama'a. Ba a nan aka tsaya ba a nazarin salo, har ma sai da aka kawo tubulan ginin salon sarrafa harshen wa}o}in nasu, irin wa]annan tubula sun ha]a da siffantawa inda ake amfani da kinaya da kamance wajen siffantawa, sai kuma salon jinsintarwa inda suke jinsitarwa ta hanyar mutumtarwa da kuma ta hanyar dabbantarwa da ta hanyar abuntarwa, an nuna haka ne ta hanyar kawo misalai daga baituka na wa}o}in. Har wa yau, an kawo salon alamci da adon harshe inda aka sami }arangiya da sa~i-zarce da aron harshe da kalmomin fannu da karin magana da sauran nau'o'in adon harshe.

Daga }arshe, an na]e tabarmar wannan aiki ne a babi na biyar, inda babin ke]auke da kammalawa da yin waiwaye a kan dukkan abin da aikin ya }unsa a ta}aice. sa'annan an kawo shawarwari na musamman ga marubuta da manazarta wa}o}in Hausa a kan abubuwan da ke cewa wannan fanni tuwo a }warya domin ganin an inganta rubuce-rubuce da kuma inganta nazarin rubutattun wa}o}i tare da amfana da falsafar da ke cikin wa}o}in. An kawo jerin manazartar da aka yi amfani da ita wajen gudanar da aikin da kuma ratayen wa}o}in da aka nazarta.

5.2 Shawarwari

Bisa la'akari da wannan bincike da aka gudanar, shawarwarin da zan bayar za su kasance ne ga marubuta wa}o}in Hausa da manazarta wa}o}in Hausa da kuma makarantun da ake nazarin Hausa a kowane irin mataki.

Da farko dai zan fara da marubuta wa}o}in, domin sai sun rubuta masu nazari za su sami abin nazari. Marubuta wa}o}i maza da mata ku sani cewa Allah ya yi maku baiwa da wani abu daga cikin baiwar da yake wa za~a~~un bayinsa wato hikima da basirar iya rubuta wa}a. sanin kowa ne cewa tsara wa}a baiwa ce daga Allah, domin haka ku yi amfani da wannan baiwar a inda ta dace, wato ku yi amfani da basirar da Allah ya ba ku wajen rubuta wa}o}i masu ma'ana wa]anda za su amfani al'umma da ma wasu al'ummomi masu zuwa, kamar yadda har yanzu ake amfani da basirar marubuta wa}o}in }arni na sha tara, wa]anda suka]auki wa}a a matsayin hanyar koyar da mutane ibada da kuma yadda za su bauta wa Ubangiji ma]aukakin Sarki. Haka kuma, ku zamo masu koyi da marubuta masu kishin kai da kishin jama'a da kishin }asa irinsu Sarkin Musulmi Attahirun Amadu wanda sarki ne amma ya yi amfani da basirarsa ya rubuta wa}a domin tserar da mutanensa daga fa]awa tarkon Nasara, haka kuma ga mazan }warai irin su Sa'adu Zungur wa]anda suka]auki al}alaminsu suka zare shi ya zame masu kansakalin ya}ar abokan gaba, ba domin

komai ba sai don su tabbatar da sun tseratar da al'umma daga fa]awa cikin mulkin zalunci da cin mutuncin talaka. Har wa yau, ga manyan mawa}an }asar Hausa wa]anda }asar Hausa take cin ribar basirar da Allah ya ba su wajen rubuta wa}o}in addini da nuna kishin kai da kishin harshen Hausa da kuma kishin }asa, wannan ba kowa ba ne illa shahararren mawa}in nan wato malam A}ilu Aliyu. Haka kuma ku dubi irin]imbin gudummawar da malam Aliyu Namangi da Sarkin Zazzau Aliyu [an sidi da su malam Bello Gi]a]awa suka bayar wajen ya}in zukatan al'umma da wa}a.

Ba domin komai ba na yi wannan waiwayen sai don in haska wa marubuta wa}o}i 'yan bana-bakwai hanyar da ya kamata su bi in dai har suna neman duniya ta amfana da basirarsu kuma ya zamanto ambatonsu bai gushewa a doron }asa har sai ranar da aka na]e }asar. Ina mata marubuta wa}o}i 'yan zamani? Domin Allah ku hanga baya ku ga me ake nufi da rubuta wa}a, ku duba ayyukan baiwar Allah 'yar baiwa Nana Asma'u wadda yanzu tsawon shekaru]ari biyu kenan da ta yi zamani amma in ana ambatonta sai ka ce tana cikinmu. Ku duba irin ayyukan mata masu]a'a da sanin darajar mata irin su Hassana Sufi da Hajiya'Yar Shehu da Hauwa Gwaram da Raihanatu Usman da Amina Anda da Ru}ayyatu S. Nasir da Shema'u Abdullahi da sauransu, ku zo ku]auki aikin daga inda suka aje ku dasa kamar yadda su ma suka]auka daga wa]anda suka gabace su. Wannan ne ka]ai zai sa a ci ribar basirar da Allah ya yi muku ta rubuta wa}a kuma ya kasance kun yi kyakkyawan }arshe, wato

ku bar duniya ana ambaton kyawawan ayyukan da kuka shuka. Kar ku yarda ku yi amfani da basirarku wajen taya she]an bidiri domin kuna ji kuna gani da ranku da lafiyarku da zarar ya gama yayinku zai kwaso wasu ya watsar da ku a kwandon shara. Allah ya kiyashe mu aikin da-na-sani.

Zan karkarta akalar shawara ta zuwa ga makarantun da ake nazarin Hausa, da su zauna su dubi]imbin hikima da falsafar da ke cikin rubutattun wa}o}i, su]ebi wa}o}in nan da aka rubuta (masu ma'ana) su sa su a manhajar koyarwarsu domin]alibai su amfana da sa}onnin da ke cikin wa}o}in da kuma falsafa da salon da ke cikin wa}o}in domin ta wannan hanya ne ka]ai za a sami }aruwar masu sha'awar rubuta wa}o}i masu ma'ana. Haka kuma, ya kamata irin wa]annan makarantu musamman ma jami'o'i su dawo da al'adar nan ta tattara }ungiyoyin marubuta da manazarta wa}o}i tare da shirya musu gasa ta musamman (irin wadda ake gudanarwa a da) tare da ba su lambobin yabo da kyaututtukan da za su }ara musu }aimi da }warin }wiwar ci gaba da sha'awar abin da suke.

Har wa yau, zan waiwayi]alibai masu karanta Hausa, wajibi ne ga kowane]alibin Hausa ya iya nazarin rubutattun wa}o}in Hausa kuma wajibi ne gare shi ya san wa]annan wa}o}i saboda muhimmancinsu. Domin haka, ina shawartar]alibai da su daina tsoron kwasakwasai ko darussan wa}a wai don kawai ba su da lokacin karanta

su, ya zama wajibi gare mu da mu nemar wa kanmu lokuttan nazarin irin wa]annan wa}o}i, domin ba ka sanin harshen al'umma da tunaninsu da al'adunsu sai ta hanyar wa}o}insu. Harshen kowace al'umma na nan a wa}o}inta, domin a nan ne za ka sami tarayyar sauran nau'oin adabi kamar karin magana, kirari, habaici da gugar zana da dai sauransu. Domin haka, muhimmin abu da ke gaban kowane]alibin da ya zo karanta Hausa a kowane irin mataki shi ne ya sa wa ransa sha'awar wa]annan wa}o}i domin sai da sha'awa ne zai iya fahimtarsu har ma ya fahimci yadda ake tsara su, don haka a yi wa kai fa]a, a zauna a rungumi wa}o}i na baka da rubutattu domin a samu a fitar da jaki daga cikin duma.

Bayan haka, su ma kafafen ya]a labarai da sauran al'umma suna da rawar da za su taka a nan, kafafen ya]a labarai na iya bun}asa rubutun wa}o}i musamman ga mata ta hanyar gayyato irin wa]annan marubuta da yin hira da su da kuma]aukar wa}o}in nasu tare da yawan sa su a koda yaushe (kamar yadda ake yawaita gayyato mawa}an zamani na fim da yadda ake yawan sa wa}o}in nasu). Ya kamata a sami daidaito wajen sa wa}o}in baka da rubutattu musamman wa]anda suka shafi wa'azi da addini baki]aya. Ga sauran jama'a kuma ya kamata su ri}a sayen wa}o}in da aka wallafa masu amfani domin }ara wa marubutan }aimi na ci gaba da rubuta wa}a.

A }arshe zan yi kira ga gwamnati wadda ita ce alhakin kula da tarbiyyar al'umma

yake kanta, ya kamata gwamnati ta fito da wani shiri na musamman da zai ri}a taimakawa fasihai da sha'irai da }arfafa masu giwa a kan ayyukan rubuce-rubuce da suke na tarbiyyar al'umma, domin in dai har gwamnati za ta]auki nauyin wasanni, ba abin da zai hana ta iya]aukar nauyin abin da ya fi wasannin muhimmanci ga jama'a wato wa}o}in wa'azantarwa da gyara halayen al'umma, domin in har gwamnati ta sami al'umma ta gari to komai nata zai tafi daidai. Allah ya sa mu dace.

Manazarta

Abraham, R. C (1962) *Dictionary of the Hausa Language*. London: Hodder & Stoughton Ltd.

Abdul}adir, D. (1979), *Za~a~~un Wa}o}in Hausa na da da na Yanzu*, Lagos: Nelson.

Aliyu, A. (1977), *Fasaha Al}iliyya*. Zaria: NNPC

Al}ali, M. A. (1982), "Rayuwar Al}ali Bello Gi]a]awa Sakkwato da Wa}o}insa." Kundin Bincike Domin Neman Digirin Farko, Sakkwato: Jami'ar Usman [an Fodiyo.

Aminu, M.L (1993), "Sake Le}a Adon Harshe: Nazarin Kwalliya A Rubutattun Wa}o}in Hausa." Takardar da aka Gabatar a Taron Masana da Marubuta Wa}o}in Hausa. Zaria, Jami'ar Ahmadu Bello.

Aminu, M.L (2000), "Wa}o}in Jihadi a Goshin {arni na Ashirin da [aya" A *Mujallar Hausa Studies*, vol. II No. 2. Sakkwato, Jami'ar Usman [anfodiyo.

Aminu, M. L (2005) "Reformism as a Theme in Hausa Religio-Political Poetry" Takardar da aka Gabatar a London: S.O.A.S.

Asma'u, [. Z (2006) "Tsoratarwa a Wa}o}in Wa'azi na Nana Asma'u" Kundin Bincike Don Neman Digirin Farko, Sakkwato: Jami'ar Usmanu [anFodiyo.

Babba, U. G (Mrs) (1986), "Hajiya Hassana Sufi da Ayyukanta." Kundin Bincike Don Neman Digirin Farko, Zaria: Jami'ar Ahmadu Bello.

Balogun, I. A (1975), *The Life and Works of Uthman [an Fodio*, Lagos: Islamic Publicatin Bureau.

Bargery, G. P (1934), *A Hausa-English Dictionary & English- Hausa Vocabulary*. London: Oxford University.

Birniwa, H. A, (1981) "The Imfiraji I & IV of Aliyu Namangi" Kundin Digiri na Biyu, London: S.O.A.S.

Birnin-Tudu, S. Y (2002), "Jigo da Salon Rubutattun Wa}o}in Furu'a Na {arni Na Ashirin" Kundin Bincike Don Neman Digiri na Uku, Sakkwato: Jami'ar Usman [an Fodiyo.

Boyd, J. & Mack, B. B. (1996), "Women's Islamic Literature in Northern Nigeria: 150 Years of Tradition, 1820-1970"

Boyd, J. & Mack, B. B. (1999), *The Collected Works of Nana Asma'u.* Ibadan: Sam Bookman Publishers.

Boyd, J. (2000), *The Caliph's Sister Nana Asma'u 1793-1865: Teacher, Poet & Islamic Leader*. London

Boyd, J & Mack, B. B. (2000), *One Woman's Jihad*. Bloomington: Indiana University Press.

Boyd, J (2001), "Distance Learning From Purdah in Nineteenth-century Northern Nigeria: The Work of Asma'u Fodiyo." Journal of African Cultural Studies. Vol. 14, No. 1, Islamic Religious Poetry in Africa. Taylor & Francis Publishers Ltd.

Bugaje, U. M. (1996), " The Role of Muslim Women in the Transformation of the Nigerian Society," Bauchi: {asidar da aka Gabatar a Taron {ungiyar Mata Musulmin (Fomwan).

Bunza, A. M. (2009), *Narambaɗa,* Lagos: Ibrash Islamic Publishers.

Doi, A. I (1983), "Education For Muslim Women: A Glimpse of Our Proud Heritage" *The Muslim World League Journal* Vol 10, No. 6-7;pg 13-17.

Dunfawa, A. A.(1990), Gudummuwar Masu [ari}a Wajen Ha~aka Rubutattun Wa}o}in Hausa." Kundin Bincike Don

Neman Digiri na Biyu, Zaria: Jami'ar Ahmadu Bello.

Dunfawa, A.A (2002), "Wa}a a Tunanin Yara." Kundin Bincike Don Neman Digiri na Uku, Sakkwato: Jami'ar Usman [an Fodiyo.

Dunfawa, A.A (2003), *Ma'aunin Wa}ar Hausa*, Sokoto: Garkuwa Publishers.

[angambo, A. (1980), "Hausa Wa'azi Verse From ca. 1800-1900: A Critical Study of Form, Content Language and Style."Kundin Bincike Don Neman Digiri na Uku, London: S.O.A.S.

[angambo, A. (2007), *Daurayar Gadon Fe]e Wa}a*. Zaria: Amana Publishers.

Fafunwa, A. B. (1974), *History of Education In Nigeria*.NPS Educational Publishers, LTD.

Furniss, G. (1996), *Prose Poetry and Popular Cultures in Hausa*. London: International African Library.

Gumi, A. M ( ), *Tarjamar Ma'anoni Al'}ur'ani Mai Girma*.

Habibu, L. (2001), "Bun}asar Rubutattun Wa}o}in Hausa a {arni na Ashirin" Kundin Bincike Don Neman Digiri na Farko, Sakkwato: Jami'ar Usman [an Fodiyo.

Hajiya 'Yar Shehu & Hauwa, G. (1983), *Al}alami a Hannun Mata*, Zaria: NNPC.

Hiskett, M. (1975), *History of Hausa Islamic Verse.* London: S.O.A.S.

Hiskett, M. (1984), “The Imagery of Light and Associated Ideas in Hausa Islamic Verse’, in I.Y Yahaya and A. Rufa’i (eds)”, Studies in Hausa Language, Literature and Culture: Proceedings of the First International Hausa Comference, 1978, Kano: Jami’ar Bayero.

Jami’ar Bayero Kano (2007), *{amusun Hausa,* Cibiyar Nazarin Harsunan Nijeriya, B.U.K

Ibrahim, M.S (1982), “Rubutattun Wa}o}in Hausa Kafin Zamanin Shehu Usman [an Fodio.” *Harsunan Nijeriya* 12:93-104, Zaria: Jami’ar Ahmadu Bello.

Ibrahim, B. (Mrs), (2008), “Gudummawar mata wajen bun}asar Adabin Hausa” Kundin Bincike Don Neman Digiri na Uku, Sakkwato: Jami’ar Usman [an Fodiyo.

Ikara, A. T. (1983), “Ummaru Wazirin Gwandu da Wa}o}insa.” Kundin Bincike Don Neman Digiri na Farko, Zaria: Jami’ar Ahmadu Bello.

Isma’il, B. I. (2008),“Al}alami a Hannun Mata: Sharhi a Kan Wasu Rubutattun Wa}o}in Mata” Kundin Bincike Don Neman Digiri na Farko, Zaria: Jami’ar Ahmadu Bello.

Mack, B. B (1982), “Metaphor And Metonymy In Na’ibi Wali’s “Wa}ar Damina” (“Song of The Rains”). *Research in African Literature*. Vol. 13 No. 1, Texas University Press.

Mack, B. B (1983), “Wa}a [aya Ba Ta {are Ni}a”: One Song Will Not Finish The Grinding: Hausa Women’s Oral Literature. Contemporary African *Literature*. Ed. Hal Wylie. Washigton, D.C: Three Continent Press.

Mack, B. B (1985), “Hausa Women Poets: Ghost Writers” *Ba Shiru*

Mack, B. B (1986), “Songs From Silence: Hausa Women’s Poetry” *Ngambika: Studies of Women In African Literature.* Edited by Carole B. David And Anne A. Craves. New Jersey: Africa World Press.

Mack, B. B (2004), *Muslim Women Sing Hausa Popular Song*. Indiana University Press.

Mahadi, H (2006), *Gender and Citizenship: Hausa Women’s Political Identity From The Caliphate to the Protectorate*. (Goteborg 2006) Oxford University.

Malumfashi, A. I (1984), “Wa’azi a Rubutattun Wa}o}in {arni na Ashirin” Takardar da aka Gabatar a Taron {arawa Juna Ilimi, Sakkwato.

Muhammad, [. (1977), “ Individual Talent in The Hausa Poetic Tradition.”

Kundin Bincike Don Neman Digiri na Uku, London: S.O.A.S.

Muhammad, J. (2006) “Wa}a a Matsayin Makami na Canza [abi’un

Al’umma.” Kundin Bincike Don Neman Digiri na Farko, Sakkwato:

Jami’ar Usman [an Fodiyo.

Muhammad, S. I & Ahmad N.G (1996), “Gudummawar Marubuta

Wa}o}in Hausa ga Kyautata Tarbiyyar Mazauna Birane”

Kundin Bincike Don Neman Digiri na Farko, Sakkwato, Jami’ar Usman [an Fodiyo.

Mukhtar, I. (2006) “Gudummawar Rubutattun Wa}o}in Hausa Wajen

Adana Tarihin Siyasar Nijeriya” *Algaita* No. 4 vol. 1

Kano: Benchmark Publishers Ltd.

Neil, K. O (1988), “Changing Female Roles in Northern Nigeria: A Study of Women’s

Oral and Written Poetry

Othman, H. F. (Mrs) (1979), “ Wa}e- wa}en Matan Hausawa da

Muhallansu” Kundin Bincike Don Neman Digiri na Farko, Zaria: Jami’ar Ahmadu Bello.

ODU AL 5/18O N0. 128 iggg; Wa}o}in Raihanatu Usman.

ODU AL 5/170 N0. 124; Wa}ar Ri}on amana, Raihanatu Usman.

Sa'id, B. (1978), " Salo da Tsarin Rubutacciyar Wa}ar Hausa ta {arni na Sha Tara." Kano: Hausa Language Literature and Culture; Journal, Vol. 1.

Sufiyanu, R. A. (1999), *Martabar Mata a Musulunci*, Kaduna: DataPrints.

Suleiman, A. M. (2004), " Rahanatu Usman da wa}o}inta." Kundin Bincike Don Neman Digiri na Farko, Kano: Jami'ar Bayero.

Yakawada, M. T. (1983) "Wa}e}eniya" Kundin Bincike Don Neman Digirin Farko, Zaria: Jami'ar Ahmadu Bello.

Yakawada, M.T. (1987), "Tarkakken Matanin *Kanzil azim* ta Aliyu Namangi." Kundin Bincike Don Neman Digiri na Biyu, Zaria: Jami'ar Ahmadu Bello.

Yaro, I. M. (2008), " Nazarin rubutattun wa}o}in mata a Kano daga 1954 – 2004" Kundin Bincike Don Neman Digiri na Biyu, Kano: Jami'ar Bayero.

Yahaya, I.Y. (1988), *Hausa a Rubuce: Tarihin rubuce – rubuce cikin Hausa,* Zaria: NNPC.

Yahya, B. A. (1983) “A Critical Anthology of the Verse of Alhaji Bello Gi]a]awa” Kundin Bincike Don Neman Digiri na Biyu, Sakkwato: Jami’ar Usman [an Fodiyo.

Yahya, B. A. (2001), *Salo Asirin Wa}a* Kaduna: Fisbas Media Services.

HIRA

Hira da Shema’u Abdullahi (marubuciyar wa}o}i) ranar 25 ga wata Mayu 2009.

Hira da Amina Muhammadu Anda (marubuciyar wa}o}i) ranar 3 ga watan Agusta 2009.

Hira da malama Balbasatu Ibrahim (a Sokoto) ranar 20 ga watan Disamba 2009.

Rataye

Wa}ar *Ilimi* Ta Hassana Ahmad Sufi

1. Bismilla na fara wa}a ta da Allahu,
   A cikin sifofin Ta'ala har akwai Ilmu.

2. Ina salati ga Manzon namu mai falala,
   Mun ji an ce fa shi ne Madinatul Ilmu.

3. Da alihi masu girma haka daraja,
   Da sahabai masu girma sadatul Ilmu.

4. Ni jahila ce mara hikima mara }wazo,
   To don karambani zan yi batu a kan Ilmu.

5. Ilimi iri biyu ne tamkar da kuka sani,
   Ilimi na Addini da na zamani Ilmu.

6. To zan yi zance a kan ilimi na Addini,
   Shi ne abin a gabatar mai bi]ar Ilmu.

7. Allah Ta'ala ya ce a cikinmu bayinsa,
   Mafiya ga tsoronsa sai mafiya yawan Ilmu.

8. Manzonmu mai daraja ya ce mu nem Ilimi,
   Ko da a birni na Sinu mu je mu nem Ilmu.

9. Ya ce farilla Musulmi duk ya nemi ilimi,
   Dukan Musulma farilla ne ta nem Ilmu.

10. Ai ilmi zuma ne hakan nan malamai suka ce,
    Ilimi ado ne a ya jama'a mu nem Ilmu.

11. Ilimi da shi muka san Allah fa ya jama'a,
    Da Annabawa Ma'ika masu san Ilmu.

12. Ilimi da shi ke sanin faralu da masaminu,
Da mustahabu da makaruhu da maharumu.

13. In babu ilimi da mai aka bauta Allahu,
Ba ka san ibada ba gafilu je ka nem Ilmu.

14. Sallah alwala da wanka ya ake yinsu,
Ba za ka san yinsu ba sai ka bi]o Ilmu.

15. Da sani fa Adamu babanmu ya]aukaka ai,
A kan Mala'ikatu jama'a mu nan Ilmu.

16. Allah ya ce su yi sujudi gare shi dukansu,
Suka yi ta sai Ibilisu uban ma}i Ilmu.

17. Yai hassada ga ubanmu Adamu ya }i yi,
Allah ya la'ane shi la'ananne uban jarmu.

18. To kar mu rafkana ko mu sake da shi jama'a,
Ya zamu rafkana ko mu sake da ma}iyinmu?

19. Ko hankali sai da ilimi ne yakan cika cif,
Don hankali bai cika sai in akwai Ilmu.

20. Wata rana da ilmu da a}alu an yi 'yar hira,
Wa ye mafi]aukakarsu a}alu ko Ilmu.

21. Ilimi ya ce ni na fika hankali ya cane,
Na fi ka domin da ni aka san shi Allahu.

22. Ilimi ya ce ni na fi domin da ni a cikin
}irgar sifofin Ta'ala kun ji dai Ilmu.

23. Sai hankali ya bi ya sauwa ilmu fifiko,
Nan suka }ulla abota hankali ilmu.

24. Ilimi fa babban makami ne uban tafiya,
Tafiya da babu makami ba uba Ilmu.

25. Wa zai ji da]inta kan hanya ko ga mafashi,
Kura da zaki suna barar marar Ilmu.

26. To dan fa shi Ibilis san zuciya shi ne,
Kura ku ce zaki duniya maru]armu.

27. To ‘yan uwa sai mu ro}i Ubangiji Allah,
Ya sa mu san hairan tafiya ga uhuranmu.

28. Allah ka ba mu yawan ilimi da aiki da shi,
Ilimin da ba aikatawa ya zame zulmu.

29. Duk wanda ya nem sani domin a ce wane,
Ai ba ka ji shi yai riya mai bi]ar Ilmu.

30. Ita ko riya rushe aikin wanda yai ta take,
Mai hankali kar ka yarda, ka je ka nem Ilmu.

31. Haka wanda ya nan sani domin ya san girma,
Ko ko ya zan arziki, kaitonsa mai Ilmu.

32. Ya ~ata iliminsa kan abu }an}ani kaito,
Abin da ba zai da]e ba a gunsa ba daumu.

33. Kamar ya shafa farar }asa a]akinsa,
Kuma sai ya hura haya}i ka ji mai Ilmu.

34. Iliminsa ya zam hujja a kansa ya jama’a,
A gobe ran lahira zai sha yawan nadamu.

35. Mu dai Ta’ala muke ro}o ya ba mu sani,
Da yawa }warai kuma mui aiki da shi Ilmu.

36. Maza da mata mu tashi tsaye mu]au himma,
Manya da yara mu zan burin mu san Ilmu.

37. Ilimi yana kau da kuwa babu dai gefe,
Sai wanda bai samu yinsa ba duk mu nem Ilmu.

38. ‘Ya’ya fa ha}}insu na nan kan iyayensu,
Su sa su hanyar karatu don su san Ilmu.

39. Amma yawancinmu ba a kula da ‘yan yara,
Tun ba a ce mace ba sai ta girma ba Ilmu.

40. Sai dai a ce zo ki]au tallar ki je ki yi man,
Mu san abin hidda kunya ba batun Ilmu.

41. To in baki talla ba da idan za a sayi,
Kayan da zan kai ki]aki, ka ji matanmu.

42. Ai kya ga tasa farantai da kirin koki,
Har tangaraye a]akin wance da’awarmu.

43. Ta gantale duk ta lalace a kan titi,
Tallar da ba ta }ulla komai sai yawan jurmu.

44. Ba arziki muka samu ba a lalace,
Don |abura babu girma ga rashin Ilmu.

45. Ban ce neman halal yana da laifi ba,
Ina nufin duk abin da ake, a nan Ilmu.

46. Da dai sani muka kama za mu arzuta,
Duniya ka za lahira, maza dai mu nem Ilmu.

47. Mun cuci ‘ya’yanmu ba ma kula da su jama’a,
Wai sai mu ce ai nufin Allahu ne Ilmu.

48. Kyan [a a ce kan ya kai balaga ya san dukkan
Abin da Rabbi ya hore mu, da ya hane mu.

49. Ya girma ya san ibada yadda ake yinta,
Ha}i}anin Musulunci, ya san shi don Ilmu.

50. ‘Ya’yansa duka ya rene su da tarbiyya,
Mai kyau irin ta Musulunci a cikin Ilmu.

51. Tsufansa ka ga ibada ka ga imani,
Tsoron Ta’ala }warai domin akwai Ilmu.

52. Girman da ba ilimi girman kwabo jama’a,
Girmansa ya fa]i wanda ba zai bi]o Ilmu.

53. Tsufan da ba ilmu tsufan majadu ai ya zama,
Kai mai dabara da wayo jeka nem Ilmu.

54. Na gode Allah da iyayena da kakanni,
Da ‘yan uwana duka masu san Ilmu.

55. Ba fariya nai ba ya jama’a ku yafe ni,
Na janta ni’imar Ta’ala wanda ya wo mu.

56. Na gode Allah iyayenmu a tun fari,
Ba su bar mu haka sasakai ba said a son ilmu.

57. Allah ya saka musu }warai da alheri,
Ya sa a gobe su zan mazauna gidan Na’amu.

58. Na gode Allahu mai baiwa }warai da yawa,
Ya ban miji malami mai so a san Ilmu.

59. Ya biyan karatu fa shi ya sanar da ni ilimi,
Ya bayyanan falalar da take cikin ilmu.

60. Mai za n ice masa ne sai dai kurum in ce,
Allah ya saka masa da]aukaka kullum.

61. Ya ba shi lada }warai ya yawaita alheri,
A gare shi nan duniya har can ga Uhuranmu.

62. Allah ya ba shi gidan Aljanna mai Ni'ima,
Ya samu jin da]i kuma ga su hundamu.

63. Madara zuma ga ruwa na salsabilu duka,
Sannan giya ga Abariqu da an amu.

64. Tufar hariru ta sandiru shumfu]u da gado,
Ido da kunne ba su ji ba su ga yawan ni'amu.

65. Allah ya ba mu kusanci da shugaban bayi,
Ka za zuwa gun Ta'ala wanda ya yo mu.

66. Ni zan ta}aita ga wa}ata marar hikima,
Manyan mawa}a ku yafe wa marar Ilmu.

67. Allah ka bamu sani domin Ma'aikinka,
Muhammadunmu abin }auna da begenmu.

68. Adam Halilunka Ibrahimu kakansa,
Ubangijin Hajara kakar Ma'aikinmu.

69. Don Nuhu, Musa kalimullahi don Isa,
Da ya samu ba da Uba ba daga Maryamu.

70. To babu al'ajabi a cikin nufin Allah,
Ga Adamu ba Uba da Uwa uban namu.

71. Sune Ulil'azami haka malamai suka ce,
Tsira aminci gare su sahiban Ilmu.

72. Allah ka ba mu sani albarkacin alu,
Sahaban Ma'aikinka sune Sadatul ilmu.

73. Abubakar, Umaru, Usmana har da Ali,
Sa'adu, Sa'idu da [alhatu shugabanmu.

74. Zubairu har abu Ubaidata namu,
Da Abdulrahamanu sune wa]anda Manzonmu.

75. Yai musu albishir da gida na Aljanna,
76. Allah ka ba mu sani don shugabanmu,
Masu girma }warai 'ya'yan Ma'aikinmu.

77. {asimu kuma da Abdullahi la}abinsa,
Dahiru [ayyabu na uku Ibrahimmu.

78. Sannan da Fa]imatu shugabar mata,
Ru}ayyatu Zainabu da Ummul kulsumu.

79. Allah ka ba mu sani domin Waliyanka,
Sun fi mu sonka gami da saninka dan ilmu.

80. Ka ba mu Allah don jikan Ma'aikinka,
Alfadimiyu Tijjani ga auliya hatamu.

81. Na }are wa}a da godiya ga Allahu,
Sunanta za ni gaya muku masu san ilmu.

82. Samaratul falali inda shajaratul ilmu,
'Ya'ya na falala ku nema ga bishiyar ilmu.

83. Allah dasa mana bishiyar ilmu amina,
'Ya'yanta su yi ta zuba a Nijeriyar tamu.

84. Hassana'u 'yar Ahmadu ita tai yi ta ran jumma'a,

Almajira nake nice mai batun ilmu.

85. To malamai sai ku gafarce ni kan kuskure,
Kun san halin jahilai Allah ya yafe mu.

86. Baiti tamanin da shida na rufe wa}a,
Allah Ta’ala ina ro}o ka ban Ilmu.
Tammat.

Wa}ar *Ilimi* ta Shema'u Abdullahi

1. Da sunan Allah nai niyya,
   Wa}a zan yo ta a kan ilimi.

2. Tsira da aminci kan [aha,
   Manzonmu Muhammad maso ilimi.

3. Ya }ara sonsa da yardarsa,
   A kansu Sahabbai mazo ilimi.

4. Ya sanya karamci gun malami,
   Mai koya tafarkin yin ilimi.

5. Mai nuni da hanya gun shirya,
   Ka bi ta ka tsira a kan ilimi.

6. Ba mai iya cewa ya fi ka,
   In har fa ka tashi ka san ilimi.

7. In ka so ka hau kan mai gaba,
   Taso maza je ka ka wo ilimi.

8. In ka yi ku]inka ya {aruna,
   Ba ka daraja sai kai ilimi.

9. In ka yi sarautar]an Dauda,
   Sulaiman tashi bi]o ilimi.

10. Ko kai kyawun]an Ya'a}uba,
    Shi Yusufu, je ka bi]o ilimi.

11. Shi ko ilimin]an Bal'ama,
    Shi ba shi da }ima sai Zulmi.

12. Ilimi fa na tsoron Arrabbu,
    Shi ne manufa fa a gun ilimi.
13. Ba ka samunsa kana kwance,
    Ba ka girma sai kai ilimi.

14. Sai kai hidima, kawo tafiya,
    Ka zo ka a zaure gun ilimi.

15. Ka je makaranta don koyo,
    Da ko koyarwa a fagen ilimi.

16. In ka so ka tashi ka je Chaina,
    Domin ka bi]o shi a can ilimi.

17. Har ma Makka in kai niyya,
    Ka yo azama domin ilimi.

18. Amurka, ka je birnin London,
    Domin cigiya ga mazo ilimi.

19. Ko Indiya ma har ma Rasha,
    Ka je ka Faranshi ka san ilimi.

20. Nijeriya ma da irin namu,
    Wayewa sana'u har ilimi.

21. Domin ita ce gaba kan kowa,
    Uwa ta Afurka fagen ilimi.

22. Har ma fa Rasulu ya wo nuni,
    Kowa fa ya tashi ya san ilimi.

23. Farilla ne shi kan namiji,
    Har ma mace je ki bi]o ilimi.

24. Ilimi ko yana fa da fannoni,
    Wanda ba su iyaka al'ilimi.

25. Ilimi da yawa ya ruwan kogi,
Yo nin}aya a cikin ilimi.

26. Fanni na furu'a kan farko,
Shi ne na ibada uwar ilimi.

27. Sallah, azumi har ma Zakka,
Har Hajji ka je ka cikin ilimi.

28. Shi tauhidi ba ya samo
Sai an bi tafarkin yin ilimi.

29. Don ita bautar Allah ku sani,
Ba a yi sai fa a kan ilimi.

30. Ba a kwaikwayo fa da yin bauta,
Sai an yi bi]ar neman ilimi.

31. Farilla sunna mun san su,
Da mustahabi a cikin ilimi.

32. Makaruhi ba a sani shi ma,
Bare fa haram, sai an ilimi.

33. Ilimi na sanin Al}ur'ani,
Gami da Hadisi uban ilimi.

34. Sana'a ma neman sa'a,
Ba a katari sai an ilimi.

35. Har ma ciniki da irin nashi,
Fannoni duk fa cikin ilimi.

36. Shi ma]inki ya zuwa }ira,
Ba a yinsu sai an ilimi.

37. Har dukanci ya zuwa jima,
Ba sa yiwuwa in ba ilimi.

38. Sa}a da rini in ka so yi,
Je kai koyi da mazo ilimi.

39. Injiniya na da irin nasa,
Fannoni duk fa cikin ilimi.

40. Gyaran mota tu}in jirgi,
Har jan machine sai kai ilimi.

41. Shi lebura ma ba ya baya,
Don ba ka gini sai kai ilimi.

42. Yin girki ma da sanin aiki,
Irin na gida sai kin ilimi.

43. Aikin office aikin gona,
Har ma lambu a cikin ilimi.

44. Kiwon dabba har tsuntsaye,
Sai ka bi tafarkin yin ilimi.

45. Kiwon zumuwa sai an gane,
Irin yanayi a cikin ilimi.

46. Har ma fa hisabi, kimiyya,
Sanin taurari kan ilimi.

47. Fannin]ibbu har ma jinya,
Zuwa likitanci cikin ilimi.

48. Shi gattai ko ko wanzami,
Ba ya aiki sai yai ilimi.

49. Kafinta yana da irin aiki,
Da koyarwa fa cikin ilimi.

50. Bare malam mai horarwa,
Sai ya yi nitso a cikin ilimi.

51. Shi malam ba mu da tamkarshi,
Fage na basira kan ilimi.

52. Sune fa magada Manzanni,
Masu ya]a irin neman ilimi.

53. Da su ne za a fa tsananta,
A hau ga matakan al'ilimi.

54. A ya]a tafarkin addini,
A reni zukata kan ilimi.

55. A goge su tsatsar jahilci,
Gami da su cutar al'zulmi.

56. A jefa tunanin Arrabbu,
Ya ratsa zukata ba zulmi.

57. Shi tsoron Allah bai samo,
Sai an je an koyo ilimi.

58. A san Allah shi yai komai,
Kuma yai kowa a cikin ilimi.

59. Shi ne fa ma}agin taurari,
Har ma tsarin sama ba zulmi.

60. Wata, rana fitilar haske,
Su ne fa makora az'zulmi.

61. Komai na tudu ya zuwa a ruwa,
Shi mai duka ya sako alami.

62. Mutum dabba aljan tsuntsu,
Kifi na ruwa je kai ilimi.

63. Zama a wuri]aya kar fa ka yi,
|ulla fa ka waye gun ilimi.

64. Daraja nai ba ka iyakance,
A kan komai shi al'ilimi.

65. Shi ke gadinka bai rabuwa,
Shi haske ne kuma al'ilimi.

66. In ka]iba ka ga ya }aru,
Bai }arewa ga mazo ilimi.

67. Ba ka ije ilimi can a gida,
Da abinka kake yawo ilimi.

68. Ba a gani sai kai magana,
Ko kai aiki a cikin ilimi.

69. Ba a sace maka don wayau,
Yana }irjinka mazo ilimi.

70. Shi ko ilimi ba a gado,
Kuma ba a sayarwa al'ilimi.

71. Ba a fa aronsa a je taro,
Sai an gano ka maras ilimi.

72. Ai shi fa }awa ne gun mai shi,
[a ne ko bawa mai ilimi.

73. Shi ke fa raka ka zuwa }abri,
In kai aikinka da shi ilimi.

74. Abu ne mai }ima ga daraja,
Ga kyau ga haske mazo ilimi.

75. Har Adamu ma ya rinjayi
Mala'iku ma a fagen ilimi.

76. Ayar al}ur'ani ta farko ma,
Ta sauka da sa}on al'ilimi.

77. Kar kui wasa kar kui sake,
Kowa ya fa tashi bi]o ilimi.

78. Haske ne shi kan haskaka,
Allah shirye mu cikin ilimi.

79. Don alfarmar Manzon rahama,
Muhammadu]an gatan alami.

Tammat Bi Hamdillahi.

Wa}ar *Ri}on Amana* ta Raihanatu Usman

1. Ya Rabbi na ro}e ka Allah,
Ka taimake ni na bar kasala,
Zan yo nasiha ga masu daula,
Maza da mata mu bar dalala,
Mui }o}ari mu ri}e amana.

2. Na yo salati ga shugabanmu,
Manzo Muhammadu ya kira mu,
Akwai fa aiki yana gabanmu,
Ranar da Allah zai kira mu,
Manzonmu ne jigon amana.

3. Wa'lihi wa'asahabinsa,
Kaza mutane masu son sa,
Abubakar Saddi}u]insa,
Usman Umar har ma Alinsa,
Wallahi ba sa cin amana.

4. Haka nan Khadijatu da Aisharmu,
Da Hafsa Zainabu sun kira mu,
Mu kama hanya mui ta kanmu,
Mu daina zaluntar fa kanmu,
Amma fa sai mu ri}e amana.

5. Ta dukiya ce ko mu}ami,
Wajen zama ne kar mu nemi,
Yardar mutane don mu sami,
Darajoji ko ko mu}ami,
Allahu ya hana cin amana.

6. Ko ta zance an yi sirri,
Mui }o}ari mu rufe asiri,
Dukkan mutane ban da sharri,
Mu zam muna neman fa khairi,

Mui }o}arin tsare dai amana.

7. Amma idan aka kauce hanya,
Mu kar mu yarda, yo biyyaya,
Mugun hali kar mu yi biyyaya,
Yarda ta Allah za mu sanya,
Cikin zukata don amana.

8. Mu tuna fa za mu tsaya gabansa,
Sarki Gwani don ba kamarsa,
A duniya haka lahirarsa,
Mutum da Aljan Mala'ikunsa
Shi ne yace mu ri}e amana.

9. Mu bauta Allah mu tsai da sallah,
Mu zam muna azumin farilla,
Mu fidda zakka mu gyara jimla,
Mu je hajji kar mui kasala,
Sannan mu tsai da ri}on amana.

10. Al}awari ne sai mu gane,
Maza fa har mata mu gane,
Har mai gida yayye da }anne,
Surukai da kakanni mu gane,
Allahu ya hana cin amana.

11. Shugabanni masu mulki,
Su zam fa lura a kan fa aiki,
Na yau da kullum su]au mataki,
Rikon amana ku tsara aiki,
Kullum ku }arfafa dai amana.

12. Allahu shi ya aza ku mulki,
Ba ku da iko sai ku]auki,
Ri}on amana ku gyara aiki,
Kui taka tsantsan a kan fa mulki,
Don kar ku zam maciya amana.

13. Al}awari da kuke ta dauka,
Na ayyuka to kar ku shuka,
Mugun tunani kar ku shuka,
Aiki marar kyau za ku kuka,
Da kanku domin cin amana.

14. Mu ma talakkawan da namu,
Allahu ya]ora su kanmu,
Domin su zam gyara halinmu,
Amma mukan no}e wuyanmu,
Dan kar mu]au kayan amana.

15. Kun san amana wuya gare ta,
Amma idan aka gane kanta,
Tana da da]i sai a huta,
Wajen mutane har ma}ota,
Ya ‘yan uwa mu ri}e amana.

16. Kun san hukuma uwa uba ne,
Kowa tana so yay sukuni,
Domin hakan nan ta sanya tsani,
Maza da mata mu san sukuni,
Sannan mu tsai da ri}on amana.

17. Hukuma Allah ya taimake ki,
Tsarin da kinka yi kin yi aiki,
Don ko ina kin sanya burki,
Domin mutane su gyare aiki,
Har ma fa kin hana cin amana.

18. Kin ansa alkawari ga Allah,
Don haka ba kya jin kasala,
Dukkan wurare masu illa,
Kin bincika har kin yi jimla,
Gyaran mutane har mazauna.

19. Al}arya ce ko fa }auye,
Duk makarantu don su waye,
Ga asibitoci don su warke,
Kin yo rijiyoyi don ki janye,
Halin }azanta sannu inna.

20. Wannan fa wa}a bakandama ce,
Ta ha]a kowa ta kasance,
Don bata }yale masu }wace,
Da masu cin kayan matacce,
Har ma da masu cinyewar amana.

21. Sarki kake ko hakimi ne,
Police kake ko lebura ne,
Dabto kake ko malami ne,
Har ma direbobi ku gane,
Allahu, ya hana cin amana.

22. Al}ali har lauya ku gyara,
Soja da police duk ku lura,
Aikinku na matu}ar lalura,
Ku yi hattara fa saboda nera,
Don kar ku zam maciya amana.

23. Office kake ciki sai ka gyara,
Dukkan takardu sai ka tsara,
Manya }anana sai ka lura,
Domin ka wawware ka]ora,
Kar kai halin fa ina ruwana.

24. Da masu kanti har tireda,
Har ma ma'auna da masu sai da
Kaya na]aki da yanka leda,
Har masu gyara da masu walda,
Allahu ya hana cin amana.

25. Har masu sai da abinci duka,
Da ‘yan dako in kunka]auka,
Kayan mutane kar ku yanka
Ku]in da ba kai har ku shuka
Rashin mutunci da cin amana.

26. [inki kake ko ko sukola,
Shara kake kar kai salula,
Ka share nan can ya yi illa,
Kai }o}ari lamarin kasala,
Domin tsananta ri}on amana.

27. Dukkan sana’oin da za mui
Mui }o}ari mu ga mun yi komai
Da zuciya]aya kar mu nemi
Cutar da kowa don mu sami
Yarda ta Allah don amana.

28. Malam na allo na kira ka,
Almajiranka da anka ba ka,
An tattara an ba ka duka,
Uwa uba sun }aunace ka,
Don haka sai ka ri}e amana.

29. Ka san iyaye sun yi }wazo,
Sun gazgato Allah da Manzo,
Ka sanar da su Allah da Manzo,
Su zamo suna ladabi da }wazo,
Koyar da su fa ri}on amana.

30. Ka sanar da su sunna farilla,
Da mustahabbai su tsai da sallah
Tsafta fa dole su yi ta jimla,
Su yo rubutu bar kasala,
Sannan fa ne ka ri}e amana.

31. Mata ku karka]e kunnuwanku,
Ku gyara sallah kui ta kanku,
Ku kama aure ban da shakku,
Ku tsarkake kuma zuciyarku,
Allah ya sa mu ri}e amana.

32. Ta mijinmu hard a ta ‘yan uwansa,
Na nisa kusanci har na nesa,
Idan yana da uwa mu gaisa,
A waje na taimako kar mu }osa,
Mu ri}e fa al}awarin fa amana.

33. ‘Ya’yan miji kuma kar mu }i su,
Ha}}in abinci tufa mu ba su,
{annen miji kuma duk mu so su,
Yayye da }anni dukaninsu,
Kar dai mu yarda mu bar amana.

34. Yi tarbiyyar yaranki jimla,
Ki zamo fa ba kya yin kasala,
Wajen training har fa sallah,
Da koya aiki har sukola,
Koyar da su fa ri}on amana.

35. Dukkan fa aiki sai mu gane,
Tsarki na zuci ake bi]a ne,
Idan aka sa riya ya yi muni,
Komai muke yi ba sukuni,
Wajen fa Allah mu kyauta }auna.

36. Sannan idan kin sa hijabi,
Ki tsarkake niyya ki dubi,
Zance na Allah kar ki dubi,
Aiki na masu riya da aibi,
Don su fa bas a kyauta }auna.

37. A gida ki rufe jikinki,
Ki sanya riga ki]aure kanki,
Ki tsarkake suturar jikinki,
Har ma jikinki saboda ha}}in
Mijinki ki ri}e amana.

38. Ki zamo nitsatstsa wajen kalami,
Kwantar da murya ki san mu}ami,
Irin na mata masu kalami,
A hankali domin su sami,
Rahama ta Allah don amana.

39. Ku ma maza sai ku sanya lura,
Don kar ku yarda ku zam garara,
Kun]au amana don ku aura,
Kui hattara kuma ku bar gadara,
Ku ji tausayinsu saboda }auna.

40. Sutura abinci tufa ku ba su,
Sannan ku }arfafa tarbiyarsu,
Wajen zama ilimi ku basu,
A waje na kwana kar ku }i su,
Don Allah dai ku ri}e amana.

41. ‘Ya’ya fa kar ku ciwo amana,
Ta iyaye har kowa ku daina,
Hatta }asar ka ri}e amana,
Komai muke fa mu nuna }auna,
Sannan mu ri}a ri}on amana.

42. Mu so Muhammadu]an Amina.
Domin fa shi ya ri}e amana,
Ya bada mamakin amana,
Ta]ora dutsen mu gane,
Rannan ya zan suna Aminu.

43. Dukkan mutanen Makka sun zo,
Don Hajarul-asawadu sun zo,
Su]ora dutsen su yi }wazo
Domin su san daula da }wazo,
[an Abdu yay shari'ar amana.

44. Na]an ta}aita 'yan uwana,
Domin mu gane mui ta murna,
Mu zam muna ha]a kai da }auna,
Ga masu mulki ban da raina
Abin da sunka yi don amana.

45. Nai sallama zan dakata ne,
Raihana 'yar Usman ku gane,
Ta yo rubut ta }arfafa ne,
Allah ya sa mu ri}e amana.

Wa}ar *Ri}on Amana* ta Amina Muhammadu Anda

1. Bismillah zani fara,
Wa}ar da za ni rera,
Don ga ta za ni rera,
Allah ka ban basira,
Wa}ar ri}on amana.

2. Farkon yabonmu Allah,
Don ba kamar shi Allah,
Ya wahidun Ta'ala,
Ka hana ni jin kasalah,
Wa}ar ri}on amana.

3. Allah ka bani iko,
Sarkin da ke da fiko,
Hana ni da]a tarko,
Sa in haye kadarko,
Don in ri}e amana.

4. Mazanmu har da mata,
Ni ga ni zan kwatanta,
Domin mu zan fahimta,
Mu bar zaman ba}inta,
Mu rirri}e amana.

5. Mu tashi ko da yaushe,
Mu zan hawa ta taushe,
Mu rirri}e shi reshe,
Ganye idan ya bushe,
{arshenta cin amana.

6. Ku zo mu kama hanya,
Cikinta babu jinya,
Amma akwai biyayya,

Duk sai ku zo mu juya,
A kan ri}on amana.

7. Mai tambaya a hanya,
Shi ke hawa da niyya,
In yai shirin biyayya,
Shi kanshi ba ya kunya,
In ya ri}e amana.

8. Shi mai zaman jahala,
To ya shiga kitala,
Kullun zama a bola,
Aikinshi na ta illa,
Shi bai ri}on amana.

9. Wallahi duk mu koma,
Ga Jallah mui yi nadama,
Mu }ara ba da himma,
Sannan mu daina gama,
Mu rirri}e amana.

10. Ku zo mu bu]e fili,
Domin mu gyara hali,
In mun ri}a muhalli,
Shin wai ina dalili,
Da za mu bar amana.

11. Mai tattalin sarauta,
A kanka sai ta hurta,
Ganin ka za ka huta,
Ina ko za ka huta,
Sai ka ri}e amana.

12. To sai ku zo ku daina,
Cuta a kan amana,
In kun }iya ku daina,
}arshenta za ku zanna,
Da ba}in cikin amana.

13. Dangi ku zo mu farka,
Komai ruwa da iska,
Ku zo mu tada shuka,
Mu daina]aure fuska,
Mu rirri}e amana.

14. Ku zo mu zage damtse,
Mu yi]ammara mu katse,
Mu zan hawa a dutse,
Gayyarmu kar ta watse,
Mu rirri}e amana.

15. Dum masu cin amana,
Su daina cin amana,
In sun }iya su daina,
}arshen su za su zauna,
Cikin cin amana.

16. Ka zo ka]au batuna,
In ka }i ko ka zauna,
A kan ciki da }una,
{arshenka]an kunama,
Yanka ba amana.

17. Ai sau ku zo ku daure,
Aikinku sai ku jure,
Ku tsatstsare ku kare,
Yancinku sai ya]ore,
In kun ri}e amana.

18. Dum mai ri}on amana,
Aikinshi in ka tona,
Cikin shi babu }una,
To sai ku zo mu zauna,
A kan ri}on amana.

19. Allah da yai hukunci,
Shi ne ya ba mu ‘yanci,
Mu daina ci da]aci,
Mu bar ri}o da }unci,
Mu daina cin amana.

20. Taro ku zo mu nace,
Ma ayyukan da nace,
Mu yi su dan mu dace,
Kar muy sake mu kauce,
A kan ri}on amana.

21. Shi dai ri}on amana,
Ana nufin mu zauna,
Kan gaskiya ka nuna,
Halinka kar ka daina,
A kan ri}on amana.

22. Allahu shi ya yi mu,
Yai tanadi garemu,
Duk arziki ya ba mu,
Ba cutuwa gare mu,
In mun ri}e amana.

23. Allah da yai halitta,
Ya yo mu don mu bauta,
Gare shi kar mu ~ata,
Aikinmu gun fusata,
Ta ja mu cin amana.

24. Wannan fa]a ta Allah,
Mu zo saboda Allah,
Mu rirri}e fitillah,
Cikin duhun jahalah,
Mu zan ri}e amana.

25. Ku zo mu nuna]a’a,
Domin mu kai ga sa’a,
Duk wanda ke da]a’a,
Shi ba ya ida a’a,
Sai dai ri}on amana.

26. Mu rirri}e amana,
Kar mui sake mu tauna,
Mu nuna so da }auna,
Gun mai ri}on amana,
Manzonmu]an Amina.

27. Ga [aha mai biyayya,
Manzo da bai }iyayya,
Sai dai ba za su shirya,
Da wanda bai biyayya,
A kan ri}on amana.

28. Ku zo mu zauna benci,
Mui shawara ta ‘yanci,
Mu daina yin butulci,
Domin akwai hukunci,
Ran tambayar amana.

29. Ranar akwai nadama,
Wurin da ba nadama,
Mui }o}ari mu kama,
Hanyar da babu gama,
Mu daina cin amana.

30. Ku zo mu jera layi,
Mui]ammara ta koyi,
Halinsa Annabiyyi,
Mu daina ci da yayi,
Mu rirri}e amana.

31. Komai ya zo da zafi,
Gare mu ko da kaifi,
Mu bar shiga da zurfi,
Ku zo mu]au mayafi,
Mu lullu~e amana.

32. Ku zo mu]auki sirrin,
Sannan mu ~oye sirrin,
Domin mu samu hairin,
Gun wanda ke da hairin,
A kan ri}on amana.

33. Kowa ya shuka hairi,
To za ya girbi hairi,
Kowa ya shuka sharri,
Shi za ya girbi sharri,
A kan ri}on amana.

34. Dama mu je mu bu]e,
Shafinta sai mu ru]e,
Kan lokaci ya har]e,
Duk rayuwa ta cu]e,
Mu rirri}e amana.

35. Manya ku]au amana,
Kayan ku ne ku nuna,
Domin }asa ta zauna,
Da arziki da nuna
Farin cikin amana.

36. Dan kar ku ce ku raina
Laifin ri}on amana,
To sai ya ja mu zauna
Cikin wuya da }una
In ba ri}on amana.

37. Ku zo mu bu]e babi,
Domin mu gane aibi,
Mu bar zama a gurbi,
Dan kar mu sami wabi,
Mu zan ri}e amana.

38. Ku zo mu gane za~i,
Domin mu daina kulabi,
Aikinmu ya yi ta gi~i,
Mu daina sha da gui~i,
Wajen ri}on amana.

39. Da za mu je mu bu]e,
Shafinta sai mu ru]e,
Kan lokaci ya shu]e,
Kan rayuwa ta cu]e,
Da mun ri}e amana.

40. Wallahi kar mu fasa,
Ri}onta kar mu fasa,
Da gaske kar ku }osa,
A zuci kar mu kasa,
A kan ri}on amana.

41. Nai godiya ga Allah,
Kullun ina ga Allah,
Ina yabon Rasulah,
Manzo gwani na sallah,
Sarkin ri}on amana.

42. Nai sallama ta wa}a,
Allahu ban haza}a,
Kullun ka ban zala}a,
Domin in dinga wa}a,
A kan ri}on amana.

43. Dangi nice Amina,
Da nai shiri na zauna,
Na tattala na zauna,
Wa}a ta nuna }auna,
A kan ri}on amana.

44. Funtuwa can garinmu,
Modibbo unguwarmu,
Shi Anda ne ubanmu,
In za ka zo gare mu,
Ka zo a kan amana.

Wa}ar *Zamani* ta Hajiya 'Yar Shehu

1. Allah ka ba ni fasaha Jallah mai }udira,
   Allah ka taimake sha'ir wa}en zamani.

2. Allahu na fara wa}a ta da sunanka,
   Kai ne Sami'u basiru Ubangijin }udira.

3. Kai ne Sami'u Basiru Ubangijin }udira,
   Ya Almussirru mai ji Jallah har da gani.

4. Domin Muhammadu Sallalahu manzonmu,
   Don Annabawa Sahabbai har da Tijjani.

5. Kai agaji a gare mu ka kange addini,
   Kana katsa aikin magaucinmu shai]ani.

6. Don keta haddi a aure sun yawaita }warai,
   Har ma wa]ansu mutane babu imani.

7. Haka nan malamai manya ku tashi tsaye,
   Aikinku ne ku tsare ha}}i na Rabbani.

8. Don ko abin ya kamata a bayyana shi ku ji,
   In kun bari wata rana za a zub da jinni.

9. Don ko akwai keta haddin masu bin sunna,
   Ta Rasulu manzonmu mai tsira da imani.

10. Kan tituna kwararo lungu da banzaye,
    Ya kai shararai gumakai babu imani.

11. In sun ga mata na aure sai su dinga kira,
    Ke Binta, ke Hajiya har ma da fizge zani.

12. In anka sami ta kirki ba ta tankawa,

In sunka sami shararu su sa~i Rabbani.

13. Allah tsaremu da su amin ku ce jama’a,
Mata maza har da yara masu imani.

14. To malamai da sarakai ga wasi}ata,
Na dur}usa a gabanku na ba ku don ku gani.

15. In kun karanta ku]au ha}uri saboda kure,
Almajirarku nake don kar ku zarge ni.

16. Domin fa]ar Rabbi ne ku an ka ba kiwo,
Daidai muke da makafi wa]anda ba su gani.

17. Ku za ku ja ma na gora har ku kai mu gari,
Ku fitar da mu daga sharrin nan na shai]ani.

18. To shi ya sa na yi }ara gunku don ku sani,
Aikinku ne ku tsare ha}}i na Rabbani.

19. Don Allah domin Ma’aiki sai ku sanya ido,
A kan shararan da ke sa~o ga Rabbani.

20. Don ko abin ya wuce haushi da mamaki,
Manyan mutane a kan titi da kaftani.

21. Sun raina sunnar Rasulu Nabi’u Manzonmu,
Wallahi ba su cikawa ma da imani.

22. Ga karuwai ‘yan uwansu ba su }aunarsu,
Sun bi shi babban abokin nasu shai]ani.

23. Sun bi shi ya kai su gun matan da ba su fita,
Da rana sai ko dare yayin da ba a gani.

24. To maimakon ma su kauce don su ba su guri,
Don girmamawar Ta’ala har da addini.

25. To sai ka gan su suna wa sauri suna ta kira,
Wai su shararan mutanen jinnu shai]ani.

26. In ka gaya musu Allah ya haramta zina,
Har ma na mata na aure ya fi ma muni.

27. To sai su ce maka wai ai yanzu an ci gaba,
Allahu shi ne ya kawo wanga zamani.

28. To sai ku duba fa]ar babban mawa}inmu,
A inda ya ambato kalmar izaddini.

29. Ita kan ta ma duniya in babu addini,
Wallahi ba ta zama, balle fa zamani.

30. Garga]ina ga mata masu bin sunna,
Ku tsare amana ta aure har da addini.

31. Ku ri}e mazanku ku daina kula da banzaye,
Ma}iyan Rasulu abokan nan na shai]ani.
32. Su sun ~ace ba su kunya ba su jin tsoro,
Ya kai shararai magautan nan na adanani.

33. Me za su ba ku ya amfane ku nan duniya?
Har za ku cutar da kanku ku sa~i Rabbani.

34. Har ma ku cuci mazanku ku ~ata aurenku,
Kuma ran }iyama ku tashi cikin su fattani.

35. Don Allah domin Ma'aiki na yi ro}onku,
Mu daina kallon gadajen nan na zamani.

36. Mu daina kallon su kumbobi gami da kabord,
Su ne suke sa wa]ansu su bi shi shai]ani.

37. Kun dai ji }aulinsa Jallah wa Azza inda ya ce,
Ku duba }arshen izazul kwa ga bayyani.
38. Tamat bihamdullahi nan na sa aya,
Allah tsare mu da sharrin nan na zamani.

39. Sunanta mai tsara wa}a sai a ce Hajiya,
‘Yar Shehu ce la}abi Kano a birni masu zamani.

Alhamdu lillahi.

Wa}ar *Zamani* ta Shema'u Abdullahi

1. Zamani riga ne,
Ko in ce wando ne,
Sa shi ko sutura ne,
Ko ka bar shi kasance.

2. Sa'ar mutum yayinsa
Girman mutum aikinsa,
{ashin mutum shayinsa,
{wazon shi shi zai zarce.

3. Lokaci yanayi ne,
Zuwa yake ya yane,
Juyi yake ka gane,
In ya zo ya }wace.

4. Taso maza kai aiki,
Ko ka je gun]inki,
Yalla ko kai mulki,
Ko a bar ka a kwance.

5. Zamani hatsarinsa,
{uricciya matsayinsa,
Ilimi ya zam matsayinsa,
Allah ya samu mu dace.

6. Lokaci na tafiya,
Ayyuka na rakiya,
Zuciya sa niyya,
Kul ka bar ta ta kubce.

7. Dare makwancin bawa,
Lokacin hutawa,
Duhun ciki sa natsawa,

Zo ka kwanta huce.

8. Ro}i Allah Sarki,
Ya baka dukkan sau}i,
Ka mi}a sosai da jiki
Ga~a~uwa su yi kwance.

9. Rana tsawo sha aiki,
Cikinsa za ai girki,
Yininsa ne sha mulki,
Komai ka ke ka zarce.

10. Ciki ake yin wa]ari,
Sannan ake yin guzuri,
Yayin biki wan bidiri,
Da ta shigo ta ta fice.

11. Da yamma ne za a cale,
Kowa ya tsale ya }yale,
Ai walwala ai tsalle,
Mu yi su ranmu a huce.

12. Sai alfijir sa ni'ima,
Haskensa ne sa zamma,
In yai tsawo sa himma,
Ka tashi nan gaggauce.

13. Kwana bakwai sha }irga,
Mako guda ka jirga,
Komai muke ma farga,
In mun ~ace ta ku~uce.

14. Ga asabar sai lahadi,
Ga litinin ba madadi,
Sai fa talata adadi,
Cikinsu kowa ya mace.

15. Ina ta samu larba,
Ke ce ta bawan riba,
Sai alhamis ka duba,
Ka tashi domin ka fice.

16. Sai juma'a sha idi,
Mui kwalliya ga siddi,
Mu hau mu jawo gardi,
Ya ja mu ko ma dace.

17. Mako hu]u kan yi wata,
Wata da shi za a kwata,
Gudu hu]u maimaita,
Idan kai sakaci ko su wuce.

18. Wata biyu ga goma,
Ha]a ka }irga ka kuma,
Cikinsu]a kan girma,
Ya sami bakin zance.

19. Wannan muke sha da kira,
Ce wai muke shi shekara,
Mui nazari mui hattara,
In sun tu}e za mu mace.

20. Su shekaru masu yawa,
Guda-guda masu hawa,
{arni suke komawa,
Yayin su ne za su fice.

21. Ga damina ga rani,
Kaka ake yin sha'ani
Aita ka]i har da gini,
Yayin biyan duk rance.

22. Sai bazara sha iska,
[ari ake ba shakka,
Ganye }asa yaka sauka,
Sanyi a nan ya }wace.

23. Second guda }iftawa,
Shi ~al~alin ~allawa,
Shi wal}iyar wul}awa,
Tsawon ciki sa }ifce.

24. Yawansu sun kai sittin,
Ana zubinsa a sittin,
Minti ake ce tintin,
{iyasi mai jan zance.

25. Sa'a da}i}u muka ce,
Sittin awa]ai kan ce,
Komai kake gaggauce,
In ka }i ko ta kubuce.

26. Shema'u ce ta tsara,
Nufinta ne]ora tsara,
Cikin bi]ar son nasara,
Kar lokaci yak ku~uce.

27. Allah ka sa mun dace,
Kar lokacinmu ya zarce,
Shi ne takobin gafce,
Wuyar ma}i cika zance.

28. Ya malikal malakutu,
Kai ne ka yo ya}utu,
Ya wanda yai alwa}atu,
Ya yi su domin su wuce.

29. In sun wuce, sun ko wuce,
In sun tu}e, sun }wace,
Ba maimaici ba nace,
Domin ko su sun zarce.

30. Don haka kowa ya tsaya,
Yai naciya yai niyya,
Aiki da kyau ba aliya,
Yai juriya ya amince.

Wa}ar *Lullu~i Ga Mata* ta Hauwa Gwaram

1. Bismilla zan yi wa}a,
Jalla }ara min haza}a,
Ban basirar tsara wa}a,
Kar~i yai na wanga wa}a,
Lullu~i na kyau da mata.

2. Dariya da ganin tsiraici,
Gun Musulmi fasi}anci,
Kori yau da cin mutunci,
Ko }azaf ko jahilanci,
Lullu~i na kyau da mata.

3. Zan bayanin masu goyo,
Kan suna tafiya da goyo,
Sai su kwance zane su juyo,
[a ya sha mama su juya,
Lullu~i na kyau da mata.

4. {addara in ta kira ki,
Kin fito waje za a ganki,
Sai a gan ki da lullu~inki,
Dena nunin kyawun jikinki,
Lullu~i na kyau da mata.

5. In kina waje ko a]aki,
[aure kai zai kyau gare ki,
Yafa]an gyale sai]iyarki,
San mutumci gun zamanki,
Lullu~i na kyau da mata.

6. Kun ga mataye na sunna,
Ba su kwance zani su zauna,
Kishiyoyi ‘yan uwana,
Ba fa]a balle hiyana,
Lullu~i na kyau da mata.

7. Mummuna mai son ta tsira,
Ita ce ta kula da gyara,
Ba ta yin yawo tsirara,
Ba ta ro}on masu nera,
Lullu~i na kyau da mata.

8. In kina da rabo ki tuba,
Karuwa da giya da taba,
Kar su ja miki shan azaba,
Sai ki hanzarta ki tuba,
Lullu~i na kyau da mata.

9. Daina yin aure da idda,
Lalubo Kalmar shahada,
Yi }o}arin koyon ibada,
Kar ki zan mai ~oye ada,
Lullu~i na kyau ga mata.

10. Ya kamata ku zo ku tuba,
Tun macewa bai taho ba,
Nemi aure kar ki duba,
Yaudarar mai baki taba,
Lullu~i na kyau da mata.

11. Mun ga gyara ya wuyata,
Yanzu ~arna ta yawaita,
Masu gyara sun }aranta,
Gaskiya kuma ta wuyata,
Lullu~i na kyau da mata.

12. Mui ta himma kar mu ta~e,
Dan hali ke sa a ra~e,
Masu zamba ku je ku ra~e,
Gaskiya fa]inta ra~e,
Lullu~i na kyau da mata.

13 ‘Yan musulmi mui du’a’i,
Don mu samu rabo ga A’i,
Jahili ba ya du’a’i,
Mui du’a’i kan bala’i,
Lullu~i na kyau da mata.

14. Kun ga mataye na kirki,
Ko kamar waje ko a]aki,
Ba su }aunar ~ata aiki,
Tattalinsu zama a]aki,
Lullu~i na kyau da mata.

15. Za su]aura zane gare su,
Kansu har ga dugadugansu,
Babu ma ice ga kamarsu,
Ma bare ya ga kyaun jikinsu,
Lullu~i na kyau da mata.

16. Sai ku tsoraci ran hisabi,
Za a watsowar kitabi,
Masu kyau da na masu aibi,
Zuciyar da ta goya gaibi,
Lullu~i na kyau da mata.

17. Za a ce mu karanta aiki,
Da mukai a fage da]aki,
Karuwai da karanta aiki,
Lahirarku saboda mulki,
Lullu~i na kyau da mata.

18. Duk abin da ka ~ata aiki,
Za a bi shi sashi da sashi,
Ko gurin da ka ~ata taki,
Ko ga sa~o ko ga shirki,
Lullu~i na kyau da mata.

19. Na yi kuka nai nadama,
Zan bayanin garga]inmu,
Na yi kuka nai nadama,
Tausayin kai babu himma,
Lullu~i na kyau da mata.

20. ‘Yan uwa mata ku ji mu,
[an bayanin garga]inmu,
Mai rabo ce za ta ji mu,
Fan]ararra sai ta }i mu,
Lullu~i na kyau da mata.

21. Duk abin da ya zo gare mu,
Jalla gyara kwanciyarmu,
Zunuban da suke gare mu,
Sau}a}e wahala gare mu,
Lullu~i na kyau da mata.

22. Zan tsaya haka don na huta,
‘Yan uwanmu ku dinga tsafta,
Zan tufa da jiki wadata,
Lullu~in jiki ya kamata,
Lullu~i na kyau da mata.

23 Jalla yafe zunubanmu,
{addara ta sa mazanmu,
Sun ha}urci]awainiyarmu,
Sauwa}e wahala gare mu,
Lullu~i na kyau da mata.

24. Kun ga Hauwa Gwaram ta fada,
Ce take wa}a gareku,
Lullu~in mata da ada,
Kyauta al’adu ga‘ada,

Lullu~i na kyau da mata.
Alhamdu Lillahi.

Wa}ar *Kishi* ta Ru}ayyatu Sabuwa Nasir

1. Bismillahi Kabiri,
Nai yabon Allah {adiri,
Assami'u gwani Basiri,
Assataru Asshakuru,
Godiyar mu gaba]aya.

2. Kai ka cancance ta nuru,
Alimun ma fis suduru,
Ahadun fardun Gafuru,
La sharikalahu Habniru,
Mahaliccin kulliya.

3. Shi ka]ai ya halicci kowa,
Shi yake iko da kowa,
Ba uba a gare shi da uwa,
Ba }ani a gare shi ba wa,
[a da mata da]aya.

4. [an uwa a gare shi babu,
Kuma bai haifa ba Rabbu,
Ba a haifar ba wahabu,
Kishiya a gare shi babu,
Shi ka]ai yake Rabbiya.

5. Shi ka]ai yake ya buwaya,
Ba abokin tarayya,
A gare shi bare hamayya,
Har ta faru da cu]ayya,
Babu wannan gashi ya.

6. Nai salati nai salami,
Bisa manzonsa Karimi,
[aha jikan Hashimi,

Yasin babban }asimi,
Na Hadiza da Mariya.

7. Da bisa Alai da Sahabai,
Na sa jimlarsu gaba da bai,
Da ba su aikata, zunubai,
Gaisuwa dubbai da dubbai,
Nai gare su gaba]aya.

8. Bayan haka ga manufata,
A bisa kishi na yi ta,
Don abin kam ya }azanta,
Hassada kushe da }eta,
Fa]uwa ne gaskiya.

9. ‘Yan uwana kun ga kishi,
Bai da amfani a bar shi,
Shin ko kun san ma’anarshi,
Ha]ama son kai da }yashi,
Da rashin bin gaskiya.

10. Tun da Allah ne ya tsara,
Lamarin kishi mirara,
Shi ya yarda maza su tara
Jumlar mata su tara,
Adadi ya wuce]aya.

11. Kun ga dai jumla na aure,
Hu]u cif cif za su tare,
Inda ko har }warare,
{war}warori ne }warare,
Dan a gane a jiya.

12. Rabbu ya yardam musu,
Don haka mu ma mu bi su,
Sau da hannu mu bar musu,
A tsakaninmu da kuma su,
Ba fa]a ba tankiya.

13. Mu yi yarda da hukunci,
Na ilahu mahalicci,
Shi ka]ai ne maka]aici,
Ku mu bar sha'awar ka]aici,
Rabbana shi ne]aya.

14. Ku mu bar }in tarayya,
Shi ka haifad da hamayya,
Tun da Allah ne]aya,
Ba abokin tarayya,
A garai ba kishiya.

15. Mu mutane babu makawa,
Tarayyarmu da 'yan uwa,
Mu ababen haihuwa,
Ai saboda haka kuwa,
Dole ne mui tarayya.

16. To dukkan ko tarayya,
In ana son gaskiya,
Sai a nisanta }iyayya,
A cikinta a]aura niyya,
Tattalin bin gaskiya.

17. Duk a daina gaganiya,
A bi turbar lafiya,
Ai zama na halaliya,
Ba fa]a ba tankiya,
Ko sabo ma da]iya.

18. Don ko }auna ta riya,
Cikin ha]in kai da aminci,
Ba ba}in }uduri a zuci,
Wanda kan ce 'yan ubanci,
Ya fi kyau haka gaskiya.

19. Don ko }auna ta riya,
Ta shigar musu zuciya,
Don rashin gaba ga su iya,
In ko kishi yai shirya,
Zai wuya ha]a kan]iya.

20. To fa don haka ya zamanta,
Rage kishi ya wajabta,
A kasance da nagarta,
Don]iya sa yi zumunta,
Halisan ba wariya.

21. ‘Yan uwa abin da ya fi,
Kar mu]au kishi da zafi,
Kar a ha}a rami da zurfi,
Na mugunta na ga ya fi,
Kyau a zauna lafiya.

22. Ya ‘yan uwana mata,
A aje kishi a huta,
Kun ga sa kai ya fi bauta,
Wahala zakkar jiki ta,
Wohoho }ajageniya!

23. Lokaci ya yi gare mu,
Da za mu lura da kammu,
Don mu nemi abin fa kammu,
Mu bar ~ata lokacinmu,
Ai ga kishin kishiya.

24. Shi fa kishi wahala na,
Kuma kullun fargaba na,
Kuma koma baya na,
‘Yan uwa da za a gane,
‘Yar uwa ce kishiya.

25. Kishiya ba ta da illa,
Ban da }oshin wahala,
Saki kowa bauta wa Allah,
Kai a yaye mar jahala,
Don a huta shan wuya.

26. Mui wa kammu fa]a da kammu,
Du}ufarmu bi]ar mu ilmu,
Kyautatawa ga mazanmu,
Ya fa kishin kishiya.

27. Duk zukata su natsu,
Hankula don kar su motsu,
Duk a daina mutsu-mutsu,
Ai karatun ta natsu,
Ko }wafa ta ga zuciya.

28. Wahala jawur tsayayya,
Duk a yarda da gaskiya,
Bin miji ne shiriya,
Ba fa wai }in kishiya,
Ko }wafa ta ga zuciya.

29. Duk a bar su kada a ~ace,
A tuna dai kar a mance,
Duk abin da mutum ya shifce,
To yana nan fa rubuce,
Ran gamommu da gaskiya.

30. ‘Yan uwa nan zan tsaya,
Duk ku huta lafiya,
Taku]in nan mai biyayya,
Sabuwa Nasiru Ru}ayya,
Adakawa ba wuya.